

SADAUKARWA

Na miƙa wannan littafi
Gaisuwa ga ‘ya’yana:

Ruƙayya da Uthman,
Rabi’ah da Amina,
Kauthar da Muhammad

****

Ina addu’a cewar su,
tareda dukkanin sauran yara,
Za su karanta wannan littafi
su kuma yi amfani da shi
wajen kyautata tunaninsu,
domin halayensu
su haifar masu da
kyakkyawar halayya
a ɗaukacin rayuwarsu.

AMEEN

Ina yi wa mahaifana, Alhaji ***Usman*** da Hajiya ***Rakiya*** add’aur:
Allah Ya jiƙansu Ya gafarta masu. Ameen.
Dukkaninmu mun amfanu da dagewarsu
wajen yi mana tarbiya domim ɗa’armu ta dace
da kyakkyawar koyarwar addininmu, Islam.

Allah Ya yi irin wannan jin ƙai da gafara
ga dukkanin iyaye waɗanda suka dage
wajen tabbatarda ‘ya’yansu kasancewa
mutane masu ilmi da hali nagari daidai iyawarsu.
Ameen.

TUNANINKA KAMANNINKA



Alhaji Bashir Othman Tofa



Hakkin Mallaka (M) 1997:
Bashir Othman Tofa

Madaba'a:
Alphabet Publishing Limited
Ruqayya House
1 Maiduguri Road, P.O. Box 760
Kano State — Nigeria

Littafi na Farko: 1993
Littafi na Biyu: 1995 & 1997
Littafi na Karshe bugun farko: 1999
Sake bugun Littafin: 2005

Registered ISBN: 978-33390-0-1


Kamfanin Alphabet
bai yarda a buga ko a juyi wani fanni
daga wannan littafi ba tareda izni ba.
Za a iya bayar da izni nan da nan idan aka nema,
daga adireshi na sama.

Mai shirya littafin da bugun Komfuta:
(planning and typesetting by:)
Alhaji Bashir Othman Tofa

(Duk Hotuna daga MS Publisher suke.
Ina godiya ga kamfanin Microsoft na Amerika)

ABINDA KE CIKI

Babi	TA'ALIKI:	8
0	GODIYA DA BAYANAI	12
1	GABATARWA	15
2	TUNANI DA HALI	31
3	WAHALA DA WADATA.	63
4	HALI DA HALAYYA.	80
5	TUNANI DA LAFIYA	88
6	TUNANI DA MANUFA	96
7	WAHALA DA MASIFU	109
8	TUNANI DA INGANCI	147
9	TUNANI DA NAZARI	221
X	RAYUWA ABAR MISALI	250
Y	TUNANI DA HIKIMA	291



A wannan littafi, *fatahar* da ke nuni ga namiji,
ita ce kuma take wakiltar *kisirar* da ke nuni ga mace.

Misali:

Tunaninka**a**	=	Tunaninki
Kamanninka	=	Kamanninki
Kanka	=	Kanki

TA'ALIKI

Da sunan Allah Mai cikakken iko,
Mahaliccin Komai, Mai yin abindaYa so.

"TUNANINKA KAMANNINKA" yunkuri ne mai kyau, wajen kyautata dabi'un al'umma tareda dorasu bisa tafarkin da zai ba su daukaka a duniya da lahira. Marubucin ya nutsu wajen fahimtar halin dan-Adam da kuma irin cutar da ke damun zuciyarsa, sannan kuma ya bayar da maganin cututtukan. Hakika, a ganina ya gano maganin. Duk wanda ya sha maganin da Alhaji Bashir Othman Tofa ya ba wa zuciya a wannan littafi, to ya waraka. Sha yanzu magani yanzu!

Marubucin, wanda gogagge ne a fannin rayuwa, ya fito da salon rubutun da babu shi a harshen Hausa. Rubutu a janibin falsafa tsohon al'amari ne a tarihin duniya. Amma a harshenmu, yanzu muka ce: "Assalamu Alaikum".

Allah (swt) Ya kara tabbatar da abinda nake ta tsokaci da shi kullum, cewa: baiwa ta Allah (swt) ce. Yana bayar da ita inda Yake so. Don haka ko yaushe sai mu duba mu gani da idon basira cewa ta



wacce hanya za mu iya amfani da baiwar da Allah (swt) Ya ba wa kowannenmu domin ƙara kusantarSa (Allah swt), da ci gabanmu baki ɗaya, ba tareda mun raina mafitar basirar ba.

Wannan littafi mai albarka, bai sauka daga ƙa'idar shari'a ko ta ɗabi'ar rayuwa ba. Zai yi fa'ida ga duk jinsi na al'umma, musammam manyan gobe.

Ina mai jan hankalin jama'a da su karanci wannan littafi tareda aiki da shi domin samun al'umma tagari.

Allah (swt) Ya albarkaci marubucin da masu karatu baki ɗaya.

Wama taufiƙ illa billah!

Alhaji (Dr.) Yusuff Maitama Sule
Ɗan Masanin Kano

20th June, 1997

Mai girma, Dan-Masanin Kano, ya yi wannan Ta'aliƙi ne tun a littafin farko. Ina matuƙar godiya da addu'ar dukkannin alhairi a gare shi. Amin.

MUHIMMAN TUBALAN GINA RAYUWA

Wani Malami ne ya ke yiwa ɗalibansa misali. Sai ya ɗauko tukunyar gilashi ya ajiye a kan tebur, sannan ya ɗauko duwatsu kamar curin fura ya ringa sa su cikin tukunyar har sai da ta cika da su yadda ba wani dutse irinsu da zai shiga. Da ya gama, sai ya tambayi ɗaliban, "Tukunyar ta cika?" Suka ce, "I, ta cika." Malami ya ce, "Kun yi kuskure. Ba ta cika ba. Bari kuma ku gani."

Ya sunkuya ya ɗauko kwandon tsakuwa ya ringa zuba su a cikin tukunyar, har sai da ya cike guraben da ke tsakanin duwatsun. Sannan ya kalle su ya sake tambayarsu, "Yanzu fa?" Sai ɗalibai suka yi shiru. Can, sai wani ya ce, "Wataƙila." Malami ya yi murmushi ya kaɗa kansa.

Ya sake sunkuyawa, ya ɗauko kwanon rairayi, ya yi ta zuba shi cikin tukunya, har sai da ya cike duk ɗan gurbin da ya saura tsakanin tsakuwoyin. Sannan ya tambayesu. Suka ce, Basu sani ba.

Sai kuma ya ɗauko kwanon ruwa, ya yi ta zuba shi cikin tukunya, har sai da ta cika maƙil, bayan rairayi ya tsotsi abinda zai iya. Sannan da kansa ya ce wa ɗaliban, "To yanzu watakila ta cika. Kun fahimci darasin wannan misali?"

Wani haziƙin ɗalibi ya ce, "Duk ƙaracin lokacinka, in ka yi ƙoƙari zaka yi yin wasu abubuwan dabam."

Malam ya ce, "A a. Darasin shi ne, idan ba ka fara shigar da muhimman tubalan rayuwarka da farko ba, to ba zaka iya shigar da su gaba ɗaya nan gaba ba. Lallai ka yi tunaninsu, ka sansu, sannan ka jera su daidai muhimmancinsu; manyan da farko sannan ƙananan, ka kuma tunkaresu cikin hanzari da lura. Komai daidai muhimancinsa. Da da rairayin na fara da tsakuwar ba ta shiga ba, da kuma ko dutse ɗaya ba zan iya sa wa ba. Amma yanzu ga shi komai ya shiga ya sami mazauninsa.

Waɗannene naka muhimman tubalan rayuwar?
Ka sansu ka kuma tsara su daidai da muhimancinsu?
Ya za ka tsara waɗannan? Addininka, Ilminka, Iyalinka, Sana'arka, Mutumcinka, Tausayawarka da Jin-daɗinka da …….?



"Bismillahir Rahmanir Raheem"
****

"Duk abu Mai-kyau da ya riskeka
(Ya kai mutum)
Daga Allah yake;
Amma duk abu Mara-kyau
da ya riskeka
Daga gareka (zuciyarka) yake.
Kuma Mun aikoka Manzo
(Ya Muhammad!)
Domin ka fadakarda Dan-Adam;
Kuma Allah isasshe ne a shaidawa"

Sadakal-Lahul Azeem
****
Surat: Al-Nisa' (4)
Aya ta 79



Godiya da Bayanai

'Don a fahimta

Dukkannin godiya da yabo sun tabbata a gareShi, Allah (swt), wanda a cikin yardarSa da alfarmarSa na rubuta wannan littafi mai muhimmancin gaske. Tsira da amincin Allah su tabbata ga ManzonSa, shugabanmu, Muhammad (saw), wanda koyi da shi ya cancanci rayuwa mai fa'ida a duniya da kuma lahira. Allah Ya sa mu gane, ameen.

Ina matuƙar farin-cikin kammala wannan littafi, wanda mutane da yawa suka karanci na farkonsa, suka kuma yi ta ƙara min ƙarfin gwuiwar ci-gaba da rubuta shi har zuwa wannan bugun. Ina godiya ga dukkanin jama'a da abokai da kuma iyalina.

Da, na yi tunanin na kawo hujjoji daga cikin Al-Kur'ani Mai Tsarki da kuma wasu littattafai da na

karanta, a kan wasu bayanai da na yi, domin na nuna yawancinsu ba ra'ayoyina ne kaɗai ba. A a. Kusan komai na rubuta yana da hujja mai ƙarfi daga cikin littattafai masu ma'ana. Amma da na fara wannan hidima, sai na tarar a kowanne shafi akwai hujjoji masu yawa da za a iya kawowa daga Al-Kur'ani da littattafan Ilmi. Idan na ce sai na rubuta waɗannan, to yawansu ba shakka zai ƙara ƙibar littafin yadda zai shige ma'ana. A hakan ma, tuni ya shige abinda na ƙiyasta masa tun farko.

Saboda haka, abinda nake so in ja hankali a kai shi ne, idan da hali a gaba, insha'Allahu, zan kawo waɗannan hujjoji a wani littafin dabam, wanda za a iya riƙeshi shi kaɗai sai lokacin da ake son yin amfani da shi wajen gano hujjar wata magana.

Haka kuma, akwai littattafai masu yawan gaske waɗanda ƙwararru suka rubuta su cikin hikamar falsafar rayuwa. Abinda yake da wahala gameda ruwaito waɗannan a matsayin hujja shi ne, da kyar za ka sami wata magana guda wadda za ka dangantata da mutum ɗaya, ko kuma littafi ɗaya tak. Don hakane ma na rubuta Baba na 11 ('Y'), wanda ya tsamo maganganun hikima har 104 da waɗanda suka yi su, don su zama jagorar tunani. Wasu a cikinsu, ni na rubuta su.



1



"Gabatarwa"

"Komai ka shuka....."

Godiya ta tabbata ga Allah (swt), Mahaliccin Sammai da Kassai da duk abubuwan dake tsakaninsu. Shi ne Maɗaukaki Mai Iko da komai a kan komai. Shi ne Allah (swt) Wanda Ya halicci Ɗan-Adam Ya kuma ba shi ikon zaɓi a kan dukkanin Tunaninsa da Ayyukansa. Idan ka ƙulla Alhairi ka ga Alhairi. Idan ka ƙulla Sharri ka ga Sharri. Wannan ita ce shiriya da gargaɗi ga masu tunani da son gyarawa.

Wannan littafi ya biyo bayan littafi na farko ne, da na biyu, saboda na fahimci yadda jama'a da yawa suka karɓesu. "**Tunaninka Kamaninka",** a yadda na kammala shi yanzu da kuma yadda zan yi ta gyara

shi a kan cancanta nan gaba, ba shakka littafi ne wanda yake ƙunshe da sigogin Rayuwa fanni-fanni. Littafin farko taƙaitacce ne ƙwarai da gaske wajen duba wannan al'amari, kodayake ya nutsa sosai wajen kafa harshashin littattafai na gaba, a bayanan dangantakar **Tunani** da **Hali** da kuma **Halayyar** Dan-Adam.

Wannan littafi na uku kuma na ƙarshe, ba shakka, yana bukatar a karance shi a hankali tareda zurfaffan nazari. Komai aka yi matuƙar Tunani kuma cikin haƙuri a kansa, ba shakka za a sami biyan bukata a sannu. Daga Babi na 2 zuwa na 6, babu wasu muhimman bambancin ma'ana masu yawa da yadda suke a Littafi na farko, illa ƙarin bayanai don inganta ma'anar. Amma Babi na 7 da na 8 sun kawo sababbin (ko kuma na ce, sun sake gabatarda) hanyoyin duba halayyar rayuwar mutum a zahiri. Babuna na 9 da na 10 (x) kuwa, manyan darusa ne idan aka yi ƙwararren tunani a kansu. Shi kuma Babi na 11 (y), hikimomin magana ne masu zurfi don sosa ƙwaƙwalwa. A wannan littafi akwai bayanai da yawa waɗanda za a iya jinginasu hujjarsu da Alƙur'ani Mai girma da ingantattun Hadisai, amma ban alamtasu ba. Toh, a nan ma, ba za su alamtu cikin hanzari ba, kamar yadda na yi bayani a can shafin baya. Amma na



san da sun karanci irin waɗannan bayanai, masu ilmi take za su dangantasu da hujjijinsu na ƙwarai.

Toh, bari dai na koma baya na tunaso mana da Gabatarwar Littafi na Farko. A can ne na rubuta cewar, rayuwa takan kasance kusan a kowanne lokaci tamkar yadda tunanin mutum yake. “Kamar Kumbo kamar kayanta”. Tuni mun gamsu da sanin cewar Allah (swt) Shi ya ke tsara komai, Ya kuma tafiyarda komai. Amma kuma mun san cewar Ya ba wa Ɗan-Adam ’yanci da damar kimtsa rayuwarsa, ko kuma watsata da kansa. Ko a addinance mun san babbar matattakalar shiriya ita ce: *“alhairi ne yake haifar da alhairi”*; haka kuma, *“sharri ne yake haifar da sharri”.* Sannan kuma, akan ce, ‘Allah Ya ce, *“Tashi Na Taimakeka”*, domin a nuna da ma can an san Ɗan-Adam shi ne riƙe da linzamin makomarsa, sai dai wanda hanlakinsa ya gushe. Watau, kai ne mai fafutuka; kuma kai ne jagorar kanka. Sai ka yunƙura a wajen waɗannan tukuna, sannan za ka sami taimako, ko da kuwa a gun Allah (swt) ne.

Idan ɗalibi bai yi karatu ba, ba zai ci jarrabawa ba; idan mara lafiya bai sha magani ba, ba zai warke yadda yake so ba; idan ba a shuka ba, ba za a girba ba; idan ba ka tafi ba, ba za ka je ba; idan ka sa hannunka a wuta, ka ƙone; idan ka dartsawa kanka

wuƙa, ka yanke. Idan ka yi tunanin banza, ka aikata banza, ka kuma sami sakamakon banza.

Saboda haka, Ɗan-Adam yana da zaɓi; kuma iko a kan zaɓin, baiwa ce daga Allah (swt), domin waɗannan su ne bambancinsa da dabba. Ita dai dabba ba ta da zaɓi yadda muka san shi, illa ta "ji" a jikinta, kuma ta aikata abinda jikin nata ya umarta, ko ya bukata. Idan tana jin ƙishirwa, kuma ta ga ruwa, sai ta sha. Idan ba ta gan shi ba ta nuna alamu waɗanda jikin yake roƙon ƙwaƙwalwarta don ta nuna. Idan ta ji zafi, ko ta ji tsoro, ta arce. Iyakacin irin nata hankalin da zaɓin kenan.

Son zuciya, ƙera ƙarya, ha'inci, gulma, zamba, baƙin-ciki, hassada da munafurci, duk mun san suna daga ɓangaren *Baƙar Aniya* ta ɗan-Adam. Amma kuma ɗan-Adam, zai iya zaɓar ya zama mai gaskiya, riƙon amana, tausayawa, taimakawa, mutumci, kawaici, ɗa'a, son-jamaa, ƙoƙari da tsoron Allah. Duk waɗannan da sauransu suna daga ɓangaren *Farar Aniya* ta ɗan-Adam. Da baƙaƙen aniyar da fararen aniyar duka abubuwan zaɓi ne ga ɗan-Adam. Ba ruwan Allah a cikinsu, in dai hankalinka cur yana jikinka. *In Hairi, hairi za ka gani; In Sharri, sharri za ka gani. Watau, duk abinda ka shuka shi za ka girba.* Ya rage naka.



Amma akwai halaye da mutum yake shiga cikin wata matsala, ko al'umma ta shiga cikin wata masifa; dukkaninsu suna zargin wani ne ya jawo masu waɗannan ba su ba. Akwai kuma wasu halayen da mutane suke ciki na matsuwa, amma sun saduda, ko 'wai' sun karɓi ƙaddara cewar haka suke ba yadda za su yi. Waɗannan halaye suna bukatar nazari cikakke, amma daidai hankali a wannan littafi.

Da farko lallai ne na ja hankulanmu cewar ba manufar wannan littafi ce ta ƙyami marasa galihu waɗanda suke cikin matuƙar tsanancin rayuwa saboda yadda al'amura suka ɗauro ba. Babbar manufar ita ce ta taimaka mana duka wajen farkawa, domin mu sake bincika kanmu ta yadda za mu iya nema, kuma mu sami "wadatar zuci" da "gamsuwar" da suka dace da mu.

La'akari cewar wasu wahalun, ƙalubalanta ne na rayuwa, yakan tsikari mutum ya tashi tsaye wajen gyara matsayinsa ta hanyar tunkarar wahalunsa. Watau, ita kanta rayuwa ba za ta yi ma'ana ba, in komai da kowa daidai suke tafiya. Idan da haka rayuwa take da tuni an gaji da ita, domin ba ta ba da damar a sarrafa tunani don tunkararta gaba da gaba ba. Da tuni ta watse ita kanta.

Haƙiƙa, Allah (swt) Bai halicci kowa da kowa daidai ba sabo hikimarSa. Idan muka yi tunani za mu ga ma'anar wannan hikima taSa; kuma akwai gurare a wannan littafi da suka taɓo wannan fanni. A ƙasashe dabam dabam, Ya ajiye al'umma dabam dabam cikin halaye iri iri na jin daɗi da na wahala. Amma idan muka lura, akan sami masu arziki sosai a guraren da talauci ya yi kanta; a kuma sami matalauta a guraren da kuɗi da arziki suka yi yalwa.

Wannan hikima ce wadda yakamata ta nunawa ɗan -Adam cewar yana da damar da zai wataya a tsakanin waɗannan halaye biyu. Idan tunaninsa da burinsa kimtsattsu ne a kan abinda yake nema, to akwai damar samun biyan bukata. Idan kishiyar haka ne mashimfiɗar tunaninsa, to sam sam, ba inda za shi. Masu la'akari tuni sun san haka.

Allah (swt) Bai ware wata al'umma, ko ƙabila, ko wasu mutane dabam a wata zuri'a ko a wani gida, Ya ce su kaɗai za su arzurta ko su talauta ba. Amma Ya nuna matattakalun hawa ga arziki, da wadatar zuci; Ya kuma nuna na gangarowa daga garesu. Mun ga ɗan sarki talaka; ɗan mai kuɗi matsiyaci. Mun ga ɗan malami ya zama jahili; amma kuma ɗan jahili ya zama malami; kamar



yadda ɗan talaka ya zama shugaban Kasa. Muna da labaran inda rimi ya juye da mujiya: mai gaisarwa ya zama mai karɓarta; mai doki ya koma kuturi; sarki ya zama talaka; direba ya zama uban-gidan mai gidansa. Mun ga mutanen da suka fito daga ƙungurman ƙauyuka, suka zama manyan masu kuɗi ko shugabanni a manyan birane; mun ga kuma kishiyar haka. Ga ɗan makaho da idannunsa; ɗan kuturu da yatsunsa. Amma kuma ga ɗan sarki yana roƙo, ko ɗan alkali ya yo sata. Ga dai misalai nan birjik. Ba shakka wasunmu sun san Allah (swt) Ya ce, *'Shi ne yake fidda mai rai daga matattace; mattace kuma daga mai rai; sannan ya arzurta wanda Yake so ba tareda awo ba'.*

Darussa irin waɗannan sune manufar wannan littafi. Watau, kada don kai talaka ne, ko wani mara galihun rayuwa, ka yarda ka watsarda rayuwarka cikin nadama. Daga matacciyar halayya, Allah Zai iya rayar maka da ingantattar halayya, muddin dai ka yi abubuwan da ake bukata don cimma wannan sabuwar rayuwar. A Gyara tunani don inganta matsayi; a nemi sana'a don inganta rayuwa; a ɗau ɗabi'u masu kyau don neman nasara. Waɗannan sune yakamata su zama ɗabi'arka domin ka zamto mutum mai manufa, mai kuma fafutuka a kan manufar taka, ko menene matsayinka. Kai ne kafi

kowa sanin kanka da abinda zai gamsarda kai. Wa ya san inda rabo yake? Haka, kada don kana zaton kana da komai, shikenan sai ka watsar da tunani mai kyau, ka ƙi adana zuciyarka, ka ƙi shirya rayuwarka. Wa ya san inda hasara take?

Idan muka yi tunani, yawancinmu mun san: da rabo (ko *nasara*) da rashi (ko *hasara)*, ba shakka, suna ga masu nemansu ta hanyar *tunaninsu*, wanda zai gina *halinsu* ya haifarda *halayyarsu*. Ba abinda ya fi damun mutanenmu irin kasalar zuci, rashin taɓusawa, wasu lokatai don son banza, wasu kuma don rashin sanin ya za a yi. Wani, haka kawai, sai ya watsar da darajar da Allah (swt) Ya yi masa, ƙememe ya ƙi gudanarda rayuwarsa kamar mutum. Haka kawai, sai mutum ya sadudarda kansa, ƙememe ya ƙi neman sana'ar yi don ya inganta mutumcinsa.

Dá samari abokai masu ƙarfin jikinsu za su haɗa kansu su yi tunanin sana'ar da za su fara, ko da ta dako ce (maimakon su zama 'yan banga, ko 'yan daba, ko 'yan ƙwaya), dá wataran sai sun sayi 'a-kori kura', Dá wataran sai mu gansu da manyan motocin sufuri. Amma, Ina!, Yawancinmu ba mu da wannan zuciyar. Dá masu sana'a iri guda, za su daure su haɗa kawunansu da jarinsu don inganta



wannan sana'ar, dá lallai wataran sun gina manyan masana'antu. Amma Ina! Hassada da zamba ba za su ƙyale yawancinmu yin haka ba. Dá samarinmu da yayyensu za su koyi sana'un yau da kullum, dá sun yi mamakin yadda za su gamsu da kansu. Dá za mu maida hankulanmu wajen gaskiya a harkokinmu, da kishin kanmu, dá ba haka ba.

Kasashen da suka ci gaba; da al'ummun da suka ci gaba, ba haka siddan suka ci gaban ba. Tunanin manufa da fafutuka a kanta, cikin la'akari da muhimmancin ɗa'a da aikata gaskiya da kare mutumcin mutum; tausayin na baya da taimakonsa; ba gaba ko gasa da shi ba; girmama na gaba da koyi da shi in ya cancanta; yabon mai gaskiya da halaye nagari, ba girmama ɓarayinsu ba; su ne suka haifar masu da ci gabansu. Ci gaba kuwa, magana ce ta tunani ba ta tsabar kuɗi da manyan gine-gine ko motoci ba. Magana ce ta shugabanci nagari, ba satar kuɗin jama'a ba. Magana ce ta ƙyamar marasa kunya, ba yabonsu ba. Mu ma akwai waɗanda suka zama masu kuɗi sosai a al'umarmu; akwai masu ilmi iri-iri a cikinmu. Amma, 'ci-gaba' wani abune dabam wanda yake shafar al'umma gaba ɗayanta, ba 'yan tsiraru ba. A haƙiƙa, na san ba inda za mu a matsayin al'umma mai ci-gaba, sai mun gyara halayenmu. Sai mun tashi mun yi da

gaske. Sai jama'a sun san mutumcin kansu, sun san haƙƙunansu, kuma sun shiryu su bi waɗannan haƙƙuna, su kuma ba wa al'umma nata haƙƙin. A taƙaice, sai sun dawo da Allah (swt) a tunaninsu da ayyukansu.

Ta hanyar gyara tunani da gaskiya ce kaɗai za mu iya sa kanmu a al-ƙiblar ci-gaba. Ta hanyar ƙwaƙƙwarar manufa ce kaɗai za mu iya kama hanya. Ta hanyar fafutuka ce kaɗai za mu iya danganawa.

Wannan littafi ya kutsa cikin dangantakar "Tunani" da wasu al'amura na rayuwa, da bayanai waɗanda za su iya taimakawa masu buɗaɗɗar zuciya. Amma akwai bayanai waɗanda wasu mutane za su iya damuwa a kansu, wataƙila saboda yadda na faɗesu. Ina tabbatarwa masu karatu cewar ban rubuta wata kalma da mummunar niyya ba. Mummunar niyya ko kaɗan ba za ta dace da manufar wannan littafi ba. Ba shakka, akwai hanyoyi da yawa na bayanin abu guda, amma kowa da irin basirarsa da azancinsa. Ni ajizi ne, sai a gafarceni a gurare irin waɗannan.

Masu karatun wannan littafi, musammam ma in sun iso Babi na 7, suna bukatar su yi cikakken tunani. A cikin waɗannan fannoni na yi magana a kan sharrin da mutum yake jawowa kansa wajen



ɗorawa Allah (swt) laifin masifu ko wahalun da suke samun Ɗan-Adam a wannan rayuwa. Wasu da farko za su ga tamkar na kama tafarkin wata gurɓatacciyar magana ce. Wasu kuma su ce ai na saki hanya ma gaba ɗayanta, saboda yadda na hango abubuwa da yadda na fassarawa kaina su. Ba shakka, ra'ayoyina a kan wannan matsala za su iya ɗaure kai, in ba a yi zurfaffan tunani da haƙuri ba. Fitarda ma'ana gameda yadda Allah (swt) Yake sha'aninSa ba ƙaramin aikin kasada bane ga mutum. Amma kada wannan gaba-gaɗi nawa ya rufe idanuwanmu da zuciyoyinmu daga ainihin gaskiyar abubuwan da za su iya gyara tunaninmu su inganta rayuwarmu. A yawancin lokatai, Hausawa sukan yi mana matashiya cewar: *'Gaskiya ɗaci gareta'*, kuma ba shakka hakane. Muhimmin abune mu kasance masu kyakkyawan tunani gameda Allah (swt) a kowanne hali da muka sami kanmu a ciki.

Idan mutum ya bar zuciyarsa a buɗe, ya kuma zama mai shirin yin tunani fisabilillahi a kan abinda ya *'ji'* ko ya *'gani'*, to ba shakka wannan mutum shi ne maciyin ribar al'amura. Amma mutumin da nan-da-nan ya ɗau matsayi ba tareda zurfin tunani da auna matsaloli ba, shi ne mai hasarar al'amura. Don haka nakan ce: *"saurin zargi*

yanayi ne na bakin tunani". Ba manufata ba ce na kange kaina daga wadanda za su iya yin kuskure a wannan sashin ilmi. Idan akwai kura-kurai wadanda aka lura da su, ni zan fi kowa farin ciki idan aka sanarda ni domin na gyarasu. Fatana, dinbun mutane wadanda ilminsu da azancinsu ya nike nawa ya shanye, za su karanta wannan littafi. Ina neman alfalmar irin wadannan shugabanni da su yi hakuri da ni, su kuma shiriyarda ni nan da nan. Wannan ita ce tasu gudun mowar, wadda za ta amfane ni da kuma jama'a masu yawan gaske.

Rokona shi ne, kada a yi saurin hukumta ni ba tareda duba al'amarin gaba da dayansa ba. In haka ta faru, ni ban ci riba ba, sauran jama'a kuma ba su ci ba. Kamar dai kai ne za a gurfanar a gaban alkali, amma sai ka ji alkalin mutum ne mai gaggawar yanke hukumci a kan abinda ya ji daga gefe daya na karar. Ba shakka, hankalinka ba zai kwanta da shi ba, domin ka san zai iya yanke hukumci cikin zalunci. Ko da a alakar mutum da mutum, ko mutum da hukuma, saurin yanke hukumci a kan jita-jita, ko zato, ba tareda cikakken bincike ba, yakan watsa dangantaka, ko ma ya haifarda zalunci. Haka za mu gani idan muka nazarci halayen wasu, ko da a matsala ce ta rayuwarsu. Kuma dai an ce, *"Mahakurci Mawadaci".*



A Babi na 8, na yi ƙoƙarin bayar da shawarwari a kan hikimar kimtsa rayuwa domin a sami nasara wajen ingantata. Yawancin abubuwan da na yi ta rubutawa sun cancanci a yi ƙoƙari matuƙa a mayarda su ɗabi'u na yau da kullum, kuma saboda Allah. Ba shakka, na san ba dadin furtawa kaɗai garesu ba, hakama gaskiyarsu take kasancewa a rayuwar wanda suka zama jagorarsa.

Waɗansu abubuwa suna da wuyar misaltuwa, musammam ma ga mutanen da suke ganin sun gwada sun gwada amma har yanzu ba su ga nasara a rayuwarsu yadda suke so ba. Nasara, ba shakka, tana da ma'aunai iri iri ga mutane dabam dabam. Akwai masu son kimtsa rayuwarsu da yin gaskiya, aunata da nunata da sanin yakamata, ba don su sami kudi ko muƙami ba. A'a, sai dai don sun yarda yin hakan shi ne daidai a gunsu da kuma Mahaliccinsu. Daga irin wannan kimtsi na rayuwa, irin waɗannan mutunen kirki suke samun yalwar gamsuwarsu. Amma, akwai kuma masu son watsa rayuwarsu daga kishiyoyin haka, saboda baƙin tunaninsu, da kuma zaton cewar babu wani abu a rayuwa wanda yake da muhimmanci; ko kuma dai haka suke son yi saboda rashin nasarorinsu a wasu lokatai na rayuwarsu. Ba mai hasara irin wanda ya ɗau kudi su ne kaɗai ma'aunin nasara.

Duniyar kowa dabam take. Wasu su fassarata daidai, wasu kuma su kuskure a fassararsu, su rayu su mutu cikin hasara. Amma lallai wanda bai ɗauketa da muhimmanci ba, ya tuna cewar, ko ya mutu, sunansa yana nan; watakila kuma 'ya'yansa da jikokinsa suna nan. Ko ba ka bar ƙwandala ba saboda talauci, to ka yi ƙoƙarin barin milyoyi na mutunci da kyakkyawan suna. Yin haka ma, ya fi barin milyoyin kuɗin da basu amfaneka ba, balle su amfani wani. Ko kuma kuɗin da za su jawowa na baya rigima da tozartawa, kamar yadda aka fi samu a wannan zamani namu. Ko kuma kuɗin da suka jawo ɓatawa tsakanin mai su da Allah (swt); kuma daga ƙarshe su zama sanadin ƙarkewarsa a Jahannama. Wannan ya yi hasara duniya da lahira. Amma mutum ya rayu cikin gamsuwa, ya fi komai daɗi. Sai dai, da gamsuwar da rashinta yawanci tasawira ce ta tunanin da mutum ya saƙawa zuciyarsa. Da arziki da kuɗi; da gamsuwa da jin daɗi, duk ma'aunansu dabam suke ga kowa.


Wasu suna sha'awar matsayin wasu, amma ba su san jidalin wannan matsayin ba. Wasu na ƙyamar halayyar wasu, amma ba su san jin daɗin wannan halayyar ba. Yawanci, abinda kake gani, ko zato, ba haka suke a ainihinsu ba. Amma kuma wannan magana ce muhimmiya a Babi na 9.



Komai na duniya mai sauƙi ne, sai in ka maida shi mai wahala. Amma duk yadda ka ɗauketa haka za ka tararda ita. Wasu al'amuran rayuwa a fayyace suke, ba a ɓoye ba. Wasu kuma a ɓoye suke ba a fayyace ba. Mu ne dai a irin tunaninmu, muke ta shagalarda zuciyarmu ta shiga yin fankama a badalar waɗannan, ko ma a cikin duhu. Amma kuma an ce: *"Wanda bai ji bari ba, ya ji woho".* Ko kuma, *"Kukan Kurciya ma jawabi ne, sai mai hankali ke ganewa".*

Ɗaukacin wannan littafi a kan *"Ilmin Tunani"* ko kuma a janibin *"Falsafar Tunani"* na rubuta shi. Watau, falsafa ne a kan yadda tsarin rayuwa ya jingina da tunanin mutum, ko al'umma, da ayyukansu da sakamakonsu. Akwai Kurciyoyi da yawa a cikinsa suna ta kuka. Allah (swt) Ya sa mu gane, mu kuma yi aiki da abubuwan da muka fahimta. Idan mutum ɗaya ya amfanu daga wannan littafi, ni na ci riba mai yawan gaske. Idan mutane goma suka ƙaru da shi, to ba shakka, aikina ya cimma babbar nasara.

Alhamdu Lillahi Rabbil Alameen. Ina matuƙar godiya da addu'a ga duk waɗanda suka sami damar karanta wannan littafi. Ballantana kuma a ce sun fara aiki da wasu darusansa. Ace…!



2



"Tunani da Hali"

Gaskiyar maganar ita ce:
"Mu ne jagorar Rayuwarmu"

Tunanin da mutum ya zaba, ya kuma aikata shi da sanin cewar, *'zuciya ita ce masakar labulen hali na badini, kuma mahaifar rayuwa ta zahiri'*, shi ne kadai zai shiriyarda mutum izuwa matsayi ma'inganci, ko kuma ya jefa shi izuwa matsayi maraunanci. Wanda ya san matsayin tunani haka, ya kuma yi aiki da hakan, to zai iya canja matsayinsa ba tareda wahala ba. Sakar da ya yi a zuciyarsa cikin jahilci a da, yanzu zai iya nutsuwa

ya warwareta ko ya ƙarfafata daidai da sakamakon da ta haifar a halayyarsa. Sanin cewar tunaninka shi ne yake gina halayenka, ba ƙaramin ilmi bane. Amma kuma babban ilmi sai mai babban tunani.

Abubuwan da suke tsakanin Ilmi da Jahilci suna da yawan gaske, amma dukkanninsu sun yi tarayya ne a cikin ɗawainiyar bincike da tunani a kansa fisabilillahi. Ta waɗannan sabon ilmi da tunani ne kaɗai, mutum zai iya canja matsayinsa daga ƙuntata izuwa matsayi na yalwata. Kin yin haka kuma ya haddasa lalacewa daga yalwata izuwa ƙuntata; ko kuma daskarewa a ƙuntatar.

Hausawa sukan ce,' *Hali zanen Dutse',* to amma fa ga rago, wanda bai ilmanta da cewar shi da kansa zai iya canjawa ba. Halin mutum yakan zama zanen dutse, ƙi kankaruwa, muddin bai shirya ya kankare shi ba. Babu wani abu a tunanin mutum wanda mutum da kansa ba zai iya canjawa ba. Idan kai mutumin banza ne, za ka iya sake tunani ka gyara halayenka na banza. Idan kai mutumin kirki ne, za ka iya sake tunani ka ɓata ko ka inganta halayenka na kirki. Idan kai malalaci ne, za ka iya canjawa ka zama mai ƙwazo. *"Hali zanen dutse"*, yabo ne, ko kuma la'anta ce, ga masu hali in sun aikata abubuwanda aka sansu da su.



Idan Jarumi ya yi jarumta; idan Mai kyauta ya yi kyauta; idan Ɗan-giya ya yi maye; idan Maroƙi ya yi roƙo; idan Macuci ya yi cuta; idan Marowaci ya yi rowa, ko kuma Sarki ya yi alfarma, to duk waɗannan halaye haka ake zatonsu daga masu su, saboda sanin tarihin halayensu.

Amma, ba abinda zai hana mutum shan giya; ko maroƙi roƙo, ko mara-kunya batsa, irin canjawar tunaninsu daga ƙoƙarinsu na fahimtar cewar su ne suke riƙe da ragamar rayuwarsu; kuma za su iya yiwa kansu sabuwar jagora a tafarki wanda zai iya canja Halinsu da Halayyarsu. Abubuwanda suka taru suka shawarta masu, ko kuma suka tilasta masu yin sabon tunani, wata magana ce dabam. Za mu iya yin misali da la'antar jama'a, shugabanci na -gari, dokokin Kasa, faɗan iyaye, shawarar abokan kirki, ko tsangwamarsu, ko ma masifar duniya ita kanta, duk a matsayin dalilai masu ƙarfi.

Mun san cewar ba daidai bane mu fassara mutum ta hanyar silin tunani guda ɗaya tak, ko kuma daga wani abu mai kyau ko mai muni guda ɗaya da muka *ga*, ko muka *ji*, ya yi ba. Misali: Don mun ji wane ya yi ashar, bai kamata mu yanke hukumci cewar shi asharari ne nan-da-nan ba. Don kawai mun ji wasu na rigima, bai kamata mu ce su kashe

kansu, don su 'yan rigima ne ba. Haka, don kawai mun ga mutum ya miƙa sadaƙa, bai kamata mu yanke cewar ga mai tausayi ko tsoron Allah can ba. Ainihin kamannin mutum alama ce ta kulliyar tunaninsa, kamar yadda *tsiro* yake kulliyar *irin* da aka shuka. Don hakane ayyukan mutum na zahiri suka zama irin halayen da ya shuka cikin tunaninsa. Munafuki kuwa, ranarsa takan ɓaci.

Ba shakka, a wannan lokacin da muka ji wane ya zabga ashar, ya kasance mai furta ashsha. Haka a wannan lokacin da muka ga wane ya miƙa sadaƙa, ya kasance mutumin kirki. Amma ga manazarcin ɗabi'u don auna halayen jama'a, dalilan ashar ɗin da kuma na ita sadakar, abubuwa ne da suke bukatar cikakken bincike, musammam ma idan mutanen da suka aikata waɗannan abubuwa ba a sansu da waɗannan halayen ba. Amma idan da ma mun san su da waɗannan aƙidoji, to sai mu ce, '*Hali zanen dutse';* mu la'anci mai ashar, mu yabi mai sadakar.

Ɗa'a, nagarta, kishin addini da na jama'a, ba abubuwa ne da suke samuwa haka kawai ba. Waɗannan kyawawan halaye *girbi* ne na daɗaɗɗar fafutukar tunani a kan hanya mai tsari da gaskiya. Haka rashin mutumci da rashin kunya da sharri da



hassada, *tsiranni* ne na munanan tunani cikin rayuwa mara fa'ida, mara tushe.

Rayuwar mafi yawancinmu, ba shakka, ta kan ginu ne a kan harshashin da iyayenmu, yayyenmu, abokanmu ko al'ummarmu da shugabanninmu suka gina mana. Amma a ƙarshe, mutum shi da kansa yake gina kansa, ko kuma ya rusa kansa da kansa, muddin mai hankali ne shi. A cikin kwanyar tunani yake shirya kayan yaƙin da zai cuci kansa ya turnuƙawa rayuwarsa masifa; ko kuma ya amfani kansa ta wajen samarwa kansa Aljarnar jin daɗi, farin-ciki da kwanciyar rai, ta hanyar canja, ko mulmula tunaninsa a kan tafarkin alhairi. Idan ya zaɓi nagari, ya kuma aikata shi daidai da kuma hikima, sai ya cimma *Farin Buri.* Idan ya yi zaɓi na banza ya kuma aikata shi to, sai ya cimma *Bakin Buri*, har sai ya zama tamkar dabba.

A tsakanin waɗannan zaɓi biyu ne mutum yake samun kansa; ya ceci kansa, ko ya cuci kansa, domin shi ne kuma mai iko da zaɓin. A taƙaice dai, mutum yana da ɗimbun iko a kan mulmula *hali* da makomar rayuwarsa, watau *halayyarsa*. Ɗauki abinda Allah (swt) da ManzonSa suka ce gameda Zuciya. Idan ta gyaru komai ya gyaru; idan ta ɓaci komai ya ɓaci. Mutum, shi yake da iko a kan ƙulle-

ƙullen zuciyarsa da abinda za ta raya masa, ko ta nemi sa shi ya aikata. Idan ya ga dama ya bi son zuciyarsa; in ya ga dama ya bi son hankalinsa, watau, kyakkyawan tunaninsa. Haka waɗannan zaɓi suke a kowanne juyi na rayuwa. Mun kuma san baƙar makomar masu bin son zuciyarsu.

Tunda kuwa mutum yana da wannan iko, sannan ga ilmi da hikima da Allah Ya ba shi, ko Ya bayar a inda zai iya tambaya, toh kuwa ashe ba shakka, mutum shi yake riƙe da maƙullin kowacce ƙofa ta kowanne hali. Haka kuma yana da ikon da zai fara ƙoƙarin canja kansa da abinda yake so, har sai ya cimma nasara. Da zarar mutum ya fara tunanin halin rayuwarsa, kuma ya laluba dalilin samuwarsa sosai, to kuwa zai iya gyara turbar tunaninsa cikin kimtsuwa da hikima ta yadda zai ci moriyarta cikin ni'ima. Wannan shi ne mutum mai la'akari wanda a kodayaushe yake fafufukar gyara kansa ta hanyar gyara tunaninsa. Tunanin *"Ba yadda zan yi"* ya fi kowanne irin tunani baƙanta, domin ta hanyarsa mutum yake sa kansa cikin ƙangin da ba ficewa. Kullum, ka cewa kanka '*Da yadda zan yi'*, shi ne kaɗai tunani da zai iya fidda kai daga ƙuncin da ka sami kanka ciki. Da wannan farin tunani za ka wasa ƙwaƙwalwarka ka fiddo da dabaru iri iri na ceton kanka da kanka.



Cin ribar rayuwa takan samu ne idan mutum ya ci gaba da rairaye halinsa tareda sanin cewar komai ya dogara ne a kan yadda ya gudanarda al'amuransa. Ta irin wannan hanya, kowanne mutum zai iya bincika kansa, ya shiga cikin ruhinsa, ya mulmula halinsa, sannan ya shimfiɗa tafarkin rayuwarsa da makomarsa. Sai da irin wannan fafutuka tsakaninka da kanka, kuma domin kanka, sannan za ka iya ceton kanka daga ƙangin rayuwar da ba ta dace da kai ba. Hausawa, sukan ce: *"Mai nema na tareda samu"*. To ka nemi kanka ka sami kanka tukuna; sannan ka binciki abinda kake neman. Lallai ne ka fara auna bukatunka da matsayinka da damarka tukuna, kafin ka nema. Ta hakane kaɗai za ka san ko abin ya dace da kai ko bai dace da kai ba. Idan ka cimma wannan matsayi, to, sai ka ƙwanƙwasa, ba sau ɗaya ba, ba sau biyu ba. Da haƙuri da juriya, tareda imanin za ka samu, za a buɗe maka ƙofa da taimakon Allah.

A nan, yakamata ka san cewar, ba lallai ne a buɗe maka ƙofar da ka ƙwanƙwasa ba, ko kuma a ɓudeta gaba ɗaya yadda kake so ba. Amma ba shakka, a sannu da sannu, ƙofa za ta buɗu. Kamar mai addu'a ne ga Allah (swt) da bukatar wani alhairi, lallai ya san alhairin ba zai samu ba, sai ya yi imani da mahimmancin addu'arsa da kuma

fafutukarsa a kan abin. Kuma ba lallai ne ya sami daidai, ko yadda ya nema, ko yake zaton abin ya dace da shi ba. Amma, ko ta wane hali, cikin haƙuri da ci gaba da addu'arsa da fafutukarsa, Allah Mai amsa masa burinsa ne, kuma alhairin zai riske shi, ko da ta hanyoyin da bai zata ba ne. Yawancin jama'a tuni sun san haka. Amma idan ba ka tace tunaninka ba, ba ka roƙi ko nemi abinda ya dace da kai ba, kuma ba ka yi fafutukar da ta dace da abin ba, to ba za ka sami biyan bukata ba, ko da kuwa ka sami abin. Kana ji kana gani abin zai zame maka bala'i ya jawo maka masifun da ba ka zata ba, waɗanda kuma ba za ka iya jurewa ba.

A nan za mu ga ashe ma akwai dangantaka tsakanin tunani, addu'a da fafutuka. Idan tunaninka gurɓatacce ne a kan amfanin addu'a; watau, sam ba ka yi imani da mahimmancinta ba, ba yadda za a yi ka yi fafutukar da ake bukata don ƙofar ta buɗu a gareka. Rashin tsabtar zuciyarka da gajen imaninta da raunin haƙurinta, sai su ringa ingizaka tafarkin da babu alhairin. Samun kanka kafin ka sami wani abu ya zama maƙasudi a cikin tsarin gyaran halayyarka. Karkon imani ya dogara ne a kan sanin haka.

Da tunani da halin mutum duk abu guda ne. Kamar



yadda halin mutum yake fito da kansa ya nuna kansa, toh, hakama sigar mutum take. Ma'ana ita ce: a dangantakar *Hali* da *Rayuwa,* babu bambanci tsakanin zahirin mutum da baɗininsa. Mayanin da mutum yake iya lulluɓe baɗininsa da shi, shi ne na munafunci. Amma tunda gaskiya ɗaya ce, asirin munafuki yakan tonu lokaci zuwa lokaci. Ko Hausawa ma sukan ce: *'Munafunci Dodo ne ya kan ci mai shi'.* Wannan Magana da ma'ana take!

Harkokin kowanne mutum suna gudana ne a kan dokokin da ya sawa kansa, waɗanda ya tsara su cikin Tunaninsa; wanda shi kuma tunanin yake haifarwa a zahirin Halayensa da kuma kasancewar Halayyarsa; watau, yadda yake a raye. Tunanin mutum ashe shi ne makamashin rayuwarsa. Watau dai, a cikin rayuwa ba abinda yake faruwa haka siddan ba dalili. Komai sakamako ne na waɗannan saƙaƙƙun dokokin tunani a kowanne hali da mutum ya sa kansa, ko ya sami kansa ciki -ko na *wadatar-zuci* ko na *ƙuntatar-zuci.* Don hakane ya zama tilas mutum ya kasance cikin koyon darasi daga halin da yake ciki, ya kuma yi amfani da shi a cikin halin da zai zo masa nan gaba don ya aza dokokin rayuwarsa a tafarkin alhairi.

Shugabanmu, Muhammad (saw), yakan yawaita

cewar, *Fafutuka ita ce ɗabi'arsa.* Wannan doka babbar darasi ce, abar koyi ga ma'abocin nazari. Fahimtar wannan ita za ta ba wa Ɗan-Adam damar canja halayyarsa ko matsayinsa a kowanne lokaci; ita ce kuma za ta iya daidaita rayuwarsa da manufofinsa da bukatunsa. Amma idan mutum ya ɗauka cewar komai a sassaƙe yake tuntuni, ba kuma damar canjawa, to haka wannan mutum ba zai iya canja kansa ta kowacce hanya ba. Amma, idan mutum ya yarda cewar shi ne mai ikon canja abubuwan da suka shafe shi, kuma ya yarda shi ne kaɗai mai iya umartar zuciyarsa ta gyara tunaninsa na baɗini, to ba shakka, wannan mutum ya zama jarumi a kan tafarkin inganta halayyar rayuwarsa ta zahiri. Wannan barde yanzu ba shakka, ya zama mai galaba kuma uban-gidan kansa. Daga wannan lokaci mutum zai iya yunƙurin fafutukarsa da addu'o'insa don warkarda lahanin halayyarsa.

Kada mutum ya ce, ya ji Allah (swt) Yana cewa, "Shi ne *Mai arzurta wanda Yake so ba tareda awo ba",* ya ɗauka wannan alama ce sakamakon fafutuka da addu'a ba su da nasaba da ƙwazon mutum a kansu. Allah (swt) ba Ya nufin haka. Hasalima dai, Yana so ne ka tashi tsaye da gaskiyarka da ƙarfinka, da addu'arka, ka yi ƙoƙarin kanka, ka kuma yi amfani da irin baiwar



da Ya ba ka wajen gyara da inganta rayuwarka. Yana son ka nemi duk abinda kake so daga falalarSa domin Shi ne kaɗai Mai Arzurtawa. Amma lallai ne ka san cewar tabbatar arzikin yadda ka nema, ko ta wata hanya dabam, wannan IkonSa ne, ba naka ba; ba kuma na kowa bane. Shi ne Mai ba wa duk wanda Ya so, yawan yadda Ya so, ba tareda Ya ba wa kowa dalili ba. Da Allah (swt) Yana ba da dalili da Ya sha tambayoyi marasa ma'ana. Saboda haka, kɛɓe dalilin awon, nuni ne na Hikima, ba na zalunci ba, domin Allah (swt) ba Ya zalunci, ba Ya kuma ha'inci. Kada ka ɗau karin maganar nan da ake cewa: *"Zafin nema ba ya kawo samu"* tamkar hani ce gareka wajen nema yadda za ka iya. So ake ka lura da abubuwan da suka zama lallai ka yi su, in kana son ka samun, kuma yakamata ka san iyaka da sauran dokokin neman. Kada ka bar mutumcinka ko lafiyarka, ko ta wasu su salwanta a cikin nacin neman.

A naka, lallai ne kayi ƙoƙarin kanka kamar yadda Allah (swt) Ya ce, kuma ka ci gaba da ƙoƙarin har sai ka dace; watau, har sai an buɗe maka ƙofa. *"Sannu ba ta hana zuwa, sai dai a daɗe ba a je ba"* inji Hausawa. Kada ka damu da daɗewar in dai kana yin abubuwan da suka dace da samun a cikin fafurukarka tareda kiyayewar mutumcinka da

lafiyarka. Kodayake sukan ce, "*Zafin nema ba ya kawo samu",* za mu iya yin wata fassarar da cewar, wannan gyara ne kawai na magana, ko kuma matashiya ce don ka yi la'akari da iyakacin abinda za ka iya yi a kan bukata guda, da kuma iyakacin abinda mutumcinka da lafiyarka za su iya jurewa. Watau, kada ka salwantar da su a wajen neman. A kullum, lallai mutum ya san:

A Fafutkar rayuwa da buri, ba "nasara" yadda muke fassarata ce mafi muhimmanci ba; ita Fafutukar ce mafi muhimmanci, musammam in an hada ta da cikakkiyar addu'a saboda Allah. Fafutukar kadai za mu iya yi. "Nasara tana daga Allah". Kuma, Yana yawaita bayar da ita ta hanyoyi da dama, Ya kuma zaba mana abinda ya fi alhairi. Amma yawanci sai an lura za a gane.

Wanda bai yi fafutuka ba, kuma ya rasa, shi yake da-nasani. Wanda ya yi fafutuka bai samu ba, shi yake da ilmi da damar sake daura damara don gaba. Wadansu, in sun kasa cimma burinsu, sai su karaya su watsar da fafutukarsu. Wannan kuskure ne. Babu asara ko kadan a cikin fafutuka wadda aka yi ta a kan abinda ya dace. Duk wanda ya bar wa Allah (swt) amanar fafutukarsa, to ba shi da wata damuwa, ko ya cimma nasara a yadda ya



nemeta, ko bai cimmata a yadda ya nemeta ba.

Wadatar zuci takan samu ga duk wanda ya yi fafutuka saboda Allah, ko menene sakamakon, domin fafutukar ita ce kaɗai abar da zai iya yi. Kamar yadda na ce, *Nasara tana daga Allah,* kuma duk mai la'akari da nazari, ya san an sami nasarar ta wasu hanyoyin. A wannan matsayi, tuni mutum ya sarrafa tunaninsa a tafarki mai kyau, ya kuma ci ɗamara don gaba. Sai a jira wata damar.

Ba shakka, zuciya ita ke taɗo ababan kwaɗayinta; haka kuma ita ce mai tofarda ababan ƙyamarta, har sai ta cimma matuƙar bukatarta. Duk wata ƙwayar tunani da aka shuka a zuci, a nan take yaɗo ta yi furanninta, har sai ta sami damar bayyana kanta. Ashe kuwa duk tunanin kirki, to furannin kirki zai tsirar a zuci. Haka tunanin banza furannin banza zai tsirar a zuci. Watau, duk abinda *ka shuka,* ko da a zuciyarka ne, *shi za ka girba.* Tuni kuma mun san cewar, halin rayuwar da mutum ya taso cikinta, ko ya shigeta, ko yake ciki, yana shafar irin tunaninsa, har ma da irin halayensa da halayyarsa.

Girma cikin mutanen kirki masu mutumci, yakan sa mutum ya koyi halayen kirki da mutumci. Zama cikin 'Yan Caca, yakan sa mutum ya iya ta, koma

ya zama ɗanta. Rashin kular iyaye takan sa ɗa ya zama taƙadari, lalatacce. Rayuwar ƙunci takan iya haifar da halin fushi ta jefa mutum cikin wasu rigimun. Rashin makaranta shi ke kawo jahilci har ma a tafi a bar mutum a baya. Ga misalai nan dai da yawan gaske a kewaye da mu. Ashe, ba shakka, halayyar muhalli da hulɗa muhimmai ne wajen gina hali da tunani. Haka, mun san ana cewa, *mutum da irin abokansa ake shaidarsa.* Hausawa da hikima suke! In ka nazarci karin maganar ƙabilu da jinsina kaɗai, ba shakka za ka ci riba. Yawancin fahimtarsu ta rayuwa tana cikinsu.

Lallai mu san cewar duk abinda aka shuka a zuci, aka kuma ƙyale shi ya yi furanni a zucin, to, ko badaɗe ko bajima, sai ya ɓullo a fili a aikace a duk yayin da halin aikatawar ya samu. Son rai da kuma buri, duk tunani ne a kan tafarkin aikata wani abu, ko a kasance wani abu da zarar damar ta samu. Ka ga ashe, yadda tunanin baɗini (ƙulle-ƙullen zuci), yake shafar halayyar zahiri; haka halayyar zahirin itama take shafar tunanin baɗinin, har sai mutum ya aikata tunanin sannan zuciyar za ta cimma burinta. Kamar maye ne ya sa ƙwalamar maitarsa a kurwar wani. Sai ya ci zai sami hutu. Ba a sanin maye sai ya kama mutum. Amma, tunda maye ne, wataran zai kama da dama ta samu.



Mutum ba ya ba da sadaƙa, ko ya yi sata haka siddan, ko kuma don haka aka rubuta masa. A'a yana yin waɗannan abubuwa ne domin su ya ƙulla a zuciyarsa, kuma yake son aikatawa. Mutum mai hankali da tsarkakkar zuciya ba zai aikata miyagun ayyuka haka katsahan don zuga, nishaɗi, ko don wata wahalar duniya ta ɗan shigo masa ba. Da ma can zuciyarsa tana tanɗo bukatar aikata waɗannan miyagun ayyuka a asirce, har sai da dama ta samu ya kuma aikatasu. *Dama ba ta iko da mutum, fassara shi kawai take yi.* Watau, ganin galala ba za ta sa mai gaskiya sata ba; duk wanda ya ɗauka ba izni, dama can akwai saƙar sata a zuciyarsa. Duk wanda ya zageka, dama sha'awarsa kenan. Haka duk wanda ya gaisheka cikin raha da zumunci.

A yawancin lokuta, mutum ba ya jawowa kansa abinda ba ya so, sai dai abinda dama shi shi ne. Ba ka jawowa kanka rigima, sai dai dama in kai dan-rigima ne, ko kuma ita kake son yi a lokacin. Ko da Giya tana sa rashin kunya; mai son yinta, sai ya sha ya ce ita ce. Mutum ba zai tare a ƙofar gidan wasu ba aikin yi ba, sai dama in shi malalaci ne, ko mai son banza. Mace ba ta karuwanci, sai dama in lalatacciya ce. Alƙali ba ya zalunci, sai dama in shi makwaɗaici ne, ko maƙetaci. A zukatan mutanen banza, ƙulle-ƙullen banza. A zukatan mutanen

kirki, shirye-shiryen kirki. Bukatunsu duka a zuci suke, kuma daga nan suke wanzarda su a fili su aikata ashsha, ko su aikata alhairi.

Ina masu cewar, '*Matsuwa ce ta sa ni*"; ko kuma, *"Komai haka Allah Ya shirya".* To hakane ta wani fanni, amma kada su manta Allah (swt) Ya yi alkawarin yin cikakken Hisabi a ranar gobe ƙiyama. Hisabi kuwa, tunasarwa ce da gargaɗi ga ɗan-Adam cewar shi (ɗan-Adam ɗin) ke riƙe da makomarsa tun daga ayyukansa a wannan duniyar. Allah (swt) Ya ba mu hankali da iko a kan hankalin, sannan Ya taimakemu da shiriya (tamkar shawarwari) a kan yadda za mu inganta rayuwarmu. Ya kuma zayyana mana horo iri-iri da lada iri-iri; Ya kuma ba mu labarin Wuta da Aljanna. Saboda ƙaunarmu da kuma son mu shiryu, sai Allah Ya kuma sauko mana da Littattafai (kamar Al-Zabura, Al-Taurat, Al-Injil da kuma Al-Kur'ani Mai-Tsarki a ƙarshe, wanda ya ƙunshi duk waɗancan). Tare kuma da waɗannan littafai, Ya sake aiko mana da AnnabawanSa, domin mu koyi darusan rayuwa ingantacciya. Ba shakka, a addinanmu muna da duk abubuwan da suka kamata mu yi amfani dasu don kyautata *tunaninmu*, tace *halayenmu* da kuma inganta ilahirin *halayyarmu*. Waɗannan lallai ne su



zama shika-shikan manufar rayuwa in dai mutum yana nemarwa kansa makoma ta alhairi a wannan duniyar da kuma can lahirar.

Masu tunani zurfaffa sun san, da ba mu ne masu iko da zaɓin tunaninmu da ayyukanmu ba, da Allah (swt) Bai aiko mana da shiriya ba. Dá hakane, da babu Hisabi. Dá hakane da babu horon Wuta ko sakayyar Aljanna. Dá hakane da ba dalilin addini, balle irin ibadunsa. Sannan kuma, dá duk waɗannan hakane, dá maiyiyuwa ne Allah (swt) Bai halitto mu yadda muke ba, tunda Ya ce dalilin halittar mu shi ne mu bauta maSa. Amma saboda alkawarin Hisabi, sai Ya bamu zaɓin mu bi, ko mu ƙi, daga ƙulle-ƙullen tunaninmu. *Rayuwarmu da makomarmu tana hannunmu.* Ashe, imani shi kansa a cikin ƙoƙon tunaninmu muke sassaƙa shi. In mun ga dama mu yi imani; in mun ga dama mu bi son zuciyarmu na sheɗanci.

Abu biyu kawai da bamu da iko a kansu a wannan duniya tamu sune *KUDRA DA IRADA*. Su kuwa waɗannan ikonni, ba yadda za mu iya yin iko da su, domin Allah (swt) Ya bar wa kanSa iko da su, Shi kaɗai. Da duniyarmu da sauran duniyoyi da dukkan abubuwan dake tsakaninsu; kai, dukkanin Sararin Samaniyar gaba ɗayansa, da dukkanin

abinda ke cikinsa, da Kudra da Irada Allah (swt) Yake sarrafa shi. Komai da komai, har da mu kanmu, sakamakon KudrarSa da IradarSa ne.

Amma, ikonnin Allah da suke tafiyarda rayuwarmu a cikinmu suke ba a wani guri suke ba. Waɗannan ikonni a halittarsu, mun sansu sarai, domin su ne zuciyarmu da ƙwaƙwalwarmu. Zuciya ta sarrafa ranka; ƙwaƙwalwa kuma ta sarrafa rayuwarka. Tunaninka a tsakaninsu yake tsira ya kuma yaɗu. Allah (swt) Shi ne Yake da iko a kan rayuwar waɗannan; amma kai ne kake da iko a kan yadda ka za ka yi amfani da su da yadda za ka gyara lafiyarsu. Tunaninmu shi ne abincinsu. Sannan kuma ayyukanmu sune amansu.

Mutum, kamar yadda muka sani, shi ne mai iko da kansa. Idan ka ga dama sai ka tashi ka faɗa rijiya. Idan ka ga dama ka tashi ka yi nafila. Idan ka ga dama sai ka tsabtace kanka; in ka ga dama ka mari mutum, komai ta fanjama fanjim. Idan ka ga dama ka nemi ilmi; idan ka ga dama ka yi taurin bashi ko ma ka ƙi biyansa, alabarshi a la'anceka; idan ka ga dama ka duƙufa wajen rubuta littafi mai amfani. Idan ka ga dama ka yi fafutuka; idan ka ga dama ka watsar ka zama ɗan daba ko ɗan ƙwaya. Duk ya rage naka da ganin damarka.



Tunaninmu da ayyukanmu su ne sukan zama ƙangi ko ‘yancin makomarmu. Su ne suke jefa mu kurkukun talauci, ko na rashin mutumci. Su ne za su iya jawo mana zagi ko wani bala’i dabam, idan muka zaɓi tunanin sharri da aikata shi. Amma kuma su ne mala’ikun rahamarmu masu ‘yantarda mu izuwa daular bushasha da mutumci, idan muka zaɓi tunanin alhairi da aikata shi.

Mutum ba ya samun abinda yake so, ko ya roƙa wajen Allah (swt), sai abinda ya dace ya samu. Ka yi karatu sosai tukuna, sannan ka roƙi Allah Ya sa ka ci jarrabawa. Ka nemi maganin cutarka tukuna, sannan ka roƙi Allah Ya kawo sauƙi da waraka. Ka fara ciniki kafin ka nemi riba. Ka yaɓe gidanka kafin damina ta zo, domin yin haka ne kaɗai zai kare gininka. Ka ƙulle kantinka da kyau, sannan ka roƙi Allah Ya tsare maka shi. Watau, lallai ka fara yin abinda yakamata ka yi tukuna. Da bukatun mutum da addu’oinsa duka suna karɓuwa ne idan sun dace da tunaninsa da ayyukansa. Kada ka yi ƙaranci a cikin abinda yakamata ka yi, sannan ka ce za ka yi kukan Allah (swt) Bai taimakeka ba. Allah (swt) da kimiyya Yake aiki, kuma tuni ya tsara yadda komai zai tafi. Ba abinda Allah (swt) ba Zai iya yi ba. Amma akwai abubuwan da ba Ya yi, domin ba haka Ya tsara ba.

Mai hassadar matsayin wani ba zai sami wannan matsayin ba ko da ya roƙa, domin matsayin bai dace da tunaninsa da ayyukansa ba. Idan kuwa ya samu, to halaka ce gareshi. Sai mutum ya zama sarki, amma babu sigar sarkin; ko kuma ya zama don wani tsautsayi a gaba. Sai mutum ya sami kuɗi babu arziki; ko kuɗin su sa shi cikin wata halaka da baƙin ciki. Sai mutum ya sami ɗaukaka, amma ya ƙarke a kurkuku. Sai ka ga tafkekiyar gona babu tsiro ta zama daji. Haka za ka ga wasu shirim ba ci ba. Ga matsayi babu mutumci; ga kuɗi babu masoya; ga sarauta babu Mulkin, ba kuma talakawam; ga ilmi ba ɗalibai.

Amma mai sha'awar matsayin wani, wanda kuma ya yi ƙwazo da fafutuka saboda Allah, sai ya sami matsayin in ya dace da wannan sha'awar da fafutukar. Irin waɗannan mutane su ne suke cin ribar abinda suka samu ko suka zama. Ta hanyarsu kuma alhairi iri iri ya tsiro wanda zai amfani jama'a masu yawan gaske. Ta nan kuma su sami biyan wata bukatar daga Allah (swt), su kuma tarar da alhairi a lahirarsu. Duk kuma daga kyaun tunaninsu.

Mutane suna son su kyautata matsayinsu da halayyarsu, amma ba sa son su kyautata kansu. A

hali irin wannan, sukan kasance cikin ƙangi na rashin ci-gaba da rashin biyan bukata. Duk mutumin da yaƙi fahimtar kansa, yaƙi gyara zuciyarsa, yaƙi yin fafutuka don kansa, ba zai taɓa cimma bukatar da ya shuka a zuciyarsa ba. Wannan haka yake, ko mecece bukatar; kuma ko da ta duniya ce, balle kuma ta lahira. Tamkar mutumin da ya ɗaura niyyar tafiya ne, amma bai fito daga gidansa ba. Ba inda za shi duk ƙarfin niyyarsa, don bai yi abinda yakamata ya yi ba. Bai ɗauki taƙar farkon da ta zama tilas ba.

** Ɗauki mutum wanda ya kamu da ciwon sukari. A shirye yake ya biya munƙudan kuɗi, ko ya yi wata ɗawainiya don neman maganin cutar, amma ba ya son ya daina shan zaƙin. Watau, yana son ya biya bukatar shan zaƙinsa, kuma har-wa-yau yana son lafiyarsa. Wannan mutum bai cancanta ya zama mai lafiya ba, domin bai koyi komai daga darasin sadaukarwa ba. Rashin azancinsa ya dulmiyar da shi; son-kansa (ko ma mu ce, ‘ƙin kansa’) ya raraki bukatarsa. Ya zama shashasha mara la’akari.

** Ɗauki misali, Dan-kasuwa da ya shahara wajen Algus da zafafa farashi; illoli biyu a kasuwa daga macuta. Idan mutane suka komar da cinikinsu

ga masu gaskiya da tausayi, sai ya yi ta fusashin ana guje masa, ba ya duba nasa laifin; har ma ya ringa sa ƙabilanci a cikin al'amarin. Wannan mutum ya zama sakarai. Har abada ba zai yi arziki ba, kuma ba zai inganta matsayinsa a kasuwar ba. Shekara bayan shekara, haka zai kasance ba ci gaba, kullum a cikin wannan rumfar, in ma ya ci sa'a. Haka wasu suke ta ƙorafi ba son gyarawa.

** Ɗauki malalata masu son banza, waɗanda suka ƙi neman aikin yi ko wata sana'a, amma suna zargin wasu na dannesu. Irin waɗannan mutane ba sa tunanin amfani da wata baiwa da Allah (swt) Ya yi masu, balle su yi amfani da ita wajen inganta kansu. Sun fi sha'awar su shantake a gaban wani, ba sa kishin kansu. Irin waɗannan mutane haka za su rayu a banza, suna gani ana ta shigesu. Su yi hasara a duniya, su kuma yita a lahira.

** Ko kuma ɗauki al'umar da ba a biyan haraji; ba sa haɗa kai ko jaddawa hukuma gameda aikata gaskiya, amma suna ta zage zagen cewar an ƙi gyara matsalolin rayuwarsu. Irin waɗannan mutane ba su fahimci ma'anar 'yanci ba, ba su kuma san cewar kwabonsu na haraji shi ne zai ba su haƙƙi a cikin milyoyin Baitul-Malin ba. Wanda bai biya haraji ba, ya rasa wannan haƙƙin.

** Ko kuma ɗauki jama'ar da suke yabon shugabannin banza; suke kai caffa ga macutansu; suke zaɓar waɗanda ba su dace ba, su kuma sun ƙi taɓusawa, amma kuma suna ƙorafin banzaye na mulkarsu; ko ana fasa Baitul-Mali ana cinye kuɗaɗensu. Shekara da shekaru, amma sun kasa ɗaukar darasi, sai ihu a kasuwa wai an dannesu, an hana su ci-gaba. Ba sa tsayawa su yi tunanin su ne suka bada iznin a cuce su. Irin wannan al'umma ba za ta ci gaba ba, sai talakawa sun san haƙƙinsu da mutumcinsu. Sai sun sa masu mutumci da gaskiya da ƙwarewa a gaban harkokinsu.

** Ko kuma ɗauki Mai-gidan da ya dakushe rayuwar yaransa; ko yaran-gida da suke cutar mai gidansu, amma dukkaninsu suna sha'awar inganta matsayinsu. Idan al'amuransu suka lalace sai su ringa zargi ba tareda nazarin nasu illolin ba. Mai Gidan ko Mai Kantin ya ƙi biyan haƙƙinsu, su kuma yaran suna yi masa sata. Dukkaninsu sun yi hasara daga illar son zuciyarsu.

** Ko kuma ɗauki iyayen da suke jin daɗin karɓar kuɗi da turare wajen 'yarsu mara aure mara aikin yi, amma suna kukan ta lalace; wai ba yadda za su yi da ita. Sun manta su suka zugata ta wajen kau da fuska daga sharrukan da ta ke aikatawa.

** Ko kuma ɗauki mai ƙaramin jari, da ya je ya ƙaro aure, ya kuma canja mota, ko ya fente gidansa don riba ta ɗan ƙaru. Amma kuma idan ya kasa inganta cinikinsa, ko ya karye gaba-ɗaya, sai ya ringa la'antar wasu da jawo masa hasara, ya manta da nasa almubazzarancin.

Mutum, ba shakka, shi yake riƙe da makomar halayyarsa, domin shi kaɗai zai iya gyara rayuwarsa. Kowa ya san kansa fiye da yadda wasu suka san shi. Wanda yake neman ci-gaba da ingantuwa, amma kuma yana ta ɓata hanyarsa da ƙazaman tunani da ayyuka, ba yadda za a yi ya cimma waɗannan bukatu. Bari in sake nanatawa: 'Kowa ya san kansa fiye da yadda wasu suka san shi'. Mutum ya iya bin diddigin tunaninsa da ayyukansa ya ga ko sun dace da neman biyan bukatarsa. Da kansa zai iya zama alƙali a kan dalilan nasararsa ko hasararsa.

A nan, za mu yi la'akari da cewar matsalolin da ke shafar *nasara* ko *hasara* suna da wahalar fayyacewa, domin ba a kodayaushe suke zama daidai ba. A cikin halayyar rayuwa, abubuwan da za su iya haifarwa wani farin-ciki, sai kuma su haifarwa wani baƙin-ciki. Mutum ya iya kasancewa mai gaskiya da aiki tuƙuru, amma



kuma ma'abocin wahala. Haka kuma, akan sami macuci mara gaskiya, amma kuma ma'abocin wadata. A zahirin rayuwa, ba kasafai irin waɗannan misalai suke faruwa ba tareda dalili ba, ko ta yaya muka auna rayuwar. Kada mu ɗauka cewar mai gaskiyar ya rasa wadatar ne don shi mai gaskiya ne; ko kuma macucin ya sami wadatar ne don ya yi cuta. Idan muka ɗau haka, to mun kai tunaninmu ƙarshen bango, kuma tunani irin wannan wanda bai ba da wata 'yar kafa ta wani dalili dabam ba, kuskure ne.

Maiyiwuwa ne, mutumin da muke ganin mai gaskiya ne a zahiri, yana da wani aibu a baɗininsa. Haka, wanda muke gani macuci ne, maiyiwuwa ne yana da wani abin kirki tareda shi, kuma wannan wadata ta samu ne saboda wannan abin kirkin. Ko ta yaya dai, Mai gaskiyar zai ci ribar gaskiyarsa a inda ya aikatata, amma kuma zai yi hasara daga aibun da ke zuciyarsa na sharri. Shi kuma mara gaskiyar zai yi hasarar baƙin tunaninsa a inda ya wanzar da shi, amma kuma zai ci ribar tunaninsa na kirki a inda ya aikata shi.

Wannan matsala, kamar yadda na ce, tana da wahalar warwarewa, musammam ma ga mai gaskiya da aiki tuƙuru wanda yake cikin wahala.

Za mu tarar da wannan magana a can gaba.

‘Me yasa mutanen kirki suke shiga wahala?’ Ba shakka, wannan tambaya ce wadda yakamata a amsata a nutse da basira. Waɗansu imaninsu yakan bar su ɗungum, ko kuma ya raunana duk lokacinda tunanin matsalolin rayuwarsu ya ɗan giftawa ƙwaƙwalwarsu. Sukan bincika yadda za su iya, amma sukan kasa samun amsar da za ta gamsarda su. Sun ga sun yi fafutukar, sun gwada gaskiyar, sun yi ibadar, sun yi addu’ar, sun nuna mutumcin da yakanar, amma ina! Maimakon abubuwa su gyaru, sai daɗa taɓarɓarewa suke. Amma fa duk a ganinsu, domin watakila ba su auna wasu abubuwan ba. Hankulansu suna wasu guri dabam.

Ba za ta yiwu a san takamaiman dalilan da suka sa mai gaskiya ya ƙasƙanta ba, sai an tace tunaninsa, an tankaɗe an kuma rairaye ƙulle-ƙullen zucinsa. Sannan ne kaɗai za a san ko ƙasƙantakar tasa sakamakon kyaun niyarsa ne, ko kuma ta mummunar aniyarsa ce. Amma, idan shi da kansa, ya nutsa sosai a cikin tunaninsa, kuma fi-sabilillahi, to zai tarar da babbar dokar nan ta Allah (swt) mai cikakken adalci, wadda ba yadda za a yi ta yi sakamakon tunani ko aikin kirki da sharri; ko kuma aikin sharri da sakamako mai



kyau. A irin wannan matsayi, mutum, zai iya komawa baya ya binciki jahilci da makantar rayuwarsa, har sai ya tararda dalilan da suke kawo masa cikas a rayuwarsa. Haƙiƙa, gaskiyar wasu takan sa su cikin wahala, domin al'umarsu ta banza ce wadda ba ta son mai gaskiya. Sai dai irin wannan wahala, ba sharri ba ce ga mai shanta. Babban alhairi ce a gaba, kuma a wajen Allah (swt). Haka akwai masu jin daɗin rayuwarsu domin su marasa gaskiya ne, ko kuma 'yan iska ne, ko kuma marasa kunya ne. Harwayau, suna jin daɗin ne domin suna cikin al'umar banza wadda ba ta ƙyamar mutane irinsu. Sai dai irin wannan jin daɗi ba alhairi ne ga mai shansa ba. Sharri ne babba a gareshi a lokaci mai zuwa. A kowanne hali, mun san: *Allah ba azzalumin kowa bane.* Za mu nanata wanan magana a gaba.

Wanda ya ƙuduri alheri, ya kuma aikata shi, to, zai ga alheri. Wanda ya ƙuduri sharri, ya kuma aikata shi, to, lallai zai ga sharri, ko badaɗe ko bajima. Wannan doka a rayuwar ɗan-Adam ba yadda za a yi ta canja, duk runtsi. Kada mu manta cewar, wasu mutane ba kasafai suke fahimtar irin baiwar da Allah Ya yi masu ba. Wasu kuma sukan fahimta, amma sukan raina, saboda hankalinsu na kan wani abu dabam da suke ganin ya fi wannan baiwar da

Allah Ya yi masu. Ba wata baiwa da Allah Ya bayar wadda ba za a iya amfani da ita a cimma muhimmin burin rayuwa ba. Sai dai in an raina ko ba a bincika ba.

Sai ka ga mutum yana ta addu'ar neman rufin asiri, ashe tsabar kuɗi yake so, bai fahimci ma'anar rufin asirin ba. Wani ka ji yana neman matsayi, amma ya san bai dace da shi ba. Harwayau, ga mai kuɗi kuma ya kasa gamsuwa don bai sami saurauta ba. Ga ɗan-Kasuwa ya ƙwallafa ransa a kan sai ya raunana wani. Sai ka ga manomi yana wahala da kwangila, ko kuma talaka yana neman auren mata ta biyu ko ta huɗu, ga 'ya'ya barkatai, yana cewa, "bakin da Allah Ya tsaga.....". Haka dai za ka ga mutane iri iri suna fankama iri iri cikin bukatu marasa ma'ana a garesu. Gaba ɗaya sun fita daga tsarin rayuwar da ta dace da su, sun shiga wata can dabam. In sun shiga wata wahala ko wata masifa, mun san inda za su jefa ƙorafinsu: Sukan ce, "Allah ne Ya jawo masu!" Wannan Jahilci!

Mutane irin waɗannan ba sa cikin lissafinmu, domin sun ƙaranta a wadatar zuci, sun ƙaranta a tunanin abinda zai fi masu alhairi. Ba su fahimci Allah (swt) sosai ba. Kuma, sun sha bamban da irin waɗanda muke zance a kansu.




Ko da a cikin neman biyan bukatu ma, mun san cewar, *duk abinda ka shuka shi za ka girba.* Ba za ka shuka Dawa ka girbi Gero ba. Haka ba za ka tatsi Zuma daga Saniya ba. Akwai abubuwan da za su iya faruwa, ko za a iya yi, ko samu; akwai kuma waɗanda ba haka bane. Wasu abubuwa ba za su canja ba, don kawai mun neme su, ko don mu ne. Tilas mutum ya fahimci wannan doka ta rayuwa kuma ya yi la'akari da ita. *Sa'a*, ita kanta, ba ta samun wanda tunaninsa ba kimtsatstse bane. A kodayaushe tafi son ta taimaki gwarzo wanda tunaninsa ya yi saiti a kan fafutukarsa. Ko da za ka ci Sa'a, to sai ka gwada nema, ko yin abin tukuna ta hanyar tunani ƙwaƙƙwara. Duk da haka, ba za ka ci Sa'a a kan abinda bai dace da kai ba, ko abinda ba zai yiwu ba. Duk wanda ya ci Sa'a, to dama can zuciyarsa da ƙwazonsa a shirye suke su karɓeta. Ba mai iya rarrabe mutane irin Sa'a, domin ba a cinta a banza.

A dandalin sakamakon rayuwa, *dukiyar kudi* gefe ce kawai. Wataƙila duk ganin wahalolin nan namu yakan faru ne saboda taƙaita sakamakon rayuwa cikin dukiyar kuɗi kawai. Watau, ba ma duba sauran abubuwan da Allah (swt) Ya yi mana na sakamako da su. Misali: Kamar shugabanmu, Muhammad (saw), za mu iya sa *Wadatar Zuci*, a

tsarin sakamakon ayyukan kirki a rayuwarmu. Haka, *Rufin-Asiri, Mutumci a idanun Jama'a, Yawan Tuna Allah, Soyayyar jama'a, Hikima da zurfin Tunani, Iyali na-gari, Damina da girbi masu kyau, Kwanciyar-rai, Kwarjini,* da *lafiya.* da sauran irinsu birjik. Duk waɗannan sakamako ne da Allah (swt) da Yake ba wa bayinSa a dalilai dabam dabam. Rashinsu, ba shakka, hasara ce ga waɗanda suka rasa su a dalilai dabam dabam.

Dukkanin waɗannan abubuwa, da wasu da yawa, a tsarin *"ARZIKI"* suke, kuma in shi ne ma'auni, to, wahalunmu, ko hasarunmu, kaɗan ne. Wanda ya san, ya kuma fahimci haka, to, zai ga sakamakon ayyukansa: Na alhairi a cikin Arziki. Na sharri kuma cikin Nadama da raina matsayi. Duk wanda ya yi tunani mai zurfi, to kuwa zai gode Allah (swt), domin Shi ba azzalumin kowa bane.

Za mu ga haka a Babi na 7, insha'Allah. Na tunkari wannan al'amari gaba-gaɗi a can. Amma a karanta a hankali a nutse.





3



"Wahala da Wadata

"Mahakurci, Mawadaci"

Yin la'akari da jawaban baya, zai saukaka fahimtar cewa, ita wahala kusan a kodayaushe sakamako ce ta gurbataccen (ko karkataccen) tunani. Watau wahala, nuni ce ga alamar mutum ya fita daga tsari na kirki. Shan wahala, ko shiga cikinta, alama ce ga mai hankali cewar yakamata ya fara tunanin tsarkake kansa, ya sabunta kansa, domin ya nemawa kansa rayuwa wadda ta dace da tsari nagari. Watau, lallai ne ya sake sabon tunani.

Kamar dai "Ciwon Kai" ne, yadda yake nuna alamar wani abu a jiki ya tabu. Nan da nan sai a yi bincike a nemi magani. Ashe, "Wahala" ita ma

ciwon-kai ce ta rayuwa. Wanda ya fahimci ya fara shigarta, lallai ne ya binciketa, ya nemi dalilinta da maganinta. Tilas ne binciken ya sanarwa kai, ko wahalar ta gaskiya ce, ko kuwa ta son zuciya ce da rashin gode Allah, kamar dai wahalar neman abinda bai dace da kai ba, ko ta ɗaukar nauyin da bai dace da kai ba. Ɗaukar wannan mataki nan da nan shi zai sa mutum ya gyara tunaninsa domin tunkarar gyaran halayyarsa.

Kafin mu yi nisa, yakamata mu tambayi: wai shin, “Mecece Wahala?” A gaskiya, “wahala” tana da wuyar fassarawa, ko mu ce ‘wahalar’ fassarawa. Amma daga wannan batu, za mu fara fahimtar ma’anarta. A taƙaice, za mu iya cewa, ita ce: “abinda aka kasa yi”, ko kuma, “ake yi da kyar”. To, wasu sa iya tambayar: tilas ne sai an yi abinda ba za a iya yi ba? A nan maganar take. Idan ya zama tilas a yi wani abu, amma babu halin yi, to akwai alamun za a iya shiga wahala a kan wannan al’amarin. Wanda ya hango haka, lallai ne kuma ya fara neman mafita, watau yadda zai yi ya kwarawa wannan matsala ruwan sanyi tun kafin ta zama wahalar. Yawancin wahalu, mutane suke jawowa kansu, amma yawanci ba tareda sani ba, saboda rashin hangen nesa. Akwai kuma mutane da suke sa kansu cikin wahala a kan dalilan da



basu cancanci halayyarsu ba. Amma a gaskiya akwai da yawa waɗanda ake jawo masu ita, sai dai in ka duba sosai sai ka tarar cewar sune suka ƙyale ake jawo masu ita. Watau, suna gani sun ƙi su kauce gabatowarta ko yin maganinta in ta ison.

Kada a ɗauka a nan cewar, wahala nuni ce ta cewar wanda ya shigeta mutumin banza ne. Ko kaɗan ba haka ce manufa ba. Fita daga tsarin kirki, yanayi ne na tunani wanda ba zai taimakawa mai yinsa samun masalahar rayuwa ba. Rashin wannan masalaha shi ne sanadiyar taɓarɓarewar al'amura, watau, tushen samuwar wahalar; kamar yadda rashin tsarkin zucin ya zama ummul-aba'isin raunannan tunanin. Wanda ba shi da kuɗi, ko matalauci, ko faƙiri, ba ya cikin wahala har sai zuciyarsa ta fara saƙa masa wasu bukatu da ba su dace da matsayinsa ba. A wannan hali ne ake shiga cikin ƙuntatar zucin dake haifarda wahalar. Haka, 'sai na yi abinda wane ya yi', ita ma mataki ce ta shiga cikin wahala, musammam ma in gasar ba ta alhairi ba ce. Mutumin da ya raina matsayi, ko hanyar da Allah (swt) Ya zaɓar masa, ya maida hankalinsa kan wani matsayin, ko wata hanyar da ba ta dace da shi ba, to sai ya shiga wahala, ko badaƙe ko bajima. Haka mutumin da ya ɗora, ko ya tsara rayuwarsa a kan ƙarya, to wataran sai

Gaskiya ta yi halinta. Daga rannan kuma an shiga wahala da jin kunya.

Matalaucin, ko faƙirin da ya yi tsab da tunaninsa, ya kuma shirya canja halayyarsa ta wajen wani yunƙuri ko wata fafutuka ta alhairi, to a hankali Allah (swt) Zai taimaka masa da hikimar da za ta fitarda shi daga ƙangin talaucin ko faƙircin. Babban wahalalle, shi ne mai neman abinda bai dace da shi ba; shi ne kuma mai nema don fariya ko don rashin gode Allah, ko don gasa. Shi ne kuma, mai son aikata abubuwan da suka fi ƙarfinsa, ko waɗanda ba su dace da shi ba. Wasu na sane suke jawo wan kansu wahala, saboda ragwanci ko saboda wawanci, ko don son su burge. Masoyanka ba sa bukatar burgarka; maƙiyanka kuma ba za su burgu da burgar taka ba. Saboda haka menene kenan amfaninta?

Idan ka haɗa ma'anonin waɗannan batu, za ka tarar cewar, a fannin farko, ita kanta wahalar da ake zaton ana ciki, saƙa ce ta zuciyar da ba ta wadata daga sauran baiwoyi da mutum yake da su ba. Ko kuma, a sauƙaƙe, zuciyar da ba ta binciki sauran kyautuka da Allah (swt) Ya yi waɗanda za su iya cike gurbin wahalar da ake zaton ana ciki ba. A fanni na biyu, son zuciya da rashin gode



Allah, da son iya yi, su kansu wahalu ne matsananta wadanda suke haifarda wasu wahalun dabam. Wanda ya ɗaukarwa kansa abinda ya fi ƙarfinsa, ba shakka shi ya gayyaci wahala.

Mun san wahala a gun wani, ba wahala ce a gun wani dabam ba, domin ba matsayinsu da halayyarsu ɗaya ba. Amma a yawancin lokaci, wahalar wasu ta haifu ne daga kwaɗayi, ko kishi ko ƙyashi, ko gasa, ko kuma hassada. Wani in ba shi da kuɗi, sai zuciyarsa ta raya masa yana cikin wahala, duk da sauran abubuwan da ya mallaka. Wani kuma ga kuɗin, amma hankalinsa na kan wani abu dabam da ya rasa. Wani yana da bukata, amma baya son ya sarrafa baiwar da Allah (swt) Ya yi masa wajen neman abin biyan wannan bukatar. Wani wahalarsa matarsa; wani 'ya'yansa; wani dukiyarsa; wani kwaɗayinsa; wani rashin gaskiyarsa da rashin mutumcinsa; wani ra'ayinsa; wani maƙiyansa; wani kuma lalacinsa ko rashin dauriyarsa. Duk waɗannan da sauransu da yawa suna da magani, in an yi tunani mai tsarki a tsanake a kansu, an kuma aikata abubuwan da suka dace.

Zurfaffan tunani mai kyau shi ne zai taimaki mutum wajen feɗe wahalar da gurɓataccen tunanin ya haifar; ya wanke gubar wahalun har sai an

cimma wadatar zuci ta wajen tunowa da ni'imomin da Allah (swt) Ya bayar tuni, amma wadanda baƙin tunanin ya rufe. Irin wannan tunani yana daga cikin muhimman hanyoyin da mutum zai iya gina zaman lafiya da kansa, ya kuma godewa Allah (swt), ko mecece halayyarsa a idanun mutane. Idan ka daka ta mutane, ko ka ce rashin wani abu da ka rasa illa ce, to ba shakka, ka shigar da kanka cikin wahala. Sarrafa abinda kake da shi wajen sauwaƙe wahalarka. Girman kai ba naka ba.

Duk tsanancin halayyarka, akwai wanda ya fi ka. Duk jin daɗin rayuwarka, akwai wanda ya fi ka. Mawahalci shi ne mai duban na sama da hassada, ko duban na ƙasa da fariya. Ma'abocin wadata shi ne wanda ya dubi na sama da farin tunani da addu'ar shi ma Allah Ya taimaki fafutukarsa ta kai shi fiye da haka. Sannan ya dubi na kasa da godiya da ni'imomin da Allah Ya yi masa, ya kuma tausaya ya taimaka. Amma duk wanda tunaninsa a kan abinda ya rasa ne; da wanda ya kasa daidaita bukatunsa da halayyarsa, to ya shiga wahala.

"Wadatar zuci", ba dukiyar kuɗi ba; ba yawan 'ya'ya ba; ba mulki ba; ba gida mai tsada ba, ba kyakkyawar mace ko miji mai kuɗi ba; ita ce babbar ma'aunin tunani wanda ya kasance



kyakkyawa, kuma ita ce alamar rayuwa mai albarka da arziki. Haka kuma, "Wahalar-zuci", ba rashin kuɗi ba; ba rashin 'ya'ya ba, ba rashin sauran adajen duniya ba, ita ce ma'aunin tunani mummuna, da rayuwa mai ƙunci. Kowa ya yi tunani a nutse cikin gaskiya da kishin-kai, to kuwa lallai a sannu zai sami amsarsa.

Ma'ana a nan ita ce: Mai-Kuɗi ya iya zama tsinanne; Talaka kuma mai-albarka, kamar yadda aka fi samu. Amma, *Kuɗi* da *Albarka,* ba yadda za a yi su haɗu a kan mutum guda, sai in kyakkyawan tunaninsa ya haifar da kyakkyawan amfani da kuɗin. Wannan mutum shi ake kira *Mai-Arziki.* Mutumin da Allah (swt) Ya rufawa asiri, ya lulluɓe shi da mutunci da yawan tuna Allah, ba shakka, yana cikin masu arziki na ƙwarai, ko da ba shi da jarin ƙwandala. Jarinsa shi ne wadatar zucinsa da zaman lafiyarsa, a lungunsu ko a ƙauyensu cikin mutuncinsa da masoyansa. Kuma da ya yi magana a saurare shi.

Talauci da *Wahala,* ba za su haɗu a kan mutum guda ba, sai a kan wanda ya ƙi tsarkake tunaninsa, ya ƙi kuma yin kyakkyawan amfani da duk irin baiwar da Allah (swt) Ya yi masa; ya ƙi daidaita rayuwarsa da halayyarsa. Mutum irin wannan shi

ake kira, *Matsiyaci,* komai kuɗinsa, ko sarautarsa, ko ilminsa. Haka Mai-kuɗin da shi kaɗai kuɗin ke amfana, ba shakka, yana cikin tsarin matsiyata marasa albarka. Kuɗin ne za su kai shi su baro. Ranar da ya rasa su ya shiga uku. Ba mai yi masa jaje, balle taya shi addu'a.

Kamar yadda *kuɗi* da *arziki* suka bambanta, haka *Tsiya* da *Talauci.* Idan muka yi nazari sosai, sai mu ga dukkaninsu yanayin zuciya ne ga mai su. Yadda ake samun matsiyacin Mai-kuɗi, haka kuma ake samun Talaka Mai-arziki. Bambancin kowanne a yanayin zuci yake; kuma shi suke fassarawa a zahirin Halinsu da kuma Halayyarsu. Zuciyar Mai arziki fara ce cike da alhairi da bushahar wadatar zuci. Amma zuciyar Matsiyaci, baƙa ce, cike da muni da ƙuntatar zuci. Duk wanda ya bincika yanayin zuciyarsa, to kuwa zai iya sanin ko shi Mai arziki ne (komai rashin kuɗinsa), ko kuma shi Matsiyaci ne (komai kuɗinsa). Duk abinda ka tarar shi ne haƙiƙanin gaskiyar kamanninka. Sai dai ka hilaci kanka, amma ka san hilatar kanka kake yi. A nan kuma ka sake zama shashasha, domin ba za ka canja ba. Ka cuci kanka da kanka.

Lallai mu lura cewar: ba wanda Allah (swt) Ya halitta Matsiyaci. Haka ba wanda Ya halitta Mai-



kudi. Da kudi da tsiya duk masifun duniya ne, ba su da nasaba ko kadan da jin dadi, halin kirki, arziki ko imani. Siffar zuciya da tunanin mutum na ainihi a suturce su ke cikin ni'imar wadata, kwanciyar hankali da cikakken imani. Akwai wanda zai iya sarrafa talaucinsa wajen kyautata rayuwarsa. Akwai kuma wanda zai iya sarrafa kudinsa wajen watsa rayuwarsa. Mai kudin da ya sarrafa kudinsa wajen kyautata rayuwarsa da ta wasu shi ne Mai-Arziki, kamar dai Talakan da ya sarrafa rayuwarsa wajen kyautata rayuwar wasu har da tasa. Dukkaninsu mutane ne masu farin tunani. Daga kokarinsu na farantawa jama'a, wasu mutanen kirki suke samun nasu farin cikin da wadatar zucin.

Dokokin halittar mutum a tsarin biyayya ga duk umarnin Allah (swt) suke. Mun san wannan shi ne: *Deen-al-Fitra,* watau: *'hukumcin asali'*, wanda a tsarinsa, duk gaɓoɓi da jikin kowacce halitta umarnin Allah (swt) kawai suke bi. Watau, ba halittar da take da ikon ainihi a kan kanta. Idan idonka ya mutu, ba za ka iya ce masa ya buɗe ba. Idan Rai ta zo fita, ba za ka hanata ba. Idan kafarka ta gurgunce, ba za ka ce mata miƙe ba. Idan gashin kanka ya fara zagwanyewa, ba za ka ce masa daina ba. Idan tsufa ya doso, ba za ka ce masa dakata ba. Duk umarnin Allah (swt) suke bi ba naka ba.

Zuciyarka kaɗai kake da ikon sarrafawa, kamar yadda na ce a can baya: ita ma a tunani kaɗai, amma ba a rayuwarta ba. Akwai darasi babba a nan ga masu tunani da zurfin nazari.

Watau, ashe duk jikinka musulmi ne, kodayake ka iya zama kafiri ta wajen tunaninka. Kafirci kuwa salo-salo ne. Ka iya kafircewa kanka ta wajen cire suturar da aka haifeka da ita, idan ka zaɓi yin mummunan tunani da aikata shi. Ko ka rufawa kanka asirin da aka halicceka da shi ta wajen kyakkyawan tunani da adance shi, yadda za ka ci gaba da kasancewa yadda kake tun asali.

Ɗan-Adam ba zai iya fita daga wahala ta hanyar tsiwa da zamba ba, balle kuma ta cuta ko sata ko hassada. Amma idan ya yi ƙoƙari ya shiga neman rufin asirin kansa, to, ba shakka, zai iya sabunta kansa ya koma cikin halittarsa ta ainihi.

Daga lokacin da ya fara tsarkake zuciyarsa, sai ka ga ya fara daina zargar wasu da cewar sune suka jawo masa wahalarsa. Sai ka ga ya fara jingine nadamarsa da sadudarsa cikin halayyar wahalar da tunaninsa ya nannaɗa masa. In kuma macucin wasu ne, sai ya fahimci zalunci ba maslaharsa ba ne. Ko menene munin halayensa; ko mecece



masifar halayyarsa, mutum zai iya sake tunani ya canja su. Wanda ya yi wannan, nan take zai farka ya fara gina kansa izuwa mutum mai imani, adali mai mutumci kuma ƙwaƙƙwara a tunaninsa da halayensa. Nan take zai fara amfani da *Halayyarsa* wajen bincikar kansa da ci-gaba da gyara kansa. Nan take zai zama mutumin kansa, mai ƙoƙarin inganta kansa. Mai farin tunani gameda rayuwarsa da halayyarsa. Ba abinda ba zai iya ba na alhairi, in ya sa kansa wajen yinsu; kuma cikin lokaci ya ga sakamakon alhairin.

Doka, ba ruɗami ba, ita take tafiyar da komai a Sararin da Allah (swt) Ya halitta. Haka Adalci, ba Zalunci ba, shi ne ruhin rayuwa. Aikata daidai, ba Mugunta da Ha'inci ba, shi ne yake haifarda dangantaka ta-gari, ya kuma samar da mutum a cikin al'umma tabbatacciya. Ashe kuwa tilas ne mutum ya gyara kansa in har yana son ya haɗe da tsarkakakken sararin da Allah (swt) Ya halitta, domin wannan shi ne mataki na farko a cimma inganta. Tareda Allah ba Wahala, ba Talauci, balle Tsiya. Ba Ha'inci, ba Mugunta, balle Zalunci. Yawancin wahalu sharrukan ƙullin zuci ne. Zuciya mai tsarki ba ta jinsu balle ganinsu.

Saboda haka, wanda tunaninsa ya kauce kyawawan

alamun Allah (swt) shi ne ya fita daga tsarin rayuwa mai wadata, ya shiga rayuwa mai wahala. Amma duk wanda ya gyara kansa ta hanyar kyautata tunaninsa gameda kansa, da jama'a, da sauran abubuwa, to zai ga cewar su ma jama'ar da sauran abubuwan sun gyara tunaninsu da al'amuransu gameda shi. An ce; *"Alhairi danko ne, ba ya faduwa kasa banza"*. To, ka yi wa kanka alhairi, ka fita daga tunanin nadama don ka rasa wani abu; ka tashi tsaye wajen gyara al'amarinka kafin wahala ta ci karfin tunaninka, ko kafin tunaninka ya dulmiye cikin wahala. Wannan ita ce gaskiya wadda ta kan gagari musu, ga mai nazari da tunani, wanda kuma ya san muhimmancin kansa yake kishin kansa.

Muhimmin darasi a nan shi ne, mu san yadda za mu fassara wahala da yadda ta shafemu. Idan ka gina wadatar zuci ta hanyar tunaninka, to ko kai Gyartai ne, rayuwarka mai ni'ima ce. Sai ka ga kana alfahari da sana'arka, kana yin abubuwan da za su ingantata, har sai ka kai matsayin da wasu za su yi mamaki. In kai direban wani ne, wataran kai ma sai an tuka ka. In kai Lebura ne, wataran sai ka dau wasu wannan aikin, ko da a matsayin Helman ne. In kai mawakin kauye ne, wata ran sai an sayi fayafayenka a birni. In kai yaron makanike ne, ko



na mai-kanti, wataran sai ka yi shagon kanka. In kai talaka ne a lungu, to nemi wata sana'a da za ka iya yi, ko mai ƙanƙantarta ka kuma himmatu a kanta, ko da ta faskare ce, ko sayar da ciyawa. Wataran sai ka yi mamaki, muddin dai ba ka wulakantata, ka watsar da ita ba. Duk mai sana'a komai ƙasƙantarta, ya fi mara sana'a komai faɗin ransa. Amma in ka shagala cikin nadama, to ka shigarda kanka cikin wahala mara magani. Muddin dai ka daure ka canja tunaninka cikin nagarta, ka kuma fassara rayuwarka da jin daɗinka yadda suka dace da kai, ka kuma godewa Allah (swt) sauran baiwoyin da Ya yi maka, ka kuma yi yunƙurin amfani da su, to, ko badaɗe ko bajima, duniya za ta tallafa maka da yardar Mai Iko da ita. Kada ka fidda ran fita daga halayyar ƙunci izuwa ta wadata, musammam ma a zuciyarka. Lallai ka tashi tsaye kan sana'arka, ka kuma dogara da Allah wajen nasararka. Mara sana'a shi ya yi hasara.

Amma duk wanda ya ɗau al'adar auna rayuwarsa da ta wasu, ya shiga ƙangin wahala. Wanda ya tsaida matsayinsa a gefen na wasu, ba don ya koya ko ya inganta kansa ba, ya shiga dabaibayin rayuwa. Wanda ya rena kansa da ƙwazonsa da mutumcinsa da isarsa, don ba shi da abin duniya, to ya fijircewa hanyar arzurta matsayinsa. Wanda ya

bar kansa cikin tunanin wahala ya shigarda kansa kurkukun rayuwa. Wanda yaƙi nema, ko koyon sana'ar yi, shi ya cuci kansa, kuma shi ne wahallale, wulaƙantacce. Wanda ya ce bara ko roƙo sune sana'arsa, to haka zai kasance a wulaƙance. Kaicon wanda kuma ya ce saɓon Allah ne sana'arsa ko sana'arta. Ba hasarrare irin wannan. Mai ƙwazon fafutuka da imani da rashin girman kai, shi ke cin riba. Shi ke iya maganin wahala. Kuma, gwada ka gani.


Da dukiya da muƙami, ba sune kaɗai ma'aunan ɗan-Adam ba, sai dai a al'ummar banza. Halin mutum da ɗawainiyarsa a kan al'amuran jama'a a ƙauyensu ko a lungunsu, da ƙoƙarin inganta kansa, sune manyan ma'aunai a al'umma ta-gari. Duk al'umar da ba ta sha'awar mai gaskiya, don ba shi da abin bayarwa; ba ta ƙaunar mai aiki tuƙuru don canja matsayinsa; ba ta son taimakon mai ƙoƙari, sai malalci; ba ta tafawa gwani sai masu ganganci da rayuwarsu, ko ma macutansu; ba ta sha'awar masu mutumci sai marasa kunya; ba ta tausayin abin tausayi sai ƙyashin masu ƙoƙari; to wannan al'umma ta shiga uku ta lalace. Kaiconta! Ba ta da shugabanni na-gari. A irin wannan al'umma ba wanda ya isa ya faɗa a ji shi, ballantana a bi umarninsa. A irin wannan al'umma talauci yake




kanta, ka ga kowa da komai sai lalacewa suke yi.

A al'uma ta-gari, wadda ta san abinda take yi, da abinda ya dameta, ba a ganin mutum da kandiri, nan da nan a ce Liman ne. Ba a ganin Liman nan da nan a ce na Allah ne. Ba a ganin mai kuɗi a ce mai arziki ne. Ba a ganin mutum nan da nan a bi shi. Ba a ganin talaka a ƙyame shi. Ba a ganin marar lafiya a guje shi. Haka ba a ganin sarki nan take a faɗi a gaishe shi. Dukkaninsu, sai an auna halayensu da daɓiunsu tukuna, an kuma fahimci abinda ya dace a yi masu. Ba duk mai rawani yake sarki ba. Ba kuma duk mai-sarauta yake mulki ba. Ba duk talaka ne matsiyaci ba. Ba kuma duk mai riƙe da carbi ne na Allah, ko yake wuridi ba. A wannan tsari kuma, ba duk abinda mutum ya ce wahala ne, ya ke kasancewa wahalarba. Ko gajiyayye, in ya yi tsaf, zai iya sarrafa gajiyawar, ba ta hanyar bara ba, ya inganta rayuwarsa, ya kuma samarwa kansa wani jin daɗi da alfahari daidai shi. Bincika a hankali ka kuma yi nazari, saboda Allah.

Masu zaton suna cikin wahala, lallai ne su san cewar ba duk wahala ce take kanta har abada ba, sai in ba a tunkareta da tunani nagartacce da kuma jarumta da dauriya da fafutuka da sadaukarwa ba.





4



Halí da Halayya

"Hali nagari Halayyar ni'ima

Mutane sukan zaci za su iya ɓoye tunaninsu, amma a zahiri ba za su iya ba, domin waɗannan TUNANI su ke jirkita su zama HALI; kuma halin, shi yake haifarda HALAYYAR mutum.

Misali: Susutaccen tunani, shi ke jirkitar da Halin mutum ya zama sususu har sai Halayyarsa ta zama tamkar ta dabba. A wannan halayya, haka sauran jama'a za su ɗau mutum tamkar dabbar har sai ya canja halinsa ta hanyar canja tunaninsa.



Mutumin da bai tace tunaninsa kafin ya ambaci ra'ayinsa ba, yakan iya faɗar shirme, kuma jama'a su ɗauke shi mashirmaci, har sai ya gyara maganarsa ta hanyar tace tunaninsa. Halayyar da ya sa kansa ciki sai ta ba shi sigar wawa, ko gaɓo, ko ma marar hankali ga waɗanda basu san shi ba, har sai ya gyara maganarsa ta hanyar gyara tunaninsa. Amma ga waɗanda suka san shi, sai mamaki ya kama su tareda tunanin, 'Me ya sami wane ne?'

** Haka tunanin **Tsoro**, ko na **Shakku**, ko na **Fargaba**, suke sa mutum ya zama matsoraci, ko mara tsaida shawara, ko mara ƙarfin hali. Su kuma ke sa a gama da shi, ko a raina shi, ko a yi watsi da shi. Duk waɗannan suke sa mutum ya yi biris da abubuwan da za su iya maishe shi cikakken mutum, su saka shi cikin halayyar lalacewa da dogaro a kan wasu. Duk Azzalumi Matsoraci ne.

** Tunanin **Lalaci,** shi ke sa mutum ya zama malalaci, wanda ke jefa shi cikin halayyar ƙazamta, rashin aiki, bara, riƙo, har ma da rashin gaskiya, koma sata. Malalaci ba ya newarsa kansa alhairin rayuwa. Sai ka ga mutum yana ta lalacewa.

** Tunanin **Kiyayya** da na la'antar wasu, suke sa mutum ya zama mai halin ƙeta, yawan zagi da

yawan faɗa. Waɗannan illoli su kuma ke jefa shi cikin halayyar watsewa da rashin masoya.

** Tunanin **Son-kai,** shi ke sa halin mutum ya zama mai-ƙwaɗayi, marowaci, mara tausayi ko na mahandami. Wannan hali shi ke jefa mutum cikin halayyar rashin mutumci.

** Tunanin **Hassada,** shi ke sa mutum cikin halin baƙin ciki, annamimanci, ƙulle-ƙullen sharri, fushi da jafa'i. Wannan hali shi ke jefa mutum cikin halayyar tsiya, talauci da rashin madafa ko makoma. A kullum a cikin baƙin-ciki da damuwa yake, saboda hassadarsa ta rufe hukuncin Allah.

** Amma, mutumin da tunaninsa na alheri ne, toh, ba shakka shi ne mai kyakkyawan hali, wanda zai haskaka halayyarsa. Wannan halayya mai haske da ni'ima, ita ce za ta maishe shi mutum mai ƙwazo, hikima, dauriya da son jama'a; kyauta, kwanciyar rai da wadatar-zuci -har ma da tsoron Allah. Wannan mutum shi ne mai kulliyar arziki, mai cikakken rufin asirin duniya da na lahira.

** Mutumin da ba ruwansa da neman hana-wani, ba haɗama, ba nufaƙa, ba yawan ƙarya ko yawan rantsuwa, ba ganin ƙyashi, ba sharri balle ƙulli a



zuciyarsa. Wannan mutum shi ne mai cikakken imani; shi ne wanda ya yi daidai ya kuma dace da Sararin da Allah (swt) Ya halitta cikin tsarki da ni'ima. Tunani irin wannan shi ne ke sa halin nagarta, wadda yake mai da mutum mai ƙwazo da kwanciyar hankali a ɗaukacin rayuwarsa. Albarkarsa kuma ta bi har zuri'arsa. Irin wannan mutum, ba shakka shi ne abin sha'awa da koyi.

** Tunanin **Jarunta** kuma, shi ke haifarda ƙarfin hali, ya sa halayyar mutum ta zama ta fafutuka da dogaro da kansa, tareda jin wata iska mai huro 'yanci. Wannan mutum shi ne kaɗai zai iya yin gwagwarmaya da fafutukar da za su kawo ɗinbun alhairi tareda shi. Mutane jarumai suke iya shugabanci da mulki cikin adalci domin tuni sun kau da mutanen banza daga gefensu, waɗanda za su ingiza su hanyar zalunci da kama-karya don su kare matsayinsu ta wajen lahanta jama'a. Adalci ba shi ga rago ko matsoraci.

** Tunanin **Jin-ƙarfin Jiki,** shi ne ke kawo halin tsabta da son aiki; waɗanda su kuma suke sa mutum ya zama lafiyayye, sannan kuma halayyarsa ta zama ta alfahari da gamsuwa da kai.

** Tunanin **Kirkin-zuci** yake haifarda halin kirki,

da mutuntaka da haƙuri. Mutum mai tunani irin wannan, shi yake cikin halayyar soyayya da zaman lafiya. Shi ne wanda zai tsinci dukkanin alhairansa a duniya da kuma lahira.

Tunanin aikata **Gaskiya, shi ke sa mutum ya zama mai gaskiya da riƙon amana, waɗanda ke haifarda halayyar kwarjini, farin-jini da kuma shugabanci, ko da a cikin abokai ne. Mutane irin waɗannan sune abin dogoro, abin bi. Idan suka yi magana ko suka faɗi ra'ayi, lallai ne sauran jama'a su saurara, don sun san ba wasa ko annamimanci a cikin maganarsu. Ku dubi dai Muhammad (saw), da sauran annabawa a misali. Da maƙaryata ne da ba a bi su ba. Da ba inda Islam za shi.

** Tunanin **Sanin Yakamata**, shi ne yake sa mutum ya zama kimtsattse mai ɗa'a, waɗanda su kuma suke haifarda halayyar zaman lafiya da zumunci da kowa, tallafar juna da gina iyali ko al'umma a kan tafarki mai kyau. Mai irin wannan tunani shi ne maciyin nasara a kowanne hali.

Duk irin tunanin da mutum ya maƙalewa, mai kyau ko mai muni, ba zai kasa haifarda sakamakonsa a cikin Hali da Halayyar mutumin ba. Halayen mutane da yawa, su ne jumullar halayen al'umma; kuma yadda sakamakon halin



mutum zai tadda shi, haka sakamakon halin al'umma zai tararda ita.

Idan kowa ya gyara Gidansa, to Unguwa ta gyaru. Idan Unguwanni suka gyaru, to Gari ya gyaru. Idan Garuruwa suka gyaru, to Kasa ta gyaru. Wannan abu haka yake a kan kowacce matsala. Daga ingancin Mai-gida da 'ya'yansa, sai Kasa gaba ɗaya ta inganta. Idan daga cikin kowanne gida, ko a cikin kowanne iyali aka sami Mai-Arziki guda ɗaya, to Kasa ta arzurta.

Don haka, kada mutum ya ga kamar halinsa shi kaɗai yake shafa. Kada mutum ya yi zaton shi kaɗai ba zai iya yin komai ba. Haka, kada al'umma ta ɗauka cewar talauci da ƙuntata, ko arziki da yalwa, na wasu ƙalilan ne a cikinta ba nata ne gaba ɗaya ba. Kada 'yan unguwa su ɗauka cewar abinda ya shafi maƙwabci bai shafesu ba. A ƙididdigar halayyar jama'a, ko Hausawa ma suka ce: "wake ɗaya ɓata gari". Ashe kishiyar haka ma gaskiya ce. Mai kyau ɗaya sai ya haskaka munana da yawa. Duk halayen mutum sa iya shafar wasu.

Kodayake mutum ba zai iya zaɓar halayyarsa tawwali ba, amma zai iya zaɓar irin tunaninsa tawwali, har sai halayyarsa ta wanzu daga halin da

wannan tunanin ya haifar. Wato daga TUNANI akan je ga HALI; daga Hali kuma ake ƙaddama cikin HALAYYA. Haka za ka taho zuwa ga Halayyarka; kuma ta wannan hanya, za ka koma izuwa tunaninka.

Mutum ya daina ƙazamin tunaninsa, na-da-nan ya ga duniya ta ƙarbe shi cikin gaggawa da hannayen taimako. Mutum ya daina hassada, yanzu ya ga arziki ya doso shi. Mutum ya daina tunanin cuta da lalaci in yana son jikinsa da lafiya. Mutum ya buɗe zuciyarsa ga tunanin alheri, in yana son ya kori sharri, ɗaiɗaicewa da kunya. Mutum ya zama jarumi, yanzu ya ga an ba shi hanya. Mutum ya zama mai tsabta, yanzu ya ga soyayya. Duk abinda ka zaɓa, shi za ka tarar; komai ya rage naka.

Duniya ita ce filin rawarka. Idan ka zaɓi kiɗanka daidai, sai rawarka ta ƙayatar: ka ji dadi, a kuma yi maka tafi.



5



Tunani da Lafiya

"Jiki baran Zuciya"

Ba shakka, duk wanda ya san, ya kuma yarda cewar, ***"Jiki baran Zuciya ne"***, to kuwa, zai iya danganta tunaninsa da lafiyarsa, kamar yadda yake danganta tunaninsa da Halayyarsa. Idan mutum ya yi tunanin kirki, sai jikinsa ya bazu da ƙyallin yarunta da lafiya. Idan mutun ya ƙulla tunanin sharri, sai jikinsa ya yanƙwane cikin cuta da ruɓunta. Kamar yadda tsiya takan zama halayyar mutum mai tunanin hassada, haka lafiya da cuta duk halayya ne dake da tushensu daga tunani da halayen mutum.



Tsoron mutuwa da yawan tarradinta, sukan gayyoto saurin tsufa, ko su ƙarasa marar lafiya nan da nan, kamar yadda ƙarfin zuci yake riƙe samartaka, ya kuma warkarda marar lafiya cikin gaggawa. Wani, sai mu ji an ce, 'Ayya! ai ya karaya'; wani kuma mu ji an ce: 'Kai! wane da karfin hali yake; har yanzu yana nan'. Mutanen da suka fi tsoron cuta, sun fi saurin kamuwa da ita domin tunanin tsoronta tuni ya tsiraice jikin ya kuma buɗe ƙofofin da cutar za ta shige shi. Masu aiki da marasa lafiya a asibiti, da masu jiyyar marasa lafiya, misali, ba su kamuwa da cutar majiyatan, in ba ta ganganci ko haɗari ba, domin ba sa tsoronta, kuma ba ta cikin tunaninsu. Tunaninsu na alhairi da tausayi da son taimakawa, sune suke kare su daga ɗaukar cutar.

Yayin da mutum yake yin mummunan tunani, jikinsa yakan canja, jininsa kuma ya gurɓata, saboda irin umarnin da suke samu daga zuciyarsa mummuna ne. Amma idan umarnin zuci ga jiki mai kyau ne, to, haka ba shakka, jikin da kuma jinin zasu kasance. Zuciyar da ta zama juji, haka jiki zai ruɓe. Zuciyar da ta zama lambu, haka jikin zai yi ni'ima. Watau, tunani shi ne famfon rayuwa:

Kwanto Ruwa garai-garai ka ga lafiya.
Kwanto kwatami ka ga cuta.

Canjin abinci ba zai canja lafiya ba, in har tunani bai canja ba. Sai mutum ya yi tunanin lafiyar tukuna, sannan zai iya cin abincin da zai dace da jikinsa. Tunanin tsabta shi ke sa a yi wanka a gyara jiki. Waliyin da ba ya wanka, ba waliyi bane, ƙazami ne kawai. An ce: *Tsabta, na daga bin Allah.* Matsabtaci tuni ya sha maganin yawancin cutaka. Babban darasinmu har zuwa nan shi ne: Idan kana son gyara lafiyarka, toh, kare zuciyarka. Idan kana son ka sabunta jikinka, toh, adance zuciyarka ta hanyar tunani tsabtatacce, wanda ba zai muzguna maka ko wasu ba. Ba sharri ga lafiya irin baƙaƙen tunani.

Tunanin hassada, ganin-ƙyashi, rashin mutunci da fushi, sukan kwaɓewa jiki lafiyarsa da martabarsa, a wannan lokacin da bayansa. Turɓunanniyar fuska ba haka kawai ake ganinta ba; tana zuwa ne daga turɓunanniyar zuciya. Hausawa ma sukan ce, *"Labarin zuciya a tambayi fuska".*

Haka kuma, mutumin da yake a turɓune a zuci yake da saurin tsufa; amma mutumin da yake a haskake a zuci yake riƙe samartakarsa har zuwa lokaci mai tsawo. Sai ka ga yaro ya tsufa nan-da-nan, amma ka ga mai shekaru da yawa da fuskar samari. Haka tunanin tsufa, ko yalwata al'adun



tsofaffi, ko son girma, ko yawan karɓarsa; yawan taƙama da sa Alkyabba, sukan fyade saurayi, nan da nan ka ga ya tsofe. Dubi samari da suke karɓar sarauta ka gani. Kamar dai yadda yawan sunkoyo, ko tafiya a sunkuye suke sa doro, ko da a kafaɗar yaro ce. Waɗansu daga al'adunsu suke kamuwa da cuta, ko kamanninsu su canja. Idan mutum bai damu kansa ba, ba zai ajiye mummunan tunani a zuciyarsa ba. Mutumin da bai ɗauki buri matsananci ba, ba zai ga tsananta ba. Irin waɗannan mutane suke cin ribar rayuwarsu, su kuma kiwaci lafiyarsu da jikinsu ta hanyar kyawawan tunaninsu. Duk inda ka gansu sai ka yi sha'awarsu saboda haibarsu, wadda ta tsiro tun daga zuciyarsu har zuwa fuskarsu.

Yadda Iska da hasken Rana ba za su shigo ɗakin da aka ƙulle tagogi da ƙofofinsa ba, haka farin-ciki da kwanciyar hankali ba za su shiga zuciyar da aka rufe ba. Rufaffar zuciya kuwa, ba ta jin shawara, ba ta kuma karɓar alhairi. Yadda ta zama mara lafiya cike da mummunan tunani da kaba'i, haka Halayya ke ƙara mata rashin lafiya, har sai tunanin ya canja izuwa mai haske sannan za ta sami wasila.

A fuskokin tsofaffi mun ga gurayen fata da suka samu don yawan murmushi; mun ga kuma

waɗanda suka samu don yawan turɓune fuskar. Ga mutanen da suka yi rayuwar alheri, ta mutunci da wadatar zuci, tsufa girbi ne, ko kuma sakamako ne na alherin da suka shuka cike gamsuwa da kyakkyawan zato. Su ne masu godiyar Allah (swt), tamkar Rana ta taso Gabas ta faɗi Yamma don cika umarni.

Amma ga waɗanda suka yi rayuwar banza, tsufa horo ne na sharrin da suka aikata cike da nadama da tararradi, tamkar ɓarawon da aka kama. Wanda ya tsufa cikin mutumci, zai mutu cikin haiba da lafiyar zuci, ko da tsufan ya taɓa lafiyar jikinsa a idanuwanmu. Wanda ya tsufa cikin nadama, zai mutu cikinta, ko da jikinsa garau yake a idanuwanmu. Wanda ya cimma lafiyar zuci da kwanciyar hankali, shi ya cimma lafiyar jiki da rayuwa abar misali. Kamanninka na ƙarshe sune kamanninka har abada a idanuwan mutane.

Ba likita irin tunani, don shi ne zai wanke duk wata cuta ta jiki. Ba wani abu mai kwantar da hankali da ya fi kyaun hali wanda zai iya watsarda duhun takaici da baƙin-ciki. Rayuwa cikin ƙazamin tunanin hassada, mugunta da ƙazafi, rayuwa ce wadda ta fi kurkuku ƙuntata. Amma fatan alhairi ga kowa, yawan murmushi tun daga



zuci, taimakon maƙwabci da zuciya ɗaya, zatawa kowa alhairi saboda Allah, suna daga imani, kuma sune matattakalun shiga Aljanna tun daga duniya. A Aljanna kuwa, ba a cuta, ba a kuma rayuwar nadama. Mara lafiya, amma mai halayen kirki, ya fi saurin warkewa, domin zatonsa a kansa mai kyau ne. Wannan shi zai ƙarfafa jikin ya karɓi maganin.

Idan ka ga mutum yana yawan fushi babu dalili, ko ka ga mutum yana saurin tsufa babu dalili; to binciki hassadarsa ko burinsa, ko al'adunsa. Da yawan fushi da saurin tsufa cutuka ne na zuci, kuma azabarsu tafi ta ciwon ƙaba. Gushewar imani tana ga mai ciwon zuci; irinsu ne ke kashe kansu da sun kai maƙura; ko ciwon zuciyar ya kashesu.

Zuciyar da ba imani a cikinta, ita ce zuciyar nadama, tarradi da fargaba, wadda da take angaza jiki ga lalacewa cikin cutar da ba a san kanta ba; ta kuma angazasu ga ɗaukar rayukansu. Ashe tunda kyaun zuciya shi ne yake haifar da farin tunani, shi kuma ya haifar da lafiyar jiki, ba wahalar danganta imani da wadatar zuci da kuma lafiya. Mai imani shi ke da madogara a kodayaushe.

Bala'i da hassadar mahassada; jidali da ƙiyayyar maƙiya; takaici cikin sharrin masharrata, duk haɗe-

haɗe ne da za su iya ƙuntata zuciyar mai fama da su, su aza masa cutanni. Imani da kyaun zuciya ne kaɗai za su iya kawo masa caffa ya sami lafiya da kwanciyar hankali. Mai imani, shi ne wanda ya dogara da Allah (swt), yake kuma neman tsari daga gareShi kaɗai. Mai neman tsari fi-sabilillah zai samu domin zuciyarsa a tsabtace take. Ba ya sharri, ba ya mai da martani ga mai sharri. Allah (swt) Ne madogarar Mai imani. Haƙiƙa, duk Mai imani ya sami madogara tabbatacciya.

Mahassadan da maƙiyan da masharratan sune za su gaji bala'in da jidalin da kuma takaicin da suka shuka, ko suna so ko ba sa so. Shaiɗan da baƙaƙen tunani sune abokan hidimarsu, kuma a cikin zurfin nadama da galabaita za su dawwama. Wannan halayya kuma ta haifar masu da ciwon zuci. Shi kuma ya halakasu. Takaici a kan takaici! Wannan ko shakku babu.

Mai imani shi ya ci ribar lafiya domin ma'aunin tunaninsa ingantacce ne. Mara imani shi ya yi hasarar lafiya, domin kuwa mun san ma'aunin tunaninsa gurɓatacce ne.



6



Tunani da Manufa

"Juji Rami ne kawai
har sai an zuba masa shara".
"Gona daji ce kawai
har sai an dasa mata shuka".

Zuciyar ɗan-Adam tamkar Miya ce wadda za a iya yi mata shirin musammam don ta yi gardi; ko kuma a barta ta yi tsami, amma dai za a sami miya ta kowanne hali. Yadda mai dafa miyar za ta gyara miyarta, ta sa kayan ƙanshi da sauransu, ta kuma dafata a tsabtace don ta yi gardi da kyaun gani a ido, haka mutum yakamata ya yi wajen kyautata miyar zuciyarsa.



Yadda Manomi zai gyara gonarsa, ya kauda ƙayoyi da ciyayin banza, ya kuma zuba mata taki mai kyau don ta tsiradda ni'imominta, haka mutum yakamata ya kyautata gonar zuciyarsa, ya kauda tunanin banza don ya ci amfanin rayuwarsa. Ta yin hakane kaɗai mutum zai iya sanin shi ne mai ikon gyara da adana zuciyarsa, watau tunaninsa, duk sa'inda yake so; shi ne kuma mai gudanar da rayuwarsa yadda ta dace da shi a kowanne hali. Ba wanda zai iya shiga ya yi wa mutum wannan gyara, sai shi kansa. Wa ya fi shi ƙaunar kansa? Wa ya fika ƙaunar kanka?

Kamar yadda Mai miya ta gyara miyarta, ko Mai gonar ya gyara gonarsa don cimma biyan bukatunsu (gardin miya da albarkar gona), haka ya zama wajibi kowanne tunani ya maƙalu da hujja ko bukata, in dai ana son samun sakamako mai ma'ana da martaba. Tunani ba tabbatacciyar manufa tamkar yawon mahaukaci ne, sai inda iskoki suka kai shi. Haka, tunani ba sanannar manufa, tamkar shiga kwale-kwale ne ba sandar tuƙi, sai inda igiyar ruwa ta fizgeka. Tunanin da ba shi da manufa, daidai yake da aikin da ba shi da sakamako. Tunanin da ba shi da ma'ana, hanyar su ɗaya da hauka. Haka manufar da ba ta da ma'ana daidai take da jifan shaho. Haka, manufar da ba ta ma'aunin iyaka da lokaci, shirme ce kawai.

Duk waɗanda ba su da manufa mai ma'ana a rayuwarsu, su ne cikin haɗari, tsoro, ciwon zuciya da rashin madafa, ko ma makoma. Waɗannan lahanoni alamu ne na kasalar zuciya, waɗanda sukan jefa mutum ga ƙarkon banza, rayuwar baƙin -ciki, da-nasani, takaici da wulaƙanci.

Maci ribar rayuwa, shi ne wanda ya ƙudiri wata manufa daidai shi, ya kuma yunƙura wajen fafutukar cimmata, sane da mahimmancinta da ma'anarta a gareshi. Lallai duk mai manufa, ya kimtsa mata gurbi cikin tunaninsa, ko da ta burin tsabtace zuciya ne, ko kuma ta neman wani ado na rayuwa. Ko ta mecece, lallai ya yi saitin ƙarfin tunaninsa a kan cimmata, kada ya bar nutsuwar tunaninsa ya bauɗe cikin kokwanto, wasi-wasi, shakkun-kai da sauran irin waɗannan raunanan tunani. Tsananta tunani a kan cimma buri shi ne shishshiken fafutuka. Ko da ba a sami biyan bukata bayan gwaji biyu ko uku ba, to ribar da aka samu ta fafufutukar -ilmi da sanin jama'a da kuma dakewar zucin- su ma nasarori ne; kuma su ne ababan alfahari, makaman tunkarar gaba da ƙarfin-zuci don samun cikakkiyar nasara. Kamar yadda ake cewa: '*Alheri danƙo ne, ba ya faɗuwa ƙasa banza'*, to haka ita ma fafutuka wadda ƙarfin tunani da ƙwazo ya gabatar, ba ta kasancewa a

banza. Duk sa'inda ka sake shiryawa sai ka ɗauka.

Mutanen da ba za su iya jure tararradin tunkarar muhimmiyar manufa ba, to yakamata su maishe da tunaninsu wajen alfahari da gaskiyarsu, iya aiki da riƙon amanarsu, ko menene ƙasƙancin matsayin rayuwarsu. Duk wanda ya ƙudiri buri mai ma'ana saboda Allah, ya kuma yi fafutukarsa saboda Allah (watau, da zuciya ɗaya mai ƙarfi), toh ba shi da hasara ko kaɗan. An ce, *"wani hanin baiwa ne"*, toh ba shakka a sannu mai fafutuka irin wannan zai fahimci dalilin rashin nasararsa a yadda ya zaceta, ya kuma gamsu; sannan a sannu zai ga sabuwar nasararsa a yadda ta kamace shi ta hanyoyi dabam dabam, ya kuma gamsu; in dai shi mai nazari ne.

Lallai mu fara sani da yardar cewa, ba dukkaninmu ne za mu iya zama Gwamnoni ko Ministoci, ko Sarakuna ko Masu-kuɗi ko Shaihunnan Malamai, ko auren waɗanda muka fi so ba. Amma dukkaninmu ma iya kwatanta alfaharinmu a cikin 'yan abubuwan da za mu iya zama, ko samu. A yawancin lokatai, za mu iya tararda gamsuwar rayuwa ta aikata abubuwan da suka kamata, tamkar mun taka tsanin burinmu. Ta irin wannan tunani ne kaɗai, da rashin raina-kai, wasunmu za su iya tattara hankulansu, su kuma gyara tunaninsu don

fuskantar gaba, sannu da sannu, da kuma ƙwazo da alfahari fiye da da. Ma'ana, kada mutum ya sake ya bar tunaninsa cikin matsayin ƙasƙanci da rashin ƙaƙa-na-ka-yi. Ko da zuciyar da ta fi kowacce rauni, muddin dai ta fahimci cewar, *ƙarfin zuci zai iya ginuwa a hankali,* kuma ta yunƙura wajen yin haka, cikin juriya da haƙuri, toh, a hankali-a-hankali ba shakka, Allah Zai tallafa har sai ta sami ƙarfinta, ta kuma cimma burinta daidai ita.

Kamar dai mai karaya ne da aka ɗora. A sannu-da-sannu zai fara yunƙurawa, yana tattakawa har sai ya miƙe da ƙwazonsa. Haka kuma zai ci gaba da ɗingisawa, yana tattakewa har sai ƙafar ta samu sosai. In ya yar da sandarsa ya kwanta, sai ƙafar ta ruɓe. Haka burin da aka watsar yake watsewa. An ce: *"Da rashin-gwaji (ko tayi) a kan bar araha."* Kuma, masu hikimar magana sun ce *"Kashi 80 na nasara zuwa gurin ne kawai"*. Gwada ka gani.

Duk wanda ya watsar da rashin alƙibla, lalaci da ragwanci; ya fara yin tunani da manufa mai tsabta, toh ya shiga sahun jaruman da suka san cewar, *Wata gazawar a yau, matattakala ce ta cimma buri a gaba. A*she kuwa wani hanin mabuɗar ilmi ce a gareka, domin ka yi la'akari da kura-kuren da suka kawo maka cikas, ka sake ɗamara don gaba;



muddin dai ka yi tunani kuma ka amince manufarka ta alheri ce, kuma daidai kai. Komai ya faru a ƙarshen fafutukarka, ka tuna cewar:

Nasara tana ga mutanen da suka sarrafa halayyarsu don ta amfanesu; suke yin ƙwararan tunani don tsarinsu; suke gwaji ba tsoro; kuma suke tunkarar manufofinsu cikin hikima da kyakkyawan zato.

Daga lokacin da mutum ya ƙudiri manufarsa, to sai ya tsara tunaninsa a miƙe don cimmata, ba duban dama balle hagu, sai dai don kawai ya kauda ƙayoyin hanya. Lallai mutum ya girgije shakku da tsoro domin sune suke gurɓata turbar nasara, suke jawo hasara. Kwazon aikata abu, fure ne na sanin za a iya aikatawa. Shakku da tsoro da jin rashin-isa su ne maƙiyan wannan ilmi. Duk wanda bai yaƙe su ba, toh kuwa za su gama da shi a kowanne mataki. Amma wanda ya gama da su, ya gama da gazawa, yá kuma doshi fuskar nasara.

Tunanin da ya abokanci manufa ba tareda tsoro ba, ya zama barden buri. Haka, duk wanda ya san wannan, toh a shirye yake ya inganta matsayinsa, domin yá mallaki ƙwaƙwalwarsa, yá kuma laƙanci tasawirar da za ta kai shi ga rayuwa mai kyau da ma'ana.

Ashe za mu iya cewar kusan, ko ma duk, abinda mutum ya iya samu a rayuwarsa, sakamako ne na irin bukatunsa da tunaninsa a kansu, wanda Allah (swt) Ya duba Ya bayar da abin ta hanyar auna buri, fafutuka da amsa addu'a. Haka yawancin hasara, ko rashin nasara, suna daga nauyin da mutum ya tilasta ɗaukarwa kansa, illa kaɗai waɗanda aka san ƙaddara ne. Karfin halin mutum da lalacinsa; tsarkinsa da gurɓatarsa, duk nasa ne, ba na wani ba, kuma shi ke jawowa kansa su da kansa, kuma shi ne kaɗai zai iya canjasu ba wani ba. In abubuwa suka yi tsamari, Halayyarsa tasa ce, ba ta wani ba. Haka nadarmarsa tasa ce ba ta wani ba; haka bushasharsa. Yadda yake tunani, haka yake; yadda kuma ya ci-gaba da tunani, haka zai kasance. Wasu na kusa da shi, sai su ɗanɗana zaƙin nasararsa, ko su ɗanɗana ɗacin hasararsa.

Mai ƙarfin hali ba zai iya taimakon rago, razananne ba, sai ragon ya zama a shirye ya karɓi taimakon. Kuma duk da haka, shi ne (ragon) kaɗai zai iya maishe da kansa mai ƙarfin hali ta hanyar ƙoƙarin kansa da tsirarwa kansa irin ƙarfin halin da ya yi sha'awa na wasu. Wanda yake zaton bai isa ya samu ba; ko bai isa ya zama ba, toh, ya dubi waɗansu ya auna yaya aka yi su suka isa? Ya aka yi suka samu? Ya aka yi suka zama? Menene



bambancinsa da su? Da irin wannan ma'auni ne kaɗai mutum zai iya auna kansa sosai don ya tabbatarwa kansa wanene shi, mai kuma zai iya yi ko samu ko zama? Da ya samo amsoshinsa daidai, toh daga nan komai zai zama a fayyace a gareshi.

Daga nan zai san cewar shi ne kaɗai zai iya canja al'amarinsa, ya kuma ciyarda kansa gaba daidai gwargwadon ƙarfinsa da kuma damar da yake da ita. Amma 'Dama' aba ce wadda sai an nemeta ko an ƙirƙirota. Idan ba ka je gurin da ake yin abu ba, ba za ka sami damar yinsa ba. Idan ba ka je gurin da ake bayarwa ba, ba za ka karɓa ba. Wanda ya zauna bai tashi ba, ba inda zashi. Wanda bai nema ba, ba zai samu ba. Akwai azancin Larabawa da ke cewa, "*Mai nema yana tareda samu*". Ashe dama tuni mun san sai ka nema zaka samu.

Wasu sukan ce: '*Jamaa sukan sha wahala ne domin wani na wahalarda su'.* Ko kuma: *'Mutane bayi ne domin wani ya bautarda su'. Saboda* haka: '*a tsani mai wahalarda sun; a tsani mai bautarda sun'.* Amma kuma, za mu iya duba waɗannan ta ɗaya gefen: *"Wani na wahalarda jama'a don sun yarda su wahalallu ne'.* Ko kuma: *"Wani na bautarda jama'a don sun yarda su bayi ne'. Saboda* haka: '*a tsani wahalallun; a tsani bayin".*

Hikimar wannan batu ita ce ta nuna yadda wasu suka zubarda damarsu da ‘yancinsu, yadda ba za su iya inganta matsayinsu ba. Hasarar, ba shakka, tasu ce su ma, ba kaɗai ta wanda suke zaton ya dannesu ya hanasu sakat ba ce. Ba wanda Allah (swt) Ya halitta banza, sai dai mutum ya maishe da kansa banza. Duk rashin kuɗinka ko galihunka, za ka iya gina mutumcinka ta yin fafutuka daidai kai, ka kuma ci nasara daidai kai. A ƙalla ka kasance cikin masu neman na kansu, komai ƙanƙantarsa. Ta haka sai mutumcinka ya tsira, kai ma ka zama cikin masu alfahari wadanda suka yi ƙwazon cetar kansu da kansu. *Gaba kuma ta fi baya yawa.*

Ko da a gasar ciniki ko matsayi, ko zaɓe; wanda ya bari aka cuce shi da gangan yana gani bai yi wani abu a kai ba, to ba shakka ya cuci kansa. Haka a gasar rayuwa gaba ɗayanta. Wanda ya zauna ya ce, “haka Allah Ya yi shi”, ya gama ƙulle kansa daga ƙudirin manufa da fafutukar da za su ‘yantarda shi daga ƙangin rayuwarsa. Wannan mutum ya yi hasara mai yawan gaske.

Da macucin da ya yi cuta don ba yadda za a yi da shi. Da wanda aka cuta yana gani bai taɓuka don kare kansa ko hana ta nan gaba ba, dukkaninsu kansu suke cuta. Da masu mulkin zalunci, sata,



dankwafe jama'a da rashin kunya; da kuma jama'ar da suka sadudar da kansu ga waɗannan azzalumai, alhali suna da yadda za su yi, dukanninsu hasararru ne; sai mu tsane su. Dukkaninsu junansu suke cuta; sai mu tsane su. Tunani mai zurfi zai nuna mana wofancin wanda ake cuta, da kuma izgilancin mai cutarwar; sakacin wanda ake cuta, da kuma rashin mutumcin mai cutar. Dukkaninsu suna bukatar canja matsayinsu da tunaninsu ta yadda za su amfani halayyarsu. Wanda ya kau da lalaci, da tsoro da kwaɗayi, ya fita daga matsayin mai cutuwa. Haka wanda ya kau da son-rai, kwaɗayi da rashin kirki, ya fita daga sahun macuta.

Mutum ba zai iya inganta kansa ba, sai ya tashi ya yi fafutuka ya inganta tunaninsa. Zai iya ci gaba da kasancewa cikin talauci da muzanci idan ya ƙi inganta tunaninsa, kuma ya ƙi ɗaukar damarsa. Sai dai kuma shi *Inganci*, ba ya samuwa ba tareda an sadaukar ba. Mutumin da ya nemi inganta kansa, amma ba ya son ya sadaukar da wasu abubuwa, nasara za ta kasance mai nisa daga gareshi. Wanda ya kasa hana kansa don ribar gaba, ba zai iya gudanarda abubuwan da yakamata ya yi waɗanda za su kai shi ga ingancin ba.


Dokokin halitta, ba sa taimakon mai son-kai, ko

mara-gaskiya, ko kuma mamugunci; kodayake wasu loton sai ka ga kamar ba haka bane saboda tsarin abubuwan da ba sa canjawa. Amma, ba shakka, masu gaskiya, rikon amana, alhairi da kwazo, har abada ba sa taɓewa. Rike addini da son Allah (swt), su ne makasudin rayuwar alhairi da buri nagari. Duk wanda ya rayu cikin yanayin zuci mai kyau, ya kuma mai da hankalinsa ga abubuwan kirki, toh kuwa zai iya cimma inganci mayalwaci. Ranarsa ta yi koli; watansa ya haskaka; hankalinsa ya kwanta; imaninsa ya karfafa; matsayinsa ya girmama da albarka.

Samun biyan bukata kowacce iri ce, sakamako ne na fafutuka, wadda ita kuma huda ce ta tunani. Ta hanyar iya sarrafar da kai, kwazo, gaskiya da kuma kyakkyawan nufi da manufa, mutum yake inganta kansa. Haka, ta hanyar shashanci, lalaci, kwaɗayi, rashin gaskiya, da sauran gurɓatattun tunani, matsayin mutum yake kaskanta.

Duk wanda yake son cimma kaɗan, toh, ya sadaukar da kaɗan. Wanda yake son cimma da yawa, toh, ya sadaukar da yawa. Wanda yake son ya rike mutumcinsa da girmansa, toh, ya adanasu; ya kuma ba wa wasu nasu. Kada ka dankwafar da kanka, domin duniya ba azzalumar kowa ba ce.

Tsara manufarka daidai kai,
Yi saitin tunaninka da fafutukarka a kanta,
Gwada ka gani.
Ba ka san inda rabo yake ba.
Sake Gwadawa ka gani.
Ba ka san inda rabo yake ba!



7



Wahalu da Masifu

"Allah ba azzalumin kowa bane"

Sau da yawa, masu ilmin Falsafa sukan fada mana cewar: *'Wahalunmu ba wahalu bane a hakika. Tunaninmu ne yake hidimar saka su a zuciyoyinmu, har sai wahalun sun sami gurbi a cikin halayyar rayuwarmu'.* Daga nan kuma sai mu shiga nadamar rayuwa har wasu su kai makurar da ba dawowa. Watau, *wahala*, saka ce ta zuci.

Kodayake mun dan tabo shigen wannan magana a gurare a baya, amma mun san, ba shakka, magana ce mai nauyin gaske da kuma wuyar fahimta. Ya za

a yi a fassarawa matalauci ko kuma mai fama da cuta ma'anar halayyarsu ta yadda ba za su ga wahalunsu ba, ba kuma za su yi zargi a kansu ba?

Wannan magana yanzu ta sa ya zama tilas mu ƙara zurfafa tunani, mu yi bincike mai zurfi a kan: 'Wai shin, mecece masifa da wahalarta? 'Me' (ko 'wa') ke jawo ta? Ya za mu yi da ita?' Haka kuma, shin za mu iya binciken, 'Me ya sa take samun wasu ta bar wasu?' Akwai waɗanda kawai su 'yan-gatan duniya ne komai nasu lafiya lau; amma kuma wasu wahalallunta, abubuwansu a watse? Ya tsarin halittun wahala da bala'i suke? Wai ma shin, me zai hana kowa da kowa su zama daidai, ba wanda ya fi wani. Shin, Allah (swt) ne Yake aiko da masifun da za su shigarda mutum ko jama'a cikin wahalu -daga gare Shi kai tsaye zuwa ga waɗanda suka sama- ko kuwa? Duk waɗannan tambayoyi daidai ne a yi su domin a fahimci wasu abubuwa iya gwargwado da hankali.

Duk da waɗannan tambayoyi masu nauyi, mun san cewar a duniyar zahiri yawancin abubuwa dama can masu ɗaure kai ne, duk da ɗimbun imaninmu. Amma, idan lallai muna son mu ƙarfafa imaninmu ga Allah, kuma saboda Allah, to kuwa lallai ne mu yi waɗannan tambayoyi, mu kuma kori tsoron



amsasu, cikin la'akari da cewar, *'Allah ba azzalumin kowa bane',* kodayake ba shakka, Shi ne Mai Iko a kan komai da kowa ɗin.

Mun san, a tsarin dangantakar mutum da mutum, wasu munanan abubuwa ba takaicin waɗanda suka sama kaɗai bane. Misali: idan jarin babban ɗan-Kasuwa ya karye, yawancin 'yan-kasuwansa sukan shiga matsala wadda za ta iya haifarda wahala, in ba a tunkari al'amarin da hikima da gaggawa ba. Shi kam tuni ya shiga. Haka mutuwar mai-gida. Haka mun san wasu masifun sukan wanzarda kokwanto ga zuciyoyin jama'a gameda adalcin duniya, musammam ma idan suka sami mutanen kirki, ko yara, ko waɗanda a tunaninmu bai kamata su samesu ba. Misalin ka ga mutumin kirki, watau mutum mai amana, bin Allah, tausayi, ƙoƙari da ƙwazo, kyauta da sauƙin-kai, haka kawai (ko a iya saninmu, haka kawai) wani bala'i ya aukar masa, nan take ya zama abin tausayi. Irin wannan takan sa wasu su tambayi kansu: *'ko zama mutumin kirki yana da fa'ida in har har abu kaza zai iya samun irin su wane Allah Na gani Bai kare masa ba?'.*

'Saboda me munanan abubuwa za su sami mutanen kirki, ko waɗanda ba su ci ba, ba su sha ba?' Wannan tambaya ba ta gushewa a tareda mu

kullum muka dubi abinda muke kira, ‘zaluncin’ duniya. Wasu sukan yi zaton cewar wasu ne suke jawowa wasu bala’i, kamar yadda ɗa ke jawowa ubansa zagi, ko yadda ganganci ke jawo haɗari. A wasu halayen, wannan haka yake, amma kuma mun san, da so samu ne, watau dá duniya ba ta da aibu a idanunmu, dá a zahirin lamari, bai kyautu wani ya wahala ko ya shiga masifa don matsala ko laifin wani ko gangancin wasu ba. Dá abubuwa, ko ita kanta halitta, ba yadda muka sansu suke ba, dá “wanda bai ji bari ba ne kaɗai zai ji woho”, don shi ne ya jawowa kansa. Dá kowa shi kaɗai zai sha wahala da masifar da shi kansa ya jawowa kansa. Toh amma, a yawancin lokatai ba haka bane.

Toh, ya kenan za mu fassara duniya idan masifar rayuwa ta sami mutumin kirki, ko al’ummar kirki? Ko kuma, rahamar rayuwa ta lullube mutumin banza, ko al’ummar banza? Don me idanun mutumin kirki suka mace? Ya aka yi mota ta faɗi da liman? Ya ɗan sarki ya shiga layin matalauta? Ya ɗan mai kuɗi ya zama matsiyaci? Ya aka yi wane mai kuɗi, wane kuma mara su? Don me wasu suka ci riba, amma wasu suka faɗi, alhali hajjarsu iri ɗaya a kasuwa ɗaya? Me ya sa cuta ta kama wane, amma ta bar wane, alhali shigen rayuwarsu ɗaya ne? Me ya sa mara imani ya yi



galaba a kan mai imani? Me ya sa aka ci zalin su wane ana gani ba a yi komai ba? Me ya sa aka kama wani, amma aka saki wani? Ko kuma…,

Me ya sa muka ga Gobara ta ƙone gidan mutumin kirki, ta halaka iyalinsa da dukiyarsa? Ya aka yi mutumin banza ya arzurta da dukiya da lafiya, komai nasa yake tafiya daidai? Ko kuwa mutumin kirki shi ne wanda duniya ta zaɓa ta yi masa sakayyar alhairi ba tareda la'akari da ayyukansa da ɗabi'unsa na banza ba; mutumin banza kuma wanda ta wulakanta, ba tareda la'akari da ayyukansa da ɗabi'unsa na kirki ba? Me ya sa wasu abubuwa suke faruwa haka tamkar babu adalci a rayuwa? Ko kuwa mu ne dai ba mu fahimci halitta da rayuwa yadda Allah (swt) Ya tsarosu ba, muke fassara abubuwa yadda son ranmu ya raya mana; ko yadda mu ke zato?

Akwai mutanen da in masifa ko wahala ta bayyana a garesu suke ɗauka cewar Allah (swt) ne Yake horonsu da azaba saboda wasu kura-kure nasu. Wannan matsala takan raunana imaninsu; kuma takan sa su kalli Allah ta hanyoyin da ba su dace da siffarSa ba, musammam idan suka lura Bai hori wasu a kan waɗannan dalilan ba sai su. Shin kuwa yakamata mu bar tunaninmu da hikimomimmu a

kan wannan kakkaifan siradi mai dimbun hadari?

Wasu kuma, saboda halayyarsu ta miskinanci ko gajiyawa, ko wata cuta, ko hasara, sukan tuhumi imanin zuciyoyinsu, sannan su shigarda kansu cikin takaici da zargi iri iri gameda wannan halayya tasu. Sakamakon duk wannan ita ce babbar nadamar rayuwa, wadda ita kuma a nata juyin take haddasa irin nata wahalun. A haka, sai a watsarda rayuwar dungum a shiga bara, ko sata, ko dai wasu dabi'u wadanda ba zasu amfanawa kowa ba, sai ma kara illoli ga al'umma gaba dayanta.

Da tsiya da talauci; da kuturta da makanta; ciwon kaba da na sukari; hadari da mutuwar masoyi; duk ababan korafi ne ga masu fama da su. Wasu kuma anazarce-nazarcensu na yadda abubuwa suke wakana a wannan duniya tamu, sukan tambayi: Me ya sa na yi hasara, amma su wane suka ci riba? Me ya sa ba a amsa addu'ata ba, amma ga wasu shagalallu can komai nasu daidai? Ga azzalumi, macuci, barawo, marar kunya marar mutumci yana ta bushasha da annashawa don jin dadin rayuwarsa cikin wadata; amma ga mai adalci, mai gaskiya, rikon amana da mutumci yana ta fankama cikin rayuwar talauci, ko cuta. Ko rashin gaskiya da rashin-kunya su ne a'ala, yin su hasara?



Wasu masu imani sun yarda cewar wahalunsu da hasarunsu jarrabawa ce daga Allah (swt), kuma sakamakonsu yana gaba, watakila a lahira. Marasa imani kuma sun ɗauka cewar dukiyarsu da jin daɗinsu alama ce babu Allah; in kuma akwai Shi, toh, Bai damu da hanyar da ka zaɓa a wajen yalwata rayuwarka ba, komai muninta.

Amma masu la'akari sun san a ƙarshe, komai yana da dalilinsa, a sarari ko a ɓoye. Kuma, Allah (swt) ba Ya ɗorawa Rai abinda ba za ta iya ɗauka ba. Haka kuma ba Ya azawa mutum masifa don ba Ya sonsa, ko don haka Yake sha'awa. Sha'awar zalunci ba taSa ba ce, domin Shi Mai ƙaunar dukkanin halittunSa ne. Haƙiƙa, babu zalunci a cikin al'amuran Allah (swt). Masu ilmi da nazari sun san Allah (swt) da *Kimiyya* Yake aiki, kuma komai naSa a tsare yake, kuma a aune da lissafi. Ilminsu da nazarinsu sun nuna masu abubuwa da yawa, waɗanda yawancinmu ba mu sani ba. Sun san ƙalubalantar duniya tana daga cikin sirrin rayuwa; kuma ita ce gishirinta. Amma sanin Allah (swt) da yadda Yake ayyukansa, ilmi ne mai wahalar fahimta ta wani gefen, mai kuma sauƙin gaske ta ɗaya gefen. Shiga cikin wannan ilmi sai an daure an faɗaɗa zuciya da haƙuri. Allah (swt) Ya yi mana jagora. Ameen. Bari na fara da wannan:

Sigar *sharri* da *alhairi* tamkar shukar irannin *Ciyawa* ce da ta *Mangwaro*. Sai ciyawar ta tsiro nan da nan ta bar mangwaron. Amma bayan ɗan lokaci, sai kuma ciyawar ta mace ta bar mangwaron. Haka misalin mutanen banza da mutanen kirki suke. Banzar ita ce ciyawar mara dogon rai; kirkin kuma shi ne bishiyar magwaron mai tsawon rayuwa har da furanni da 'ya'ya. Haka kuma dangantakar take tsakanin Karya da Gaskiya; tsakanin Zalunci da Adalci; tsakanin Kafirci da Imani. Duk mai hankali da basira ya san cewar akwai dalilai masu ƙarfin ma'ana na yadda Allah (swt) Ya tsara komai.

Bayanan masifu da auna wahalun rayuwa a sikelin azanci abune mai wuya, amma kuma tilas a yi, in har muna son bin diddigin dalilan da suka sa rayuwa take kasancewa haka ga mutane dabam dabam. Tambayar da za mu yi a yadda muka taho da zancenmu ita ce: Menene bayanin dalilan da suka sa rayuwar jama'a take bambamta, wasu tasu da muni, wasu kuma da kyau?

Bari mu yi nazari a kan waɗannan bayanai uku, mu ga ko za su iya gamsarda mu; watakila ɗayansu, ko dukkanninsu, su ne dalilan da suka sa muka zama dabam. Kafin na fara, Ina roƙon a



karanta a hankali a haƙurce cikin tunani. Kada a yi saurin rufewa ƙwaƙwalwa hikimar rairayenta: An ce: *"Mahakurci, Mawadaci"*. Saboda haka, sai a bi ni a hankali; kada a yi saurin husata da irin wannan azanci na masana abin, wanda zan yi amfani da shi don nazari da neman dalilan da suka dace da tambayoyinmu:

1.
TSARIN RAYUWAR 'YAN-ADAM TAMKAR SAKAR FAIFAI CE:

Da ka dubi faifai, ko tabarma ko darduma, za ka ga daga "*cikin*" faifan ga saƙa nan kyakkyawa gwanin sha'awa; kowanne zare, kowanne launi, ya shiga ɗayan daidai, kuma gaba ɗayansu sun haifarda tsarin saƙa da launuka masu kyau da ƙayatarwa ba kuskure. Amma juya "*bayan*" faifan ka ga hargitsi da rashin tsari. Zararruka a tsinke, ko a yanke, ko a ƙulle; wasu gajeru, wasu dogaye cikin hargitsi ba tsari balle ƙayatarwa. Duk wannan (watau, da "*ciki*" da "*bayan*" faifan), ba don wani zare yafi wani ba, a a, sai dai don haka saƙar ta haifar. To haka, idan muka dubi rayuwa da azanci irin wannan, sai mu ce haka bambamcin 'yan-Adam yake a yadda Allah (swt) Ya saƙa faifan rayuwa. Wasu baƙaƙe, wasu jajaye, wasu kuma

farare, wasu ruwan makuba. Wasu dogaye, wasu gajeru. Wasu gasu a miƙe, wasu a lanƙwashe. Wasu a ƙulle, wasu a murɗe; ga wasu can kuma a sassauce, amma wasu tamau. Wasu sun yi hagu, wasu kuma dama. Gasu nan dai, ba mai son amfani da bayan faifan saboda rashin daidaituwarsa.

Toh amma, da hankalinmu, ma iya cewa haka Allah (swt) Ya tsara rayuwar duniya: ciki da tsari, baya ruɗami? Idan "*bayan*" duniya ce, masu imani sa iya yin godiya cewa duk da halayyarsu ta yalwa ko ƙuntata, sun kasance daga tsari na saƙar Allah, wadda sakamakonsu ita ce "*cikin*" faifan, watau Lahira, inda kowa ma zai ji dadi. To amma kuma, ina adalci a wannan tsari tunda duk zararrukan sun sami ni'ima iri ɗaya a sakamakonsu, ba tareda la'akari da matsayinsu a bayan faifan ba? Watau, ibadunsu da ayyukansu masu kyau basu amfanesu ba kenan? Wasu kuma sun sami kyakkyawan sakamako a ɓagas kenan? A wannan tsari ba adalci, musammam ma ga waɗanda suka wahala a duniya komai imaninsu da kyaun halinsu.

Ko a kimiyyance mun san akwai dalilan da suke sawa a haifi wasu da lafiya wasu kuma a naƙashe; wasu kyawawa, wasu munana. A cikin rayuwar duniya kuma akwai abubuwan da suke jawo

masifu da wahalunsu ta hanyoyin da muka tauna da waɗanda za mu duba a gaba. A lahira kuma, mun san akwai Hisabi da Sakamako, kuma, ma'aunan Allah (swt) suna da yawa. Shi ya fi sanin ilahirin dalilan halayyarka, amma kai ma ka san wasu. Haƙiƙa, Allah Bai yi tsari irin saƙar faifai ba. A naSa tsarin, babu kuskure ko misƙala-zarratin. Saboda haka, wannan ba amsa ba ce.

2.
A CIKIN TSARIN ALLAH (swt) DUK HALITTA DA KISHIYARTA:

Wannan haka yake ba shakka, kuma haka ma Allah Ya ce; domin ga Dama da Hagu, ga Kyau da Muni, Mace da Namiji, Dare da Rana, Sama da Kasa, Fari da Baƙi, Gaskiya da Karya, Arziki da Talauci, Hankali da Hauka, Kyauta da Rowa, Adalci da Zalunci, Lafiya da Cuta, Tausayi da Mugunta, Ilmi da Jahilci, Imani da Kafirci, Zaƙi da Ɗaci, Haske da Duhu, Sanyi da Zafi, I da A'a, Gaba da Baya, Sama da Kasa, Rani da Damina, Dogo da Gajere, Rayuwa da Mutuwa. A lahira ga Aljanna ga Wuta.

Ga dai misalai nan birjik; idan ba ɗaya toh, ba ɗayan. Idan ba Dare toh ba Rana. Idan ba Yau, toh ba Gobe. Idan ba Arziki, yá za a san Talauci? Ko

idan ba Adali, yá za a san Azzalumi? Idan ba marowaci, yá za a san mai kyauta? Ko kuma, idan ba Rayuwa yá za a Mutu? Allah (swt) da hikima Yake! Komai da kishiyarsa, kuma duk saboda komai ya daidaita.

To amma, saboda me wasu suka zama daga tsarin munanan halittun, wasu kuma daga kyawawan halittun. Ya aka yi Almu ya zama mutumin banza, amma Alu mutumin kirki? Me yasa Ishola talauci, amma Sikitu arziki? Don me Ngozi ta kamu ta cuta, amma Jamila lafiyarta lau?

Duk waɗannan tambayoyin suna da amshoshinsu. A hankali, za mu fahimci yadda tsarin Allah (swt) da ‘yancin mutum suka zama tushen hallayarsa.

3.
MASIFUN RAYUWA
DARUSSA NE GA MASU SHANSU:

Cuta, Talauci, Hasara, Kurkuku da ire-irensu, duk darussa ne ko kuma horo ne daga Allah (swt) domin masu shansu su tsarkaku su gyara halayensu. Kamar dai yadda uba ke horon ɗansa, ba don yana ƙinsa ba, sai dai don yana son ɗan ya gyara halayensa. Ba shakka mun san duk



waɗannan baƙaƙen alamu ne masu nunin lallai a yi sabon tunani mai kyau a tsarkake hali domin halayya ta gyaru. Amma, in Allah (swt) ne Ya aiko darussa don horo, don me sai wane suka samu ba wane ba, alhali wannan ya fi wancan ƙazamta da halayen banza? Mecece makomar imaninka kenan, idan a zatonka ba ka dace da wannan darasin da horo ba, amma ga shi an aiko maka da shi?

Toh, Ya kenan? A ina za mu tsaya a wannan siradi mai wuyar tsallakewa? Shin, maƙalawa Allah (swt) ilahirin jidalanmu shi ne hankali, ko kuwa zai fi mana alhairi mu tsame Allah (swt) daga cikin samuwar masifu da bala'an da suke samunmu; amma kuma mu amince cewar Yana nan shirye Ya taimaka mana jure masu da ficewa daga garesu, in mun shige su? Toh, in ba Allah ne Yake aiko su ba, 'wa ye', ko kuma, 'menene' yake turo mana, ko sa mu, cikin wannan ƙuntatattar halayya? Ko kuwa, akwai masifu da za mu iya dangana su ga Allah, mu ce, *'Haka Allah Ya yi';* wasu mu dangana su ga kanmu, mu ce, *'mu muka jawowa kanmu';* wasu kuma mu dangana su ga wasu abubuwa dabam, mu ce, *'abu kaza ne ya jawo su'?*

Duk waɗancan Misalai guda uku, sun maƙalu ne a kan cewar Allah (swt) ne Yake aiko mana da

yawancin masifu, ba mu ke jawowa kanmu ba; ba kuma wani abu dabam ke jawo su ba. Saboda haka, ko mu yi fushi da kanmu don mun san mun dace Allah (swt) Ya aiko mana da su; ko kuma mu yi takaicin cewar Allah (swt) Ya ware mu Ya aiko mana da masifu ba tareda mun dace da su ba. Masu cewar, Allah Ya aiko mana ne don darasi a garemu, suna faɗar haka ne don imaninsu ya tilasta masu kare Adalcin Allah (swt). Sun sha'afa da cewar 'Allah ba azzalumi bane', kuma ba Ya bukatar kariyarsu. Ba abinda yake faruwa haka siddan ba dalili. Idan ba a ga dalili ba, to ba a bincika sosai ba.

Maƙalawa Allah (swt) dalilan masifunmu da wahalolinmu, ba su ne maslaha a garemu ba. Duk da imaninmu na cewar, "Allah ke iko da komai", zai fi mana alhairi idan muke nemi dalilan da suka dace da afkuwar masifun, muka kuma yi ƙoƙarin kauda su, ko gyarasu, a tsarin rayuwarmu. Idan muka ci gaba da ɗorawa Allah ba tareda nazari ba, to kuwa, kafin mu je ko'ina, imaninmu zai raunana ko ma ya salwanta, kuma ba haɗari irin wannan. Amma kuma, ɗauke Allah (swt) ɗungum daga cikin waɗannan al'amura, har-wa-yau, ya fi komai ganganci. Tsakanin waɗannan gefuna biyu, lallai mu nemi azancin da zai kawo maslahar wannan

matsala, don mu fita daga wannan tarko na imani.

Bari mu sake tambaya: Akwai dalilan da suke sa masifu faruwa, ko kuwa haka katsahan suke isowa ba tareda hannun Mai-ikon ba? Wannan ita ce magana abar dubawa. Amma, kafin ita, zai yi amfani mu duba wasu misalai tukuna, domin maiyiwuwa ne, idan muka nutsu sosai, za mu fara ganin masalaharmu a wannan sabon azancin.

*** Mai Gida ne ya kunna aci-balbal, ko kandir ya dora kan taga ko ya ajiye a cikin alkuki, inda ya saba dorawa, ba tareda ganganci ba. Can, ba zato ba tsammani, sai iska ta huro ta tunkude kandir din a kan kujera ko wani abu mai saurin kama Wuta. Kafin ka ce wannan, Gobara ta mamaye gidan; rayuka da dukiya sun salwanta.*

*** Dalibi ne ya ki karatu da nazari yadda yakamata, kuma ga Jarrabawa a gabansa. Maimakon haka, sai ya yi ta addu'ar Allah Ya sa ya ci jarrabawarsa. Ya yi ta addu'a har ranar da aka kawo sakamakonta. Da ya buda anbulan, sai ya ga ya yi muguwar faduwa!*

*** Mai cikakken imani ne a kan cewar Allah Shi ke bayar da lafiya ga marar ita. Wataran, sai ya*

kamu da Cuta. Ciwo ya yi tsanani, amma ya ki neman magani, yana ta addu'a da fatan zai warke. Amma Ina! Kafin wani lokaci sai Cuta ta bazu a jikin; Rai kuma ya yi halinsa.

*** Mutum ne mai kwazo, wanda ya tashi haikan wajen neman wata daraja, ko dukiya, ko wani ado na rayuwa. Mutumin ya yi duk abinda yakamata a kan hanyoyi karbabbu domin ya sami biyan bukatarsa, amma har yau ba ta samu ba.*

*** Mutane ne da yawa suka taru a wani muhalli don neman wata alfarma a gurin shugabansu. Alfarmar guda daya ce tak, kuma duk sun dace da ita. Da fitowar shugaban, sai kawai ya zabi mutum daya ba tareda la'akari da wani abu da aka sani ba, ya ba shi alfarmar, ya sallami sauran ba tareda bayani ba.*

*** Saurayi ne, sabon aure, mai kokari da kyakkyawan fata a gaba, wanda yake rike da nauyin duk iyalinsa. Yana cikin tukin motarsa a hankali da nutsuwa, sai katsahan tayarsa ta fashe, ya kuma rasa ransa, ko gabobinsa, a wannan hadari mummuna.*

*** Mai-Kudi ne, duk yadda za a misalta mai



kudi a garinsu. Ana nan, ana nan, sai kawai duk kudin suka kare; kadarori kuma suka bace; yanzu ga shi ya zama matalauci abin tausayi.

*** Budurwa ce mai hankali da iyaye na-gari ta shiga auratayya da wani saurayi mai sigar mutumci. Wata rana sai ya wulakantata ya saketa; ga 'ya'ya, ba kuma tareda wani laifi da aka sani ta yi masa ba.*

*** Mahajjata ne suna dawowa gida daga Hajji, sai jirginsu ya kama wuta a sama, ya fado. A wannan mugun hadarin, dukkaninsu suka rasa rayukansu.*

*** Al'ummar wani kauye ce wadda ta dogara nomarta ga wani katon kogi da ya ratsa garin. Wata damina da kogin ya kawo, sai karfin igiyarsa ya karya madatsarsa, ambaliya ta shafe kauyen, wasu suka rasa rayukansu da dukiyarsu.*

Duk wadannan misalai ababan tunani ne don warware matsalar dake cikin tambayoyinmu, kuma ba su dace a makalawa Allah (swt) dalilan faruwarsu ba, in har aka yi tunani mai zurfi. Idan har yanzu ba ka yarda cewar bala'ai da masifu za su iya faruwa da kansu ba, toh 'wa' za ka dorawa

laifin ambaliyar Ruwa da ta halaka ɗimbun jama'a? Waye da laifi idan mahaukaci ya ɗauko bindiga ya harbe jama'a a titi? Waye ya jawo faɗuwar Jirgin Saman da duk na ciki suka rasa rayukansu? Wa ya haddasa girgizar ƙasar da ta haɗiye Gari guda da yawancin jama'arsa? Wa ya fasa Dutse da aman wutarsa ya mamaye komai?

Shin, za mu iya cewa duk waɗannan masifun Allah (swt) ne Ya haddasasu don kawai sha'awarSa? Ina yaron da ya yi haɗari da mota ya mutu? Ina wanda 'yan fashi suka tare suka kashe? Ina wanda Cuta ta kama ta halakar? Ina yarinyar da mijinta ya saketa? Ina wanda ya nemi dukiya ya rasa? Ina tajirin da ya karye? Duk wa ya jawo masu waɗannan masifu? Lallai ne mu ƙididdige masifu da bala'ai da kuma wahalolin da suke samunmu, mu bambance, *"wa?"* ko, *"me?"* yake haddasa irin waɗannan; Haka, *"wa"?* ko *"me?"* yake haddasa irin waɗancan. Kuma waɗanne ne suke faruwa don kansu, ko don wasu dalilan.

***** DOKOKIN HALITTA da Allah (swt) Ya samar, su ne suke tafiyarda komai, kuma ba sa canjawa a tsarinsu na asali. Watau Allah (swt) Ya riga Ya kammala tsarinSa, Ya kuma shiriyarda komai-da-komai yadda za su tafi da yadda za su cuɗanya da



yadda za su kasance. Kuma, kodayake Ya ba wa kanSa Iko a kan komai, amma kuma ba Ya canja wasu abubuwa, kuma ba Ya hana wasu faruwa, kuma ba Ya sa wasu su faru, muddin dai tuni suna cikin injin Dokokin HalittarSa. Waɗannan dokoki, mataimaka ne a garemu, ko a jikinmu suke, ko kuma a kewaye da mu suke. Amma kuma za su iya lahantamu idan muka saɓa tsarinsu.

Misali: Mun san amfanin Dare da Rana. Don hakama sai mu yi barci da daddare, mu yi ɗawainiyar rayuwa da Rana, kamar yadda Allah Ya tsara mana. Mun san jikinmu yakan iya kare kansa daga cutanni. Don haka ma idan muka sha magani sai mu tayar da makaman da za su yaƙi cutar. Mun san yadda komai ka jefa sama, toh, ƙasa zai faɗo. Don hakama muke tsaye daram, mu da gidajenmu, mu kuma yi yawo a kan doron duniya ba tareda mun faɗi ko muna lilo a Sama ba. Mun san amfanin Ruwa. Don hakama mun san rayuwa gaba-ɗayanta ta dogara ne a kansa. Mun san muhimmancin duk waɗannan da sauransu.

Amma kuma, mun san cewar idan ka ƙurawa Rana ido, ta iya makantaka. Idan ka sha ruwa ba ƙa'ida, ya iya ƙulle cikinka. Idan abu ya faɗo kanka, ko ka faɗo daga cikinsa, ya iya halakaka. Idan ka dogara

kan jikinka kaɗai ba magani, ko ka ƙi kula da shi, ka iya kamuwa da wata cuta wadda za ta iya zama ajalinka. Mun san amfanin wasu abinci a tareda mu, amma idan ka ƙi gyarasu guba ne. Mun san amfanin Wuta, amma ta iya ƙonaka. Mun san amfanin iska, amma ta iya hureka, ko ta rushe gidanka. Duk waɗannan ba ka da iko da su, ko yadda suke aikinsu. A rayuwarka, tilas ka san yadda za ka yi mu'amulla da su, ba sune za su san yadda za su yi mu'amulla da kai ba, ko waye kai.

A wasu halayen kuma, mun san harshashi ba shi da hankalin zaɓi, idan aka harbo shi, bai damu ko waye kai ba. Idan fukafukan Jirgin Sama suka ɓalle, ko inji ya lalace a sama, in zai faɗo ba ruwansa da ko su waye a ciki. Idan annoba ta doso gari, ba ta san Liman ba, balle Sarki.

A cikin Dokokin Halitta, Allah (swt) Ya tsara komai tuni. Idan abu-kaza da abu-kaza suka gauraya, abu-kaza ne zai faru; ko abu-kaza ne zai samu. Wannan doka ba za ta canja ba har abada-abadin, kuma ko waye a gurin. Dá Dokokin Halitta sukan canja, da ba mu rayuwa ba; domin dá wataran Ruwa ba zai kashe Wuta ba; ba kuma zai yi maganin ƙishirwa ba. Dá Wuta ba za ta ƙona komai ba, balle ta dafa shi. Dá Maniyin namiji bai



maƙalu da Kwan mace an sami ciki ba, balle iyali da al'umma su ginu. Dá fatar Jikinmu ba za ta fidda gumi ba har sai ta ƙone. Dá Girgije bai zamto hadiri an yi ruwa ba, balle ƙasa ba ta fidda tsiro. Dá wataran Haske ya zama Duhu. Dá ba a sami Petur daga guɓataccen Mai ba. Dá Gaskiya ta zama Karya. Dá Zalunci ya zama Adalci. Dá wani sai ya ƙi mutuwa. Dá ba Hisabi.

Dá al'adar Allah (swt) ce Ya rinƙa miƙa Hannu a kowanne lokacin da masifa za ta faru, don Ya tsame mutanen kirki; dá mutanen kirki sun nemi ƙure Allah. Dá kuma sauran jama'a sun zubda imaninsu domin Allah Ya nuna ba ruwanSa da su, don su ba mutanen kirki bane. Dá Allah zai jingine Dokokin Halitta ga mutanen kirki, ko wasu, da ba su yi rashin lafiya ba; dá sai su ringa keta titi da gangan; dá sai su ringa dirowa daga bene, maimakon su biyo ta matattakala; dá sai su ƙi gudu in gobara ta tashi. Haka kuma dá duk makafi, kutare, guragu da marasa lafiya; ko matalauta da mahasaranta, an fassarasu da siffar mutanen banza. Dá haka Allah (swt) Ya tsara rayuwa, dá ruɗanin ya faskara. Dá yanzu ba duniyar! Allah (swt) Shi ne Mai hikima, mai iya tsarin da ya fi dacewa.

Baikamata mu ringa dangana dukkanin masifu

cewar “Haka Allah Ya yi ba”. Idan marasa lafiya suka mutu saboda rashin magani a Asibiti; idan Shugabanni suka danne haƙƙin talakawa saboda rashin imani da rashin tausayi; idan Mota ta ƙi tashi saboda rashin gyara; idan Yaro ya zagi na gaba da shi saboda rashin kunya; idan Mara kunya ya ci zabe saboda shashancin al’umma; idan Bango ya faɗi saboda rashin yaɓe; idan Madatsar Ruwa ta ɓalle saboda rashin ƙarfi da rashin gyara; idan Abinci ya ƙare saboda rashin noma; a faɗa min: Meye na Allah (swt) a cikin waɗannan? Ko kuwa so ake a maida Fadar Allah (swt) jujin zuba ƙorafi? Ko kuma muna so ne mu laɓe da Shi don mu ringa ɓoye gazawarmu? Ko kuwa har yanzu ba mu san Shi bane; labarinSa kawai muke ji?

Ba abinda yake cutar al’umma, ya kuma dakushe ci-gabanta, irin saurin cewa: *“Haka Allah Ya yi”.* Kuma ga wasu mutane da bahagon imani. Da wani wawa ya katse magana da wannan furuci, shikenan magana da shige. Ba mai sake tasota, balle wani ya ce, “Kai, wannan laifinmu ne”, balle a yi tunanin gyaran lahanin; balle a sami ci-gaba.

Idan Girgizar Kasa ta girgizo; Ambaliyar Ruwa ta kwararo; Guguwa ta nannaɗo; Gobarar Daji ta danno; Dutse mai harshen Wuta ya fashe, taɓon



wutarsa ya malalo; toh, dokokin halitta ne suke sha'aninsu, domin wasu abubuwa sun gaurayu da wasu, ko domin wani abu ya tsikaresu, a cikin tsare -tsaren halitta na fil-azan. Duk waɗannan da muke kira, "Masifun Halitta", sukan faru ne yawanci saboda Kasa a doron duniyarmu, tana ci-gaba da gyara zamanta. Ikon Allah da TausayinSa ne kaɗai za su iya kiyaye jama'a su kuma taimaka masu wajen sake gina rayuwarsu. Sanin wannan yana da ɗinbun mahimmanci ga imani.

Fari da yunwa da cutannin da suke rakosu. Muggan yanayin sanyi da na zafi da irin illolinsu. Aradu da kwarankwatsa da ɗinbun ruwan saman da yake biyo bayansu. Guguwar iska da ta teku da yadda suke farfasa komai a kan hanyarsu: Duk waɗannan masifun muhalli ne da tsarin yanayinsa. Mazauna irin waɗannan gurare da sauran 'yan Adam a doron duniya, lallai su san haka halitta take a guraren zamansu, su kuma nemi maganin lahaninta tunda wuri, ko su bar gurin. Caffar da Allah (swt) Zai kawo ce kaɗai za ta tserarda su ta kuma turo mutanen kirkin da za su tallafawa waɗanda suka tsira domin su sake gina rayuwarsu.

Amma, idan 'yan Ta'adda suka sa bom a jirgi, ko a kantuna. Idan Ɓarawo ya yi fashi, ya halaka

Maigida ko ya kwashe dukiyarsa. Idan Maƙiyi ya farma mutum ya raunana burinsa. Idan masharraci ya yi sharrinsa, wani ya shiga cikin wata masifa. Idan Matsafi ya yi makarunsa, har ya lahanta lafiyar wani abokin adawarsa: A waɗannan halaye, ba Dokokin Halitta ne suke ɓarna ba; mutanen banza ne ke yinta. Ikon Allah da kiyayewarSa ne kaɗai za su iya ceton jama'a da warkarda su, da kare su daga masu sharri da ɓarna, su kuma ba su ƙarfin hali da tunani da imanin da za su iya jure wannan rashi da hasaru da jidalan rayuwa.

Idan shugabanni suka ci amana, mutane na ganinsu ba su yi komai a kai ba; idan saboda haka Hukuma ta tsiyace, fatara kuma ta dannowa Kasa. Idan Talakawa ba su san mutumcinsu ba; idan saboda haka suke girmama waɗanda ba su dace ba, suna yabo da biyayya ga marasa kunya, suna zaɓen ɓarayunsu; idan saboda haka ba sa samun shugabanni na-gari, al'umma kuma ta lalace. Idan Azzalumai suka yi yawa a Kasa, har doka ta zama makamin kama-karya; idan saboda haka, cin-mutumcin masu mutumci ya yi yawa, wata masifar kuma ta ɓullowa ƙasar: Ku faɗa min, wa ya haddasa duk waɗannan masifu? Dokokin Halitta ne, ko kuwa mutanen Banza, ko kuma Jama'a su da kansu suka jawowa kansu saboda sakacinsu?



Amma mun san cewar, Ikon Allah da RahamarSa ga muminai, da waɗanda ba su ci ba, ba su sha ba, su ne kaɗai za su iya cetar jama'a daga waɗannan miyagu, su kuma taso da maza da matan ƙwarai waɗanda za su yi gwagwarmaya don ceto da kafa tushen ci-gaban al'ummar. Yawancin mutane suna ɗauke da kuskurarrun *"kamanni" da "alamun"* Allah (swt). Sai ka ga ana yi maSa shaidar da ta sha bambam da yadda Shi Ya misalta kanSa. Duk kyawawan Sunayen nan 99 na Allah (swt), ba mummuna guda ɗaya. Ba inda Ya ce Shi, "Mai-Cutarwa ne"; ko Shi, "Mai-Mugunta ne", ko Shi "Mai-wahalarwa ne". Lallai ne mu fara lura!

Ko ana zaton cewar Allah Ya ajiye adakun cuta da mugunta da masifu ne; sai Ya ɗau waccan ya jefawa wannan; Ya ɗau wannan Ya jefawa waccan? "Talauci! Mamaye Abubakar. Zazzabi! Kama Balaraba. Mota! kaɗe Samuwal. Hasara! Harbi jarin Gambo. Lami! Yi ɓari; Audu! Saki Jummai. Jirgi! Faɗo kowa ya mutu. Maciji! Sari Helen. Ruwan Sama! Rushen gidan Jauro. Gobara! Cinye gidan Goje. Kuturta! Ciji Musa. Makanta" Rufe idanun Bello". Haba, Jama'a! Ai yakamata mu ringa aiki da hankali da kuma ilmi. Lallai ne jama'a su sake tunani a kan waɗannan abubuwa.

Idan Dokokin Halitta, ko Mutane da Shugabannin Banza, ko kwaɗayi da fadanci, ko Jama'a su kansu, ko ɗaurowar al'amura, (kamar saran maciji, tuntuɓe, da wani bangare na haɗari), ko rashin lura da ganganci sun haddasa wani abin takaici, to lallai ne mu san ba Allah (swt) bane. Amma kuma muhimmi ne mu san cewar Yana nan a shirye Ya karemu, Ya kuma taimakemu wajen isarda sauƙi ko warwarewar duk waɗannan ababan takaici da suka same mu, in dai mun neme Shi.

Lallai mu fahimta, mu kuma amince cewar, a wajen taimako da caffa ake samun Allah (swt), ba wajen cutarwa ba. Idan muka hango wata masifa ta nufo, muka nemi taimakonSa da kariyarsa, toh ba shakka, Zai zo mana a kan waɗannan taimako. Amma fa lallai ne muma mu yi abubuwan da suka dace mu yi, ba kawai mu saduda ba.

Idan wata masifa, ko wani abin takaici, ko wahala ta sameka, to maza tsarkake tunaninka, ka yi abinda yakamata; ka kuma nemi Allah (swt) da taimakonSa. Ba shakka Zai zo maka, kuma Zai taimaka maka ta duk inda ba ka zato; in dai tunaninka da al'amuranka na alhairi ne. Allah (swt) Shi ne Mataimaki. Ba abinda Allah (swt) ba Zai iya yi ba. Ba abinda ba Shi da iko a kansa. Ba

abinda zai faru ba tareda saninSa ba. Iznin Allah (swt) a kan tabbatar komai tuni ya kammala, a lokacin da Ya idar da lissafinSa, Ya kuma tabbatar da dokokinSa. Shi Ya halicci komai da komai a aune, Shi ne kuma Mai iko a kan komai da koman.

Don hakane ma a shikashikan imaninmu, muka amince ba abinda zai faru ba tareda iznin Allah (swt) ba; da mai kyau da marar kyau. "Iznin" ba irin wanda akawu yake karɓa wajen manajansa bane, ko irin wanda uba yake yi wa ɗansa. Iznin Allah (swt) a cikin rayuwar halittunSa yake; ta yadda suke aikinsu ko tunaninsu. Watau, iznin ne injin samuwarsu da rayuwarsu da al'amuransu. Lallai mu fahimci wannan ta yadda yakamata, mu guji amfani da ma'anar "izni" yadda muke karɓarsa ko ba da shi ga junanmu, wajen maƙalawa Allah dukkanin jidalanmu. Ba shakka, Allah (swt) Ya ke iko da komai, amma akwai abubuwan da Allah ba Zai yi su ba, ko kuma ba Ya yinsu yau da kullum, domin tsarin yadda Yake tafiyarda abubuwanSa sun kammalasu tuni, tun kafin su farun.

Duk wanda Ya san Allah (swt) sosai, ta hanyar alhairi kawai ya san Shi, ba ta hanyar sharri ba. A naSa ayyukan, Shi ba Ya sharri, duk da mun san sharrin -da masu aikata shi ko kawo shi- suna cikin

tsarin izninSa. Misali: Idan mutum ya aikata sharri, mun san a cikin “iznin” Allah ya aika wannan sharri, domin Allah ne Ya halitto shi tareda duk abinda ya yi amfani da shi wajen aikata sharrin. In ta hanyar mulki ne, Allah ne Ya ba shi mulkin. Idan ambaliyar ruwa ta rushe gidaje ko ta halakar da mutane, to Allah ne Ya halicci ruwan da kuma iskar da ta huro ruwan, kuma Shi ne Ya yi lissafin cuɗanyarsu. Idan Damusa ta cinye mutum, mun san Allah ne Ya zaɓar mata nama a cikin abincin da tafi so, Ya kuma ba ta ƙarfin da za ta iya turmushe abincinta.

Amma kuma, mun san masharracin nan, shi ya zaɓi ya aikata sharrin; wanda Damusa ta cinye, shi ya je kusa da ita. Azzalumin nan shi ya zaɓi yin zalunci daga ɓangaren mulkin da Allah (swt) Ya ba shi, duk da ya san Allah (swt) Yana fushi da azzalumai. A cikin waɗanda ambaliya, ko aman wutar dutse, ko girgizar ƙasa ta halaka ko ta rushe gidajensu, ko ta lalata gonakinsu, akwai waɗanda suka jawowa kansu, domin sune suka nace da zama da noma a gindin wannan dutse wanda sun san zai iya fashewa. Akwai kuma waɗanda haka al’amarin kawai ya ɗauro, saboda kasancewarsu a wannan muhalli a wannan lokaci. Watau, tsautsayi ne, ba yadda za a yi. Waɗanda suka gina gidajensu



a kwari ko a hanyar ruwa ko a kan tsohon kududdufi, yakamata su san in ruwan ya zo ba zai saurara masu ba. Duk irin waɗannan al'amura haka suke. Tunaninmu ne kaɗai zai iya shiryarda mu domin mu yi abubuwan da za su taimaka mana kare waɗansu bala'ai. Amma ba shakka, Allah (swt) Mai jin addu'a ne, Mai kuma aiko da taimako ne duk sa'inda aka nema, kafin ko bayan masifar.

Kada mutum ya nemi Allah (swt) a ayyukansa na lalata, ko ayyukansa na sharri, ko ayyukansa na mugunta. Allah (swt) ba Zai taimaka ba. Ya riga Ya barwa Iblis wannan sararin da aƙidar. Kada mutum ya yi zaton akwai wasu haɗe haɗe da zai yi da sunan Allah (swt), ko Ayoyin littafinSa don lahanta wani abu, ko jawo wani bala'i ga wasu ko ga ƙasa. Irin waɗannan tunanin, da ayyukan da sakamakonsu duk tsafi ne. Allah (swt) ba Ya sharri, baYa yarda a yi sharri da sunanSa. Duk wanda bai san haka ba, toh bai san Allah (swt) ba. Duk wanda ya zaci cewar akwai sharri a littafin Allah (swt), ko zai iya amfani da Allah wajen ƙulla sharrinsa, to wannan mutum ya halaka, har sai ya sake tsarkake zuciyarsa, ya tuba ya dawo kan sabuwar hanya miƙaƙƙiya. Kuma Allah (swt) Mai sauraron nadamunsa da tubansa ne. Allahu Akbar! Allah da tausayi yake!

A tsarin Samaniya gaba-ɗayanta, Allah (swt) Ya kafa dokokinSa na yadda komai zai tafi. Tun asali Ya tsara kulliyar dokokin ISKA, RUWA da WUTA. Ya riga ya lissafta komai, Ya ba da umarninSa na Dokokin Halitta. A doron Duniya Ya ajiyewa duk halittunSa dokokin rayuwarsu. Waɗansu tilas jikinmu ya bi su; wasu kuma 'yancin zuciyarmu ya sa tunaninmu ya bijire shawarwarinSa garemu na yadda za mu yi rayuwa mai amfani.

Haka wannan umarni da biyayya suke ga duk halittun Samaniyoyi da Kassan da Allah (swt) Ya halitta. Ashe, babu abinda zai faru sai da yardar Allah (swt), ba kuma wanda zai iya tsaida komai, sai Shi, domin komai naSa ne. Don hakane muke cewar komai umarninSa yake bi, umarni na tun fil-azan. Deen al-Fitra. Amma mutum ya iya bijircewa a tsarin tunaninsa da ayyukansa. Ya iya ƙin gudu in Kura ta biyo shi; ya iya ƙin yin Salla in lokacinta ya yi; ya iya ƙin shan magani in ya kamu da cuta; ya iya gina gidansa a kan hanyar ruwa, ko ya kafa bukkarsa a kusa da maƙera; ko ya bi ƙungurmin daji cikin dare shi kaɗai; Ko ya sa kansa cikin yanayin da zai kamu da wata muguwar cuta. Haka mutum ya iya cutar maƙwabcinsa, ko ya yi fashi a daji ko a ofis. Duk zaɓi na gare shi, domin kuwa Allah Ya ba ba shi ikon yin zaɓin.



Da bijircewar zuciya da kafircinta suna da muhimmin bambanci. Akwai bijircewar zuciya ta ƙi bin umarnin Allah (swt) na yadda ka zaɓi ka bauta maSa, ko yadda kake fahimtarSa, ko kuma yadda za ka tafiyarda rayuwarka. Akwai kuma kafircewar zuciya, watau rufewarta ɗungum, daga imani da samuwar Allah (swt) Shi kaɗai yadda Yake. Bayanin wannan kafirci ya fita daga manufar wannan littafi, sai dai kawai mu ce zuciyar ce kaɗai take cikin wannan kafirci, ita ce kuma take dasa hali da halayyar karfircin.

Akwai misalai na bijircewar zuciya daga bin tafarkin rayuwa mafi maslaha; watau bijircewarta daga yin amfani da shawarwarin da za su haifarda rayuwa ta-gari, da kuma bijircewarta daga son biyan bukatar jiki. Idan jiki ya bukata, amma tunani ya ƙi yarda a biyawa jikin bukatarsa, to sai halayyar jiki ta taɓu. Misali: idan ka ji yunwa ko barci (bukatar jiki), amma ka ƙi cin abinci ko barcin da gangan (bijirewar tunani), to sai halayyar ciwon-Kai ta wanzu; wadda ita kuma alama ce wani gu (ko wasu gurare) a jiki sun sami naƙasa, kuma yakamata a duba. Idan ka ƙi, har kuma wannan ta jawo wata masifar dabam, toh ka ga kai ka jawowa kanka wannan illa ta jiki daga mummunan tunaninka. Haka, idan ka kamu da

wata cuta saboda ka shiga halin da za ka kamu da ita, sai ka ƙi shan magani, to in halaka ta riski inda cutar take, maiyiwuwa ne kaima ka halakan. Ka ga, mummunan tunaninka ya jawo ka rasa rayuwarka ɗungum. Wannan tsari da Allah (swt) Ya mallaka mana iko a kan tunaninmu ba ƙaramar rahama ce tareda mu ba. Amma idan muka bijirce, to mun san sakamakon a taredamu. A taƙaice: Ita kanta shiriyar addini don amfaninmu ce kaɗai, ba don amfanin Allah (swt) ba. Ya haƙiƙa!

Za mu iya bijircewa bukatar jikinmu ta hanyar munanan tunani, nan-da-nan halayyarmu ta zama ta cuta, wadda za ta iya jawo babbar naƙasa ko ma ta kawo halaka. Haka kuma, za mu iya bijircewa bukatun rayuwarmu ta hanyar munanan tunani, nan-da-nan Halinmu da Halayyarmu su raunana, waɗanda kuma za su iya kawo nadama a cikin rayuwar gaba ɗayanta.

Farin Tunani a kullum, a kan kowacce matsala, shi ne yake kusanta mutum da Allah (swt), a kuma sami taimako da tallafarSa a kodayaushe. Wannan shi ne tsarin addini da dalilinsa, domin mu ci ribar rayuwarmu. Amma kuma, *Baƙin Tunani* shi yake sa mutum ya bijircewa shawarwarin Allah (swt), ya ƙazamta zuciyarsa da tunanin Allah ne Yake

barin wulakanci da wahaloli suna shafar rayuwarmu. Mai wannan tunani, ba zai iya komawa ga Allah (swt), ya kuma yi abubuwan da suka kamata wajen sabuntawa da inganta rayuwarsa ba. Tilas ya canja tunaninsa tukuna, sannan ya sami maslahar wahalolinsa tareda taimakon Allah (swt). Idan ka ɗafawa Allah (swt) laifin wahalunka, yaushe kuma za ka je gareShi neman taimako, tunda ka ce Shi ya jawo maka?

Lallai ne daga yanzu mu san kanmu, mu kuma san dalilan da suke sa mu cikin wahalu, ko suke kawo bala'i da masifu a ƙasa da kawunanmu. Idan na Dokikin Halitta ne, to mu yi nazari, mu ga ya za mu iya fisshe da kanmu daga garesu tun kafin su zo, ko in sun zon. Idan na Miyagun mutane ne a cikinmu, mu san ya za mu yi da waɗannan mutane. Idan namu ne na kanmu, mu san ya za mu canja kanmu, mu kyautata, mu inganta rayuwarmu. Idan masu faruwa ne don haka al'amari ke ɗaurowa, mu san ya za mu kiyayesu, ko mu magantasu, ko mu jure masu, in sun farun.

Abune muhimmi ga mutum ya zama mai ƙarfin zuciya daga ƙarfin tunani. Kada wanda ya yi fafutuka sau ɗaya ko sau biyu ya barta domin bai sami nasara a gwajin farko ko na biyun ba. Kada

mutum ya fidda rai ɗungum daga samun nasara daidai shi a rayuwarsa. Kada matar da aka saki ta kama hanyar lalacewa, ko ta fidda rai daga sabuwar rayuwa, ko samun miji wanda ya fi wancan alhairi a gareta. A tsarin Allah, watakila sabuwar rayuwa ce a gabanta mai albarka da gamsuwa. Kada Mai arzikin da talauci ya riske shi, ya zubda rayuwarsa cikin jujin nadama da fitar imani. Ya tambayi kansa: 'Da, ya aka yi na samu?' Sannan ya sake maida himma da gyaran tunaninsa da halayensa da kurakurensa. Da wannan sabon tunani da aƙida Allah Zai kimsa masa wadatar-zuci, Ya kuma isar masa da sababbin bukatunsa. Kada mutum ya rufe imaninsa ga Allah. Canjin alhairi yakan biyo bayan takaici, in an barwa Allah. Don hakama ake cewa, *"Wani hanin ga Allah baiwa ne"*, kuma akwai misali da yawa.

Kada mutanen da ba su sami alfarman nan daga shugabansu, su ɗauka nan gaba ba za su samu ba, har su kama hanyar watsewa, ko ɓatawa wanda ya samu, ko zagin shugaban. Lallai ne su sake maida al'amuransu wajen Allah su kuma yi aiki tuƙuru. Kofofin Allah suna da yawan gaske. Kada iyalin saurayin da ya rasu a haɗari, ko shi, in ya tsira da ransa ba da wasu gaɓoɓinsa ba, su ɗauka shikenan ba wani sauran haske a rayuwa sai duhu. A cikin



wannan canjin halayya, Allah Ya san yadda zai yi da su ya cike masu gurbin hasarunsu, muddin dai tunaninsu da ƙwazonsu ba su raunana ba. Kada 'yan'uwan Mahajjatan nan su ɗauka cewar Allah (swt) Bai damu da ibadar 'yan'uwansu ba, kuma bai damu da su ba. Sakamakon ayyukansu na alhairi, da ibadarsu, ba za su taɓe ba. Allah ne Ya fi sanin hanyoyin alhairi da zai sakawa mamatan da kuma waɗanda suka yi rashin.

Amma lallai ne ɗalibin nan ya san ba zai taɓa cin jarrabawa ba, sai ya yi karatu a nutse. Allah (swt) ba Zai canja sakamakon jarrawabarsa ba; ba zai kankare 'Faduwa' Ya rubuta masa 'Ci' ba. Haka, duk mai Cuta ya san magani ne kawai mai warkar da ita, kuma don haka Allah (swt) Ya ba mu maganin komai, har ma a cikin wasu ayoyinSa, Ya kuma ilmantarda mu a kansu. Ka sha maganin tukuna, sannan ka yi addu'ar domin Allah (swt) Ya tallafa maganin ya warkar, ko da maganin ya naƙasa a dacewarsa da cutarka. Idan ba ka da halin sayen maganin kuma, sai ka yi addu'a Allah Ya aiko maka da yadda za ka yi ka sami maganin da ya dace da cutarka. Kada ka manta cewar wasu ayoyin Al-Kur'ani mai girma, muhimman magani ne, musammam in ba halin neman irin maganin da aka sani. Ba ta'inda Allah (swt) ba Ya tallafawa,

indai an name Shi da farin tunani na farar zuciya. Mai nema daidai, akodayaushe, yana tareda samu.

Amma, wanda ya tunkari abinda ya fi ƙarfinsa, ko ya ƙi kaucewa abinda zai illace shi da gangan, komai ya faru gareshi shi ya jawowa kansa. Duk abinda ya faru ga mutum, ko ga al'uma, ya zama tilas a yi tunani mai zurfi tukuna, a binciki dalilai sosai, sannan a nemi maganin abin, in ana da shi, ko a ƙirƙiri dabarar tunkararsa, idan ba shi da magani. Mutum da al'ummar da suka ɗau wannan Hali a ɗabi'arsu, to ba shakka su ne masu iya kange masifun da suka doso su, ko suka same su. Su ne kuma masu iya tunkarar su idan ba za su kangu ba. Allah (swt) Zai taimaka a wannan gwagwarmaya ta masu amfani da imaninsu da hankalinsu da ƙoƙarinsu. Amma waɗanda suka saduda, suke maƙalawa Allah (swt) laifin jidalan su, ba inda za su a filin dagar maganin masifunsu, balle kuma na warakarsu da ci-gabansu.

Ba jarin da ya fi muhimmanci ga ɗan-Adam irin ya fahimci Allah (swt) daidai gwargwadon yadda zai iya, domin ya san yadda Yake gudanarda ayyukanSa da HikimoninSa. Ta hakane kaɗai, mutum zai san nasa ayyukan da abinda tilas ne ya kiyaye, muddin yana son zaman lafiya da gamsuwa a rayuwarsa. Allah (swt) da Ya haliccemu, Ya fi ƙarfin ya zaluncemu. Su wa ye mu? Yaushe kuma muka isa?









Tunani da Inganci

"Araha ba ta ado"

Arayuwar mutum, akwai wata aba guda wadda take da muhimmancin gaske wajen auna matsayinsa. Wannan aba kuwa ita ce, *Nasara*. Akwai waɗanda suka ci "nasara" a rayuwarsu; akwai kuma wadanda suka yi "hasara" a rayuwarsu. Da 'nasara' da 'hasara' a yawancin lokuta, tunanin inganta kai, ko rashinsa, suke haifarda su. Wannan shi ne harsashin maganar.

Haƙiƙa, ba mutumin da ba ya son nasara a cikin duk abinda ya sa, ko ta sa, a gaba, sai dai wawa. A kodayaushe mukan ce, *"Nasara tana daga Allah"*,

kuma wannan magana gaskiya ce. Saboda haka, lokaci ya yi da yakamata mu bincika ma'anarta a nutse. Mun san cewar, ƙwazo da fafutukar mutum wajen neman nasara sukan taimaka ƙwarai da gaske wajen samun nata. Don hakama muke cewa, "*Allah (swt) Ya ce, 'Tashi In taimakeka'".* Watau, kada wanda bai taɓusa ba ya sa rai a cikin samunta, ko ya yi ƙorafin bai sameta ba. Ashe, *Allah Ya ce: Tashi In taimakeka,* gargaɗi ne, ko kuma ƙarfafa gwiwa ce, ga masu nema domin su tashi tsaye su yi fafutukar da ta dace da burinsu da manufarsu. Ita kanta "*Sa'a"* takan zo ne ga zuciyar da ta kimtsu ta karɓeta.

Akwai abubuwa na Halaye waɗanda in mutum ya yunƙura ya gina su cikin tunaninsa, toh, ba shakka, zai iya inganta rayuwarsa da Halayyarsa ta hanyar inganta Halayensa, kuma ya ji daɗin gudanarda kansa da al'amuransa a kowanne hali. Mutane da yawa sukan yi hasara a rayuwarsu, ba don komai ba, sai dai don kawai sun yi sakacin gyara, ko nuna wasu halaye waɗanda za su iya kusantarda su ga mutane, su kuma ƙara masu kwarjini, mutumci, da sauran alamun mutum masu angazo nasara a cikin hulɗa, kowacce iri ce.

Gyara Hali ta wajen gyara Tunani, zai iya fassara mutum a surar da za ta amfane shi, ta kuma ba shi



damar aikata wasu abubuwa da za su ƙara masa sa'a wajen cimma wasu buri, waɗanda in ba tareda waɗannan halayen ba, da wuya a sami sa'ar, balle kuma nasarar. Ita dai Nasara, tana da muhimmancin gaske, domin takan hure baƙin-ciki da tunanin banza; ta hana zaman banza; ta kuma kore damuwa. Duk waɗannan dangi ne na Farin Tunani, mai yalwata Farin-ciki da lafiya da basira da alfahari-da-kai, da kuma cancanta. Ba shakka, nazarin wannan Babi da shawarwarinsa zai yi fa'ida ga waɗanda suke son nasara a tareda su.

Akwai dokokoin rayuwa kamar 19, ko ma fin haka, waɗanda mutane masu son inganta kansu za su iya la'akari da amfani da su, har sai sun zama ɗabi'unsu. Na tabbata masu yalwata tunani da nazarin rayuwa za su iya ƙara wasu dokokin a kan waɗannan da na zana. A nan ga ɗabi'un da zan fara maganarsu a cikin sauƙaƙaƙƙen bayanansu, don a fara amfani da su.

1

KYAKYKYAWAR LAFIYA

Kamar yadda muka gani can baya, a Babi na 5, Tunani mai-kyau yana da babbar nasaba da lafiya mai-kyau. Ita kanta lafiyar jiki mai-kyau,

sakamako ce ta kyakkyawan tunani gameda lafiyar. Idan mutum ya ringa tunanin rashin lafiya, misali *'ciwon Kai',* sai ya ringa jin kamar ya kama shi. Tunanin bawali, yakan matsa jin bawalin; haka tunanin hasara yake kawo fargaba; tunanin tsoro kuma ya haifar da ragonci.

Tunanin fargaba da tsoro sukan ƙara saurin famfon zuciya har gudun jini a jijiyoyi ya ƙaru. Da wannan ta faru, sai jinin ya fara ɗumi, abu wanda ke haifar da 'hauhawar jini' -cuta wadda za ta iya halakarda mutum nan da nan. Ashe yaƙin fargaba ba zai yi nasara ba, sai an yaƙi tunanin hasara kowacce iri ce. Yawan tunanin hasara, yana daga ƙarancin imani, har da na gamsuwa, gaskiya da wadatar-zuci. Amma, mutumin da ya yalwata zuciyarsa da Tunani mai kyau, shi ne zai iya samun kwanciyar hankali.

Idan mutum ya yalwanta tunanin lafiya, ya kuma ringa faɗawa kansa labaranta tun daga zuciyarsa cewar, *"Ni, ba ni da wata matsananciyar Cuta",* ko, *"Ni, Jiki na lafiyayye ne akasarinsa", ko, "da yardar Allah ba zan bar wannan cuta ta gama da ni ba",* to kuwa, ya tabbata, ba shakka, saƙon da jikin zai ji kenan; kuma umarnin da zuciya za ta ba shi kenan domin ya baza makamansa na yaƙin duk



wata ‘yar ƙwarya-ƙwaryar cuta. Abin fa kamar imani ne; wanda ya yi imani da magani, toh sai farin zatonsa na alhairi, watau, farin tunaninsa, ya umarci jiki ya karɓi maganin da zuciya guda. Haka ma addu’a take. Wanda kuwa ya yi shakkun magani ko addu’a, ko ya ringa zatawa kansa cuta, to ba zai warku daga maganin cikin sauri ba, domin tunaninsa bai karɓi maganin ba, ko kuma bai amince da addu’ar ba. Cimma waraka da samun biyan bukatar lafiya cikin hanzari za su yi wuya ga mai ƙorafi ko zafafa cuta.

Hausawa sukan ce: *“Riga Kafi Ya fi Magani”.* Wannan ba ƙaramar shiriya ba ce ga mai tunani. Amma, Riga-Kafi, ba shi ne kaɗai ka sha magani kafin cutar ba; a a, ka kori ma duk wani abu wanda zai iya lahanta lafiyarka daga tsarin al’adunka. Shaye shayenka da ciye ciyenka; barcinka da makwancinka da mahutarka da wajen sana‘arka; har ma da jima’inka, lallai ne su kasance masu la’akari da lafiya. Ko juji ka ringa zubawa tarkace, to ya ƙara wari. Kada ka lahantar da jikinka da gangan, domin ba za a musanya maka shi ba.

Lallai ka kyautata jikinka. Shan Giya, Shan Taba, Shaƙar Iskar banza da shan Yaji ba ƙa’ida ganganci ne. Haka cin abincin da ba ƙa’ida, yadda

cikinka zai cika tam, ko numfashi ba ka iya yi sai da kyar. Wannan takan matsawa huhu da zuciya wajen aikinsu, ta kuma haddasa wata cutar in ba a yi hankali ba. Lallai mu ɗauki shawarar Annabi Muhammad (saw) wadda ta ce: *"Raba cikinka gida uku: Sulusi, "Abinci"; Sulusi, "Ruwa": Sulusi, "Iska".* Haka ya ba mu shawara, cikin Kimiyya ta hikimar kiwon lafiya. Kullum ka zama mai tunawa da wannan batu: *'Ci Mai-lafiya, ka yi Lafiya. Ci Cuta ka Cutu'.* Lafiyarka dukiyarka. Lafiya uwar jiki. Kai zaka kula da lafiyarka ba wani ba.

Isashshen Barci, Motsa Jiki a-kai a-kai, abubuwa ne masu muhimmanci sosai, kuma lallai ne a maida hankali a kansu. Wasu na wasa da lafiyarsu ta wajen matsantawa jikinsu da neman ƙure shi. Ko inji yakan bukaci hutu da binciken lafiya loto-loto. In ka ƙi kula da shi ya buga. To haka jikin mutum, ba shi da bambamci da injin Mota, domin an ƙerata ne daga tasawira da bukatun ɗan-Adam. Duk abinda ka gani a halittar mutum, to Mota na da shigensa. Haka yadda mota za ta buga daga gurɓataccen petur, mutum ma zai buga daga gurbataccen abinci ko abin sha. Zuciyarka, Kaburetanta. Jininka, Petur ɗinta. Jijiyoyinka, Wayoyin injinta. Tumbinka shi ne Tankinta. Rihinka kuma Hayaƙinta. Yadda ka ke son ruwa,



haka take so. Yadda take son sabis, haka ka ke bukata. Ka kula da ita, amma ka ƙi kula da kanka? Ko Babur gareka, shi ma haka yake. In ba ka da su kuma, ya fi zama wajibi ka kula da kanka da lafiyarka, domin kai ne abin hawanka.

Zuciya Jagorar Lafiya; Lafiya Uwar Jiki; Jiki Magayi. Duk waɗannan batun Hikima mataimaka ne a gareka wajen tunaninka gameda lafiyarka. Tunda kyakkyawar zuciya takan yalwata lafiya, ashe kuwa yakamata ka nutsu ka kuma tabbata cewar kana jin daɗin ayyukanka, ko cinikinka, da hidimominka ga al'umma, iyalanka da abokanka; ka kuma san kuɗi ba su ne kaɗai tushen farin-ciki ba. A gaskiya ma, yawancin lokatai su ne tushen baƙin-ciki, musamman idan ba a aikin alhairi da su. Lallai ne ka sami abokai na kirki masu ƙaunarka saboda Allah, ko da basu kaika a matsayi ba. Ka shiga ayyukan taimakon jama'a da taimakon kai-da -kai da na addini, don ka farantawa kanka, ka tabbatar cewar rayuwarka ta zama cikakkiya mai lafiya da amfani gareka da al'umma duka.

Wanda ya mayarda lafiyarsa abokiyar rayuwarsa, shi zai rayu cikin halayyar da zai iya neman nasara a al'amuransa. Wanda kuma ya yi banza da lafiyarsa, shi ne ya yi hasara. Duk wanda za ka yi

hulɗa da shi, amma ya lura ba ka da cikakkiyar lafiya, to ko bai ƙyameka ba, to kuwa lallai zai ja da baya a wannan hulɗar. Ba mai son ya ɗau kasadar ciniki ko kasuwanci da marar cikakkiyar lafiya. Haka ba wanda yake son ya ɗanka amanar al'amuransa ga wanda lafiya ta guje shi. Duk sa'inda aka lura ba ka da lafiya, to ba shakka za a fara nesa da nemanka a kan al'amuran mutane, balle kuma na shugabancinsu a kowacce harka. Ko rumfa gareka a kasuwa, ba ka da jarin da ya fi lafiyarka, domin in ba ita ka karye. Daga nan nasara ta ɓace. Duk wanda ya sake da lafiyarsa, ba shakka, ya sake da rayuwarsa. Don haka lallai ne mu himmatu ga lafiyarmu fiye da komai.

2.
KALAMI MAI KYAU:

Iya Magana da amfani da kalmomi masu ma'ana da ƙayatarwa sukan cicciɓa alfarmar mutum su kai shi sama. Haka Murya wadda ta dace da al'amarin da ake magana a kansa; kuma cikin murya miƙaƙkiya mai fidda zance taryan-taryan, ba yawan gyaran murya, ko kaki, ko shaƙar hanci, kilisar haƙora, gyatsa, balle tofarda miyau. Ko ba komai duk waɗannan ɗabi'u ne munana, waɗanda ba su dace a yawaita yinsu cikin jama'a ba.



Mutumin da ya san zai yi magana cikin jama'a, to lallai a kodayaushe ya zama cikin tunanin irin maganganunsa. Lallai ne ya yi la'akari da ma'ana da kuma tsayawa a kan abinda ake zance. Wajibi ne ka auna matsayin mutanen da ka ke magana da su da gurin da ka ke magana da su; sannan ka ba su girman da ya dace da su ta hanyar yin maganar da ta dace da su.

Idan ka cika mutane da surutu, ko dogon bayani tamkar mai magana da kidahumai, ko ka ringa magana ba ci-gaba; watau, ka yi gaba, ka dawo baya, ko kana ta susar wuya ko hammata; ko kana ta kalle kalle, ko kana kallon ƙasa ko sama, to kafin ɗan lokaci mutane za su ƙagu, watakila ma su yi fushi da kai. Kodayaushe ka ɗauka cewar mutanen da ka ke magana da su sun san abinda suke yi, ko da yara ne; ala-barshi, ka ba su damar tambayoyi a ƙarshen jawabinka. Wannan shi zai fassaraka a garesu ta hanyar reni ko girmamawa.

Yin magana cikin hikima da murya mai dacewa, kuma fitatta, a hankali, takan ƙara martaba da karɓuwar mutum da maganarsa cikin sauƙi da lumana. Wani, da iya tsara maganarsa, daɗin muryarsa da azancinsa, ya ke kafa manufofi da akidunsa. Komai gaskiyar magana da

muhimmancinta, in ba a yi ta cikin lafazin da ya dace ba, sai ta yi ɗacin da ba mai ɗanɗanata.

3.

TSABTA:

Shiriyarmu a Hausa da addini a kan wannan ita ce: *"Tsabta tana daga bin Allah".* Watau, *Ibada ce.* Sanya tufafi masu tsabta da haske, sukan fiddo da mutum cikin surarsa ta mai tsabtataccen tunani. Gujewa launuka rambatsau kamar mahaukaci, yakan fiddo da mutum a surarsa ta mai kimtsatstsen tunani. Iya ado na azanci, ba na fariya ba, yakan fiddo da mutum a surarsa ta mai ɗa'a da daidaituwa a tunaninsa. Tsabta da nunata a kowanne hali, manyan darajoji ne ga mai ita. Tsabta alama ce ta farin-ciki da godiya. Kazamta kuma alama ce ta baƙin ciki da rashin godiya.

Da ƙazami da mai rambatsa launuka, da mai jibgo ado wai sai ya fi kowa, duk mutane ne masu ƙuntatattun zucuyoyi da tunani. Idan ka danƙa shugabanci ko wani al'amari a hannunsu, to yadda suke sa kaya, haka za su tafida shugabancin ko al'amarin. Kuma, tuna wasu da ka sani ka gani.

** Kazami, shi ne wanda bai damu da kansa



ba, balle ya damu da wani. Bai damu da lafiyarsa ba, balle ya damu da ta wani. Ba abinda ya dame shi, ba kuma abinda za ka faɗa ya yi tunani mai-kyau mai-tsabta a kai, domin ƙazami ne. Bambancin Jikinsa da muhallinsa da na dabba kaɗan ne, in ma akwai.

** Mai rambatsau, ya iya zama mai tsabta, amma ta hanyar wanki kawai. Ba shi da azancin tsari da dacewa. Idan ka bar zurfafan shirye-shirye a hannunsa, to, sai ya hautsunasu, domin bai san abubuwan da suka dace da juna ba.

** Mai Cin ado don ya fi kowa, mutum ne mai son nuna isa. Idan ka ba shi dama, sai ya cinkishe kowa do son nuna ba wanda ya fi shi. Yawancin irin waɗannan mutane akan same su da girman kai, amma ba kasafai suka sani ba. Duk waɗannan mutane marasa tsabta ba su karɓuwa ga jama'a, da zarar an gane halayensu. Hasara ce babba, mutum ya kasance ƙazami a waɗannan fannoni.

Mai tsabta shi ne wanda mutane ke sha'awa, domin bayan kullum ga shi tsaf-tsaf da shi, sai kuma ka ga ya iya ado mai ma'ana da ban sha'awa, ko da kayansa masu sauƙi da araha ne. Ko da da yadin alawaiyo ko akoko ne, wasu sun san yadda za su

tsara shi su adance kansu, su kuma fi mai adon siliki, amma ranbatsau bakinsa da hammatarsa na wari. Irin wannan tsabta ko ƙazamta ta jiki da tufafi, har a zuci take, domin fassara ce ta irin tunanin mai ita. Watau, matsabtata mutane ne masu tsari, ƙawata kaɗan da hikimar shirye-shirye. Su ne ababan zaɓi, su ne kuma masu saurin samun karɓuwa da nasara a cikin mutane. Kazamai kuwa sune kishiyar waɗannan. Ko a tsarin gemunsu, zaka gane su, domin kamar na bunsuru yake.

A kimtse, a adane, za ka sami muhallin mai-tsabta, ko kantinsa, ko ofishinsa, ko motarsa, ko takalminsa, ko haƙoransa da faratansa da gashin kansa da gemunsa. Ko da ba ka san muhimmancin tsabta ba, in ka je gun mai ita, to za ka yi sha'awar komawa. Idan kai ƙazami ne, ka je tsabtataccen guri, to nan take za ka ji a jikinka cewar ka ƙasƙanta. Nan take za ka ji a jikinka cewar ba gurinka bane, ko da kuwa muhallin abokanka ne. Tsabtar jiki da muhalli da tufafi, suke sa mutum ya zama mai tsabtar kalami da ɗabi'u, ba tareda gangancin zuci ba. Irin waɗannan mutane, su ake sha'awa; su ne masu alfarma; sune suka dace da soyayya ko ma shugabancin jama'a. Su kowa yake son ya kusanta, a kowacce irin hulɗa da suka sa kansu ciki. Su ne ma'abota nasara tsabtatacciya.



4.
NUTSUWA DA DAGEWA

"Alamun cimma nasara suna daga zurfin nutsuwa". Idan Nutsuwa ta haɗu da dagewa, sukan zama matattakalun nasara a cikin al'amuran ɗan-Adam, na sana'a da siyasa da mulki da soyayya da kasuwanci da gina iyali da yawancin sauran manufofi na rayuwa. Kada a yi shakkun haka. Amma nutsuwa da dagewa ba sa samuwa idan mutum ya yarda wasu abubuwa na damuwa suka tsinka tunaninsa. Haka, tunanin wahalu a ɗarikar fafutuka, ko tunanin gazawa a gwajin farko, duka sukan gurgunta dagewar zuciya su jawo hasarar manufa. Da-na-sani da tausayin-kai, su ma illoli ne masu lahanta tunanin samun nasara, kamar dai yadda zaman banza yake dakushe ƙwaƙwalwa. Abune muhimmi mutum ya tashi ya ringa yin wani abu, a kodayaushe, ko da tunanin abinda zaka yi gobe ne, ko abinda za ka yi a wannan makon, ko a wani lokaci mai zuwa.

Dabara ce babba, mutum ya shirya tunaninsa dalla-dalla, a rubuce in da hali. Tsara buri a tunance, da dabarun cimmasu a rubuce, sukan kawo gamsuwa da sakamakon alhairi mai ban mamaki ga wanda ya yi haka. A yayin da ka ke tunani kana rubutawa, a

wannan lokacin sababbin tunani da suka fi na da za su ringa zuwan maka. Kuma gwada ka gani! Kowanne mutum zai iya cimma bukatunsa daidai ƙarfin zuciyarsa, ɗokinsa, maida hankalinsa, lissafin lokaci da hangen-nesansa.

Kada ka ringa cewa kanka, "*Ba zan iya ba",* ko *"Na kasa nutsuwa".* Waɗannan baƙaƙen tunani sune za su hanaka ci gaba, su raunana maka zuciyarka, su jawo maka hasarar manufofinka. A cikin niyyarka ta fafutuka, guji cewar, *"Abu kaza sai su wane:,* ko, *"Wane Ni".* Duk abinda ka sa kanka, bayan ka yi tunaninsa sosai, ka kuma tsara dabarunka yadda za ka iya, to fita ka yi shi sosai, da kyau ba sassautawa. *"Duniyar-nana, ba ta Rago bace",* in ji Mamman Shata.

Kai dai ka tabbata a zuciyarka cewar abinda za ka nema, ko za ka yi, ya dace da kai. Hausawa a hikimarsu, sukan tuna mana cewar, "*Da rashin tayi a kan bar araha".* Gwada ka ga ni. Jarumin da ya nutsu a kan fafutukarsa, yana tareda nasara. In tunanin shirya wani alhairi don jama'a ya zo maka, maza tashi ka shige kan gaba wajen shirya abin. Ba da daɗewa ba, za ka ji wasu na cewa, "wallahi ni ma na yi wannan tunanin." Watau, suna nuna maka cewar, ina ma su ne.

5.
MARTABA LOKACI

Duk mai cikakken hankali, to kuwa yakamata ya kasance mai martaba lokaci, domin babu abu mai muhimmanci irinsa. Duk abinda ka sani, a ƙayyade yake a lokaci, musammam ma rayuwa ita kanta. Haka idan lokacin abu ya shige, ba mai iya juyo shi ya tabbata yadda yake a lokacinsa. Ba mara kishi da rashin sanin yakamata irin wanda ya san lokacin abu, amma ya ƙi, ko ya kasa kiyaye shi. Ɗauki lokacin Salla a misali, ka yi tunanin me ya sa Allah (swt) Ya tsayar mata da lokatai tabbatattu? Mecece kuma sigarka, idan ka makara ga Sallar ba tareda ƙwaƙƙwaran dalili ba? Daga nan ma za ka san muhimmancin lokaci, yadda Allah Ya koya mana.

A tsarin cimma bukatunka, da huldodinka da jama'a, ka ɗebarwa komai lokacinsa, sai in ya zama dole ka ƙara, ko ka rage, domin dai ka san cewar, wata damar ba za ta sake dawowa ba. Kada ka ringa shirya rayuwa a hargitse ba lokaci, domin duk abinda ba lokaci a cikin tsarinsa, to shirme ne, fankama ce. Duk abinda yakamata ka yi yau, to kada ka bari sai gobe. Aikin da za ka yi da karfe huɗu, to ka yi shi da karfe huɗun. Mutumin da bai san muhimmancin lokaci ba, shi da dabba

bambamcinsu kaɗan ne. Ni, a guna ma gara ita.

Alamar mai iya rike nauyi
da sauke haƙƙi da cika alkawari,
tana daga mai iya rike lokaci.

Duk mai ɓata lokaci da yawan makara, to haka duniyar za ta tafi ta bar shi, kuma mutumcinsa ya zube, mutanen kirki su watsarda shi a kan bai san alkawari ba, domin kuwa bai san muhimmancin lokaci ba. Lokaci shi ne ma'aunin rayuwa. Wanda ya ɓata shi ya ɓata rayuwa, ko tasa, ko ta wasu. Idan ka yarda aka ɓata maka shi da gangan, ka cuci kanka. Idan ka ɓatawa wasu shi da gangan, ka cuce su. Shugaban da ya makara, ba shakka bai san haƙƙin jama'arsa ba, domin ya renasu. Wannan shugaba ya naƙasa. Ko harkar kasuwanci, ko ta wani abu muhimmi, zaka shiga da wani, ya zo a makare ba dalili ƙwaƙƙwara, to, in ka kauce masa ka kaucewa hasara da nadama a gaba. Haka, ɗalibin da ya makara a makaranta, bai kama hanyar gina rayuwarsa ba, balle kuma wanda ya ƙi zuwa sam sam.

Rashin sanin muhimmancin lokaci yana cikin dalilan rashin ci-gaban wasunmu, har da Kasarmu. Ma'ana watau, rashin sanin muhimmancin lokaci shi ne ginshiƙi a cikin rashin cin nasararin



rayuwarmu da ta al'ummarmu a wasu fannonin. Ga wasu bicanni, makara har ta zama ado. Alla-wadai da wannan mummunar ɗabi'a. Bin lokaci, kamar tsabta, yana daga ibada. To haka lokaci yake. Wanda ya san lokaci, shi ne nutsatstse wanda zai iya tsara rayuwarsa, ya kuma cimma burinsa a lokatan da suka dace. Shi ne wanda ya cancanci riƙe amana da shugabanci, don ya san hakkin jama'a; kuma zai yi masu ayyukansu a lokutan da suka dace dasu. Wanda bai san muhimmancin lokaci ba, shugabancinsa ko wakilcinsa ko hulɗa da shi, kowacce iri ce, duk hasara ne. Manzon Allah ya ce, "Ba na murna da mai ɓata lokaci". (Buhari, Muslimu da Abu Dawud)

6.
TUNAWAR KWAKWALWA

Iya tuna abubuwa yakan ƙara samuwar nasara; yakan ciyarda komai gaba; yakan bunƙasa ilmi, farin-jini da kuma bajinta a wajen magana. Sannan kuma yakan ƙarfafa yadda aka amince da mutum. Amma, mantuwa da sakaci, sharruka ne masu samarda duk kishiyoyin waɗancan kyawawan sigogi; su jawo jin-kunya, nadama da hasara, har a ringa cewa mutum sususu ne, ko ba shi da tabbas. Irin waɗannan la'anta, ba shakka, sukan dakushe siga da nasara.

Duk abinda mutum ya ji, ko ya gani, a cikin ƙwaƙwalwarsa ake ajiyesu nan take. Shiga cikin kwanyar, da buɗe shafin abin, shi ake kira, *"Tunawa".* Ka shiga, ka kasa buɗe shafin, shi ake kira, "*Mantuwa".* Waɗannan abubuwa suna da tsironsu ne a zuci, watau a tunanin mutum.

Ka daina faɗawa kanka cewar, *"Ai ni mutum ne Mai-Mantuwa";* ko yawan cewa, *"wallahi na manta".* Mai irin wannan hali yana fallasa kansa ne ta waɗannan batu. Yawan faɗar, ko tunanin wannan takan sa kwanyar mutum ta dakushe, ta ƙara lalacewa wajen buɗo shafin abubuwan da ake son tunanwa. A kullum ka shiga gado don barci, ko ka tashi da safe, zai taimaka maka idan ka ringa tunanin cewar kwanyarka ta fi ɗazu, ko ta fi jiya iya tuno da abubuwa. A halaye irin waɗannan, ka rinƙa ƙoƙarin tuno da duk abinda ka *yi*, ko ka *ji,* a yau ko jiya. Lallai ne ka fara gaskanta kanka da ƙwaƙwalwarka. Kada ka ce komai sai ka rubuta sannan za ka tuna.

Idan ka yi niyyar yin wani abu, maza ayyana kanka kana yi. Wannan dabara za ta iya sa abin ya fi zaunuwa a kwanyarka ka kuma tuna abindazarar lokacin yinsa ya zo. Idan kana son ka tashi da karfe biyar na asuba, faɗawa kanka, cewar, *"Zan*



tashi karfe biyar", kamar sau uku kafin ka kwanta, kuma ka ayyana kanka kana tashin. To ba shakka, a sannu-da-sannu, za ka iya saitin kwanyarka ta kaɗa maka ƙararrawa da ƙarfe biyar. Za ka yi mamakin koyawa kanka tunawa da abubuwa ta wajen ayyanasu. Idan ka saba da yin ibada a kan lokaci, alal misali, da lokacin ya yi, za ka ji kwanyarka tana kaɗa maka ƙararrawar lokacin ibadar. Waɗanda suka tsaida Sallah a kan lokaci, ko wata ɗabi'a a lokaci tsayaiye, sun san haka.

Idan kana da wata lacca da za ka ba yar, to ka gwadata kai kaɗai a ɗaki, tamkar jama'ar na gabanka. Haka kuma, ka yi tambayoyin da ka ke zaton za a tambayeka -komai ɗacinsu- kuma ka ba yar da amsoshinsu da misalai da ƙididdiga da isharorin da suka dace. Za ka yi mamakin yadda yin haka zai taimaka maka wajen ƙayatarda mutane a lokacin da ka ke yin maganar a gabansu.

A ƙarshe, kada ka ringa cewa, *"Zan yi ƙoƙari in tuna"* ko, "*Ina fatan zan tuna".* Ka ce kawai: "*Zan Tuna".* Ta wannan ƙwaƙƙwaran tunani cike da niyya tabbatacciya ne kaɗai za ka iya sarrafa ƙwaƙwalwarka yadda kake so. Tamkar mai son hadda ne. Tuna tasawirar shafin da salon rubutun, makamai ne a filin hadda. Idan aka sanka da riƙe

abubuwa, watau rashin mantuwa, take za a yarda da al'amuranka, a kuma ba ka dama wadda ta dace. Idan an san ba za ka manta ba, to kuwa ba za a yi maka wasa ba, ba kuma za a gujeka ba.

Amma idan aka sanka da mantuwa, to ka gama yawo. Ba wanda zai ɗora rayuwarsa da sauran al'amuransa a hannunka, don mantawa za ka yi.

7.
SANIN ABINDA DUNIYA KE CIKI

Sigar mutum da karɓuwarsa ga jama'a, ko kuma nasa iya zaman da jama'a, suna da dangantaka da irin abubuwan da ya sani da kuma waɗanda ya shiga cikinsu a wasu gurare dabam, ba ƙauyensu, ko unguwarsu, ko garinsu kaɗai ba.

Mukan haɗu da mutane da yawa, waɗanda kidahumancinsu da jahilcinsu a kan yadda sauran ƙasarsu ko duniya take ciki, sukan ɓata al'amuransu, su maishesu baya a ma'auninmu. Rashin sanin abinda duniya take ciki, yakan dakushe ilmi, ya ƙulle maka damar fahimtar wasu abubuwa da za su iya taimakonka da sana'arka. Idan ka tafi haka sai ka yi ta fankama cikin

jahilcin rayuwa da abubuwan da suke da muhimmanci a gareka. Ko kai Malami ne, ko ɗan-Kasuwa ne; ko kai Mai-Mulki ne, ko Ma'aikaci ne; zurfin fahimtar yadda duniya take ciki abune muhimmi ƙwarai da gaske. Misali:

** Malami wanda yake ƙoƙarin bayanin wata Aya, ko wani Tarihi a kan mulukiyar Rum, amma fa bai ma san inda Rum ɗin take a tasawiyar duniya ba, bai kuma san abinda take ciki a da ko yanzu ba. Ba shakka, bayaninsa ba zai ƙayatar ba, domin shi kansa bai san abinda yake zance a kai ba. Amma Malamin da ya san wani abu dangane da inda take da abinda ya faru ko yake kuma faruwa cikinta a tarihi da kuma a yau, zai iya yin bayani yadda masu sauraronsa za su ƙayatu, har ma ya iya kwatanta lokatan Ayar da lokatan wannan zamani, ya fidda tafsiri tabbatacce. Rum ta Turai kenan.

To ɗauki Ayoyin Kimiyya, ko na Mulki, ko wata matsala dabam. Kamar dai Malamin da yake son bayanin wata Aya, ko muhawara a kan, *"Nunƙayar Duniyoyi a Sararin Samaniya",* amma ko kaɗan bai karanci, ko saurari wani abu daga fannonin wannan Ilmi ba. To ba yadda za a yi ya yi bayani a kan abinda bai sani ba. Wasu suna son su nuna *Sani,* amma ko abinda ke faruwa a garinsu ba su sani ba.

Daga son burga, sai su zama masu kuskure da jin kunya a maganarsu; ko ma su ƙara ɓatarda wasu.

** Ɗan-Kasuwar da ya san Japan, ko China da tarihinsu da al'adunsu, da yadda abubuwa suke tafiya a can a yau, ba shakka, zai iya harkar kasuwanci da su, su kuma ƙayatu wajen ilminsa na al'amuran rayuwa irin tasu. Ko a Hausa, mukan ce: *"Wanda ya sanka, shi ya damu da kai."* Haka, shi zai ci ribar hulɗa da kai.

** Mai-Mulkin da ya tunkari al'amuran wata Kasa wadda bai san abinda take ciki ba, ba yadda za a yi ya sami cikakkiyar nasara cikin hulɗarsa da wannan ƙasar. Ko da a hira ne, sarki ya nuna ya san wani abu daga al'amuran ƙasar da tarihinnta, kuma ya san abinda ake magana a kai, ya san abinda ke faruwa a wasu gurare, ba shakka, wannan sarki mai iya ƙayatar da abokan maganarsa ne, balle a ce baƙinsa ne daga can. Wannan ilmi nasa, ba ƙaramar kadara ba ce tareda shi da ƙasarsa, a guraren da suka dace.

Wanda ya san abinda duniya take ciki, ya kuma nemi ilmin abubuwa dabam-dabam, zai tarar cewar duk waɗannan abubuwa ashe makamai ne da zai iya amfani da su ya fidda kansa daga ƙangin

kaɗaita da jin kunya. Sanin ƙasashen Bosnia da Chechnya; Kosovo da Albania da Macedonia; Afghanistan da Pakistan da Iraƙ da Paladinu; tarihinsu da abubuwan da ke faruwa yanzu da dalilansu. Sanin tarihin ƙasashen Gabas-ta-tsakiya da ƙasashen kewayenka da al'amuransu; kai hatta fahimtar sauran ƙabilu da al'adunsu a ƙasarku, duk ilmi ne mai ɗinbun yawa mai kuma amfani. Ita kanta hirar duniya da abinda take ciki abar ƙayatarwa ce, abar wasa ƙwaƙwalwa ce tsakanin abokai; abar hana zaman banza ce. Ba hasara da takaici irin abokanka suna hirar da ba ka fahimta ba, alhali kuwa kana da damar kai ma ka sani, amma ba ka kula ba. Haka ba hasarar rayuwa irin ta mutumin da yake da damar kewaya garuruwa, ko ma ƙasashen duniya, amma bai je ba, yana kuma da hali. Yawon duniya da manufa, ba ƙaramin ilmi ba ne. Lallai mutane masu hali su tashi su je.

Sanin abinda duniya take ciki, da kewayata -in akwai hali- sukan buɗe sababbin ƙofofin alhairi iri-iri; sukan kuma ba da wadatar-zucin cewar an karanta, ko an ji, ko an je wasu daga cikin guraren da Allah (swt) Ya samar a doron wannan duniya tamu. Ganin yadda 'yan-Adam suka bambanta; launi-launi; harsuna iri iri; mutane kima-kima; al'adu da addinai birjik, ba ƙaramar riba ba ce a

rayuwar mutum. Wanda ya yi ɗamara da ilmin sanin abinda duniya ke ciki, ya yi damara mai ƙarfi, kuma nasarar rayuwa ba za ta butulce shi ba, domin ya kiwata tunaninsa da ilmi mai amfanin gaske wanda zai amfane shi ta kowanne juyi. *"Yawon duniya mafarki ne, a tafi a dawo*", in ji Mamman Shata.

8.

FADAR GASKIYA BA TSORO:

Allah (swt) Shi ne, *Gaskiya*. Haka muhimancinta yake. Gaskiya ɗaya take a kodayaushe, kuma wanda yake faɗinta saboda Allah a guraren da suka dace, to, kada ya ji tsoron komai. Tunda ita Gaskiya ɗaya ce, to kuwa ashe duk sa'inda ka maimaitata, ba za ta canja ba. Amma ƙarya fa? Duk lokacin da ka maimaitata sai ta canja, kuma sai an fahimci karkacewar maganar da ka ke yi, ko badaɗe-ko-bajima. Marigayi, Sa'adu Zungur, yana waƙe yana cewa: *"In za ka faɗi, faɗi gaskiya; komai taka ja maka ka biya".* Hikimar wannan baiti ya bayyana komai.

"Idan ka faɗi Gaskiya yau,
ba ka da abinda za ka tuna gobe."



Kullum ita kaɗai ce a muhallinta, ba wani abu sai ita. Duk lalacewar jama'a, suna darajta Gaskiya, faɗarta da aikatata. Haka kuma sukan ƙyami maƙaryaci, duk lalacewarsu. Da zarar mutane sun fahimci halayenka, to haka za su ɗauke ka tareda aƙidunka. Kodayake maƙaryaci ya fi saurin burgewa da karɓuwa, amma kuma saboda *"Karya fure take yi, ba ta 'ya'ya..."*, burgar wannan maƙaryacin ba za ta yi ƙarko ba. Mai son kafa gaskiya a al'umma, da kuma yawan faɗarta duk inda ta dace a faɗeta, yakan yi wahalar karɓuwa, saboda marasa sonta a cikin al'umma yawanci su ne masu gudanar da al'amuran al'ummar. Amma, da zarar an fahimce shi sosai, to kuma yawancin jama'a gunsa za su koma, ko da ba da gangar jikinsu ba, to da ruhinsu da kuma girmamawarsu.

Mun dai gamsu da sanin cewar, shugabanmu, Annabi Muhammad (saw), da Gaskiya ya kafa sunansa, da kuma ita ya kafa addinin Allah (swt). Da an taɓa shaidarsa da ƙarya, ko da guda ɗaya ce, da addinin bai karɓu ba, balle ya ƙure tsawon lokaci. Da sai kafiran su ce, "Haba! Wa zai saurarai maƙaryaci!" Wannan ma Aya ce wadda ta cancanci a yi nazarinta da tunani mai zurfi.

Mai faɗar gaskiya, ya kuma aikatata, ba zai yi

hasara ba, domin yawancin hasara takan haifu ne daga tsari na ƙarya, ko na cuta. A al'umma wadda ta ɗau gaskiya tamkar dukiyarta, ba a sata balle fashi da makami. Shugabanni da suka sa gaskiya a gabansu, to ita ce za ta zama makarin dukkannin sharrin 'yan-adawarsu, ko da bayan mulkinsu. Gaskiya tana da 'yaya da yawa kuma duk na alhairi. Adalci, misali, ɗa yake gareta, domin in ba ita ba shi. Haka alhairi shi kansa. Ba yadda za a yi mai kwatanta Gaskiya ya taɓe, komai talaucinsa domin ita take gamsar da Ruhi ta huro iska mai ni'ima mai kuma bunƙasa wadatar zuci. "*Gaskiya Ta fi Kwabo*", inji masu iya magana, domin ita, kishiyar kuɗi, ba ta ƙarewa, ba ta jawo masifu da rigimu. Hasalima, ita ce maganinsu duka. Ba abinda ya fi ta haske. Duk kuɗin maƙaryaci, talaka mai Gaskiya ya fi shi. Ba zuciyar da za ta shiga duhu in ta yi riga da ita. Da zarar an fahimci kai mai ita ne, to nasara tuni ta zama taka, domin kai ne abokin hulɗa.

9.
TUNANIN FAFUTUKA DA GYARA SANA'A

Farin tunani shi ne wanda yake wanke zuciyar mutum daga duk wasu abubuwa munana, ya kuma



cetarda ita daga halin gazawa. Ba illa ga mutum irin yin tunanin gazawa, ko kuma ya ringa yin zaton wata illa tareda shi, ba tareda cikakken nazari ba. Sai ka ji mai niyyar tafiya yana cewa, *"Abinda ma Jirgin latti zai yi";* ko, *"Karshenta ma a yi Ruwa",* ko, "*Watakila ma tafiyar banza zan yi".* Wani lokaci sai ka ji ɗan-Kasuwa yana cewa: "*In an kawo kayan ma faɗuwa za a yi".* Ko ka ji Mai-neman aiki yana cewa: *"Da kyar zan sami aikin nan",* ko, *"Wannan aikin ya fi ƙarfina, ba zan iya ba".* Ko ka ji mai sana'a yana cewa, *"wallahi na tsani wannan sana'ar",* ko ma ya ringa jin kunya ana danganta shi da ita. Dukkaninsu kaiconsu!

Yawancin waɗanda ba sa zaton nasara tun kafin su taɓuka, to ba sa samunta ko sun taɓukan. Irin waɗannan mutane ne baƙin tunaninsu yake sa wa su yi ta kura-kurai saboda raunin zuci, har sai hasarar ta wanzu, kamar dai yadda suka ayyanata tun farko. Da ma ita suke zato, to kuwa ita za su tarar. Ko da nasara ta samesu a wannan ɗawainiya ta su, ba za ta yi ƙarko ba, domin ba za su riƙe martabar da hanneye bi-biyu ba. A dangantakar Tunani da Halayya, idan ka nemi lalura sai ta zo maka; idan ka ayyana zazzabi sai ka ji shi; idan ka tsoraci mutum sai ya azabtaka; idan ka nemi barci sai ya kamaka; idan gabanka ya faɗi an gama da

kai. Kada ka yarda tunanin gazawa ya sami gurbin da zai zauna ya yi saƙarsa a zuciyarka. Ko menene ƙasƙancin sana'arka a idanun wasu, lallai ne ka ɗauketa da ƙarfi da muhimmanci domin ita ce sana'arka. Idan ka girmamata, ita ma wataran za ta girmamaka. Idan kuwa ba ka sonta, ko ba ka jin ɗaɗinta, to canjata maza. Lallai ne ka zamto mai jin ɗaɗin abinda ka sa a gaba da sana'arka.

Maiyiwuwa ne ka daɗe kana ta tunanin cewar rayuwa ba ta kyauta maka ba. To tashi ka tunkare ta; ɗauki makomarka a hannunka. Idan duniya ta tunkuɗaka, kai ma tunkuɗota, har sai ta ba ka guri. Jin cewar wani ya fi ka a abinda ka iya, shi ke sa wa ya bar ka a baya. Tunanin damuwa da '*ya zan yi*?' hasaru ne manya; kada ka yarda su ci agararka, su yanke hanzarinka ta wajen dakusarda zuciyarka da cin ƙarfin fafutukarka.

Lallai ne duk mai son tunkarar wahalun al'amuransa, da niyyar samun nasara, ya auna su sosai, ya kuma yi tunani mai zurfi a kansu, sannan ya tsara dabarun kuɓuce masu ta hanyoyin da za su inganta sigarsa da mutumcinsa, sannan ya tunkare su gaba-gaɗi. Kada mutum ya yarda shi banza ne, don an faɗa masa, ko an nuna masa haka. Kada ka sake cewa "*Ba yadda zan yi*", muddin a zuciyarka



ka san ba haka bane. Takaicin da ba zai gyaru ba, kamar rasuwar masoyi, ko wata keɓaɓɓar hasara, ko cutar ajali; sune ake yin haƙuri a dangana, don imani ya ƙarfafa, zuciya kuma ta ƙuduri niyar ci-gaba da rayuwa tareda taimakon Allah. Lallai ka zama gwarzo a filin dagarka.

Al'ada ce mai-kyau, mutum ya yi nazari a kan waɗanda yake ganin sun yi nasara cikin rayuwarsu, in dai ta dace da burinsa da kuma tsarinsa. Ka fahimci ya suka yi? Me suke da shi wanda ba ka da shi? Dama can suna da abin, ko kuwa ya aka yi suka samu? Kai kuma ya za ka yi? Kwaikwayon wanda ya ci nasara ba aibi bane; yi masa hassada ne aibi. Mai hassada kuwa a cikin hasara yake kane -kane a kodayaushe. Idan kana neman shawara, jeka ga wanda ya sami nasara a fannin burinka. Nemi direba ya koya maka tuƙi.

Da ka fara fafutuka da addu'ar Allah (swt) Ya tallafa maka, kuma ka daure ba ka karaya ba, kuma ka sa nasara da ƙwazo a zuciyarka, to kuwa nasarar tana tareda kai. An ce: *"Mai nema yana tareda samu",* amma, *"in Jarumi ne".* A rayuwa, mutane suna ganin abubuwa iri-iri; wasu su gamsarda su, wasu kuma su nadamarda su. Amma yawancin fassarar nasara ana yinta ne da son kai ba tareda

zurfin tunani a kanta ba.

Wasu sukan kafa ma'aunin nasara yadda suke sonta ba tareda la'akari da abinda yake maiyiwuwa bane a halin da ake ciki. Sai su kikkiɓo buri ba azanci ba awo, in sun kasa samun nasara su fara ƙorafi. Dá sun yi tunani dá sun fahimci laifukansu; dá kuma sun binciki burinsu da niyyar gyara shi. Lallai ne masu tunanin laifukansu ne suka jawo wahalunsu ko hasararsu, su tsarkakar da zuciyarsu, su daure su nemi gafara daga waɗanda suka yi wa laifin, ba tareda noƙiya ba. Tunanin laifi, musammam ma wanda ka aikatawa wani ba ka nemi gafara ba, yakan hanaka sakat, ya sa ka ringa gudun mutane, ka kuma kasa neman shawara da taimako a kan harkokinka. Managarci ne yake neman gafara ba alkaba'ibi ba. Idan ka nemi gafara daga mutum, ko bai yi maka ba, ka ci riba, tunda ka yi abinda yakamata, kuma hankalinka ya kwanta. Allah (swt) kuma Shi ne Alƙali tabbatacce a muhimmiyar Rana.

Kada mutum ya ringa cewar, *"Mu dama Matalauta ne",* ko, *"Iyayena talakawa ne, ta ina zan arzurta?"* Wai Shin, ba ka ji Allah (swt) Ya na cewa: *"Shi ne Mai fidda mai-Rai daga Matacce"* ba? 'Ya'yan Matalauta nawa ne suka kuɗance a gabanka?



‘Ya’yan Jahilai nawa ne suka zama shaihunnai a idanunka? ‘Ya’yan Talakawa nawa ne suka zama Sarakuna, Ministoci har da Shugabannin-Kasa a zamaninka? Duk waɗannan masu “Rai” ne daga “Matattu”, amma ba haka siddan ba. Kai ma tashi tsaye ka ga ikon Allah (swt). Ba abinda ba za ka iya zama ba, in dai abin ya dace da kai, kuma ka neme shi ta hanyoyin da suka dace.

Lallai duk mai son nasara a rayuwarsa, to ya gujewa macewa daga rayuwar tasa, ta hanyar tashi tsaye da yin gini a kan alhairi da baiwowin da Allah (swt) Ya samar tareda shi. Ba wanda Allah (swt) Ya halitta, ba tareda Ya ba shi makami da damar inganta kansa ba. Idan ka ƙi fahimtar makaminka (watau, wata baiwa da Allah Ya yi maka), ko ka fahimceta amma ka ƙi amfani da ita, to, kuwa ko badaɗe-ko-bajima, sai ka shiga wahala, in dama ba a cikinta kake tuni ba. Kaicon wanda ya san zai iya yin wani abu na halal domin ya ci da kansa gaba, amma ya ƙi yi don jin kunya, lalaci ko wani dalili mara ƙarfi dabam. Kai za ka wahala, kuma kai ne za ka zargi kanka da aibinka.

Ka sarrafa baiwar da Allah (swt) Ya yi maka wajen inganta kanka, ka kuma taimakawa wasu duk sa’inda dama ta samu. Da mulki, da dukiya, da

ƙwaƙwalwa mai kaifi, da iya waƙa, da iya magana, da ƙarfin jiki (ƙarfin tuwo), iya noma, iya ƙirƙiro labarai, gudu, iya bal, iya talla; ban dariya; iya saƙa ko jima ko ƙira ko ɗinki; iya girki; kai, ko mecece baiwar da Allah (swt) Ya yi maka, idan ba ka yi amfani da ita ka inganta rayuwarka ba, to, ka yi babbar hasara.

Wani daga dako yake arziki har ya sai manyan motocin sufuri, don ya fahimci cewar Allah (swt) Ya yi masa baiwa daga ƙarfin jikinsa. Sai ka ga Gyartai ya fara sayar da ƙwarya, domin bai raina iya ɗinketa ba. Wataran sai kantin kwanuka. Sai ka ga Tela ya kafa masana'antar ɗinki, don bai raina sana'arsa ba. Da wasu Mawaƙanmu ba zunɗe suke yi ba, da yanzu suna cikin manyan masu kuɗinmu. Da wasu masu iya Girki a cikinmu ba daudu suke ba, da yanzu sune masu gudanarda manyan gidajen abincinmu. Da masu iya Magana a cikinmu ba roƙo ko sharri suke ba, da yanzu sune sha'awar kunnuwanmu. Da wasu masu kuɗi a cikinmu ba almubazzaranci suke ba, da yanzu ba wanda yafi su. Da Masaƙanmu da Maƙeranmu da Majemanmu ba su rena sana'unsu ba, da yanzu kayansu muke sawa. Da kowa ya ɗau sana'arsa da mutumci, kuma kowa ya girmama sana'ar wani, da yanzu ba haka ba.



Baƙaƙen tunani da ke sa a raina sana'a ko a watsarda ita jin cewa ita wulakantacciya ce, suke sa mu koma baya, masu sana'ar su lalace, al'umma ta lalace. A hankali, har sai waɗannan sana'un su ɓace mana, ko wasu can su ɗauke su, su adana su su kuma ci ribarsu muna zaune muna kallo. Sai ka ji wani wawa wanda ya ƙi neman aikin yi, amma yana kyamar sana'ar wani. Sai ka ji ya ce, 'ai wane mahauci ne' ko, 'ai gyartai ne'. Ya manta in ba su yawancinmu ba za mu ci nama ba, ba kuma za mu iya sayen sabuwar ƙwarya duk sa'inda tamu ta fashe ba. Irin wannan hassada da rashin hankali, ba ƙananan illoli suke yi mana a cikin wannan al'umma tamu ba.

Amma kyautata sana'u da alfahari da su; tareda binciken baiwoyin da Allah (swt) Ya yi wa mutum da kuma amfani da su cikin hikima da alfahari da hazaƙa, su ne dangin fararen tunani masu kawo maslaha da arziki a cikin al'umma. Dagewa da sarrafa rayuwa da duk baiwar da Allah (swt) Ya bayar ta hanyar kirki sune a'ala, kuma sune shukar da za ta tsirar da furannin nasara ga wanda ya gane. Duk wanda ya girmama sana'rsa da ta wasu, ya kuma yi fafutuka a kanta, to a hankali zai ga sakamakonsa na alhairi da gamsuwa da kai. Wannan shi ne mai nasara.

10.
KORAR HASSADA A TUNANI

Son-kai da ganin-ƙyashi mugayen abubuwa ne, kuma sukan dakusarda arziki, ta wajen haifarda hassada. Jin ba wanda ya dace sai kai; ko jin nasarar wasu hasararka ce, ko hasarar wasu ita ce ribarka ko nasararka, ba munin da ya fi su. Mai irin waɗannan tunani shi ne mai hassada, wanda in dama ta samu sai ka ji ta a bakinsa da ayyukansa. Irin wannan mahassadi shi ne la'ananne wanda zai tararda nadama a rayuwarsa ko badaɗe ko bajima.

Idan kai mai wannan hali ne, to wanke kanka nan da nan, ka fara ɗaura niyyar taimakon wani, ko yaya, ka ringa tunanwa kanka cewar hassada muguwar ɗabi'a ce. Da ka ji ka fara tunaninta a kan wani ko wasu, maza ka tsaida wannan tunanin, ka tuba ka bar wa Allah (swt) al'amuranSa. Aikin alhairi daidai ƙarfinka ba ƙaramar nasara ba ce a tareda kai, domin zai sa ka ji a ranka kai mutumin kirki ne, ka kuma ji cewar kana kusa da Allah (swt). Aikin sharri kuwa, shi zai sa ka ji lallai kai mutumin banza ne, wanda ya yi nesa da Allah (swt). Ba mai azabta kansa irin wanda ya san shi mutumin banza ne, ba sai an faɗa masa ba. Wannan ya yi matuƙar hasara. Duk mahassadi

yana cikinsu, kuma ya sani. Kullum ransa a ɓace.

Wanda ya yi tsaf cikin tunani, fi-sabilillah, kuma zuciyarsa ta tabbatar masa, tana shaida masa cewar: “Kai mutumin kirki ne”, to wannan mutum ya cimma falalar rayuwa da wadatar zuci. Amma wanda ya bincika kansa ya tarar da kishiyar haka, tilas ya farka ya canja salon rayuwarsa. Irin wannan auna kai, ba ƙaramar riba take kawo ba. Lallai fa ka tuna: Ba wanda ya sanka fiye da kai; kuma ba ka da abokin shawara fiye da kai. Ya rage naka ka farka, ko ka ci gaba da barci a gwalalon nadamar rayuwa da ƙaskancin matsayi ta hanyar hassada. In wani abune ya ɗaure maka kai, nemi shawarar wanda ka san masoyi ne, kuma ya san abin. Tashi ka taimaki kanka tun kana da lokaci.

Farin Tunani da aikata alhairinsa, sukan taimaki zuciya, su ƙara mata ƙwazo da zaton nasara a dukkannin fafutukar da za ta yi. Baƙin Tunani kuwa da aikata sharrinsa su ke lahanta zuciya, su hanata zaton nasara, su kuma sa ta cikin fushi da nasarar wani. Lallai mutum ya faɗawa kansa Gaskiya, ya bar tunanin hassada ya nemi nasa arzikin. Lallai ne mutum ya roƙi Allah (swt) Ya taimaka masa kamar wane, ko ma fiye da wane, idan shi mai sha’awar wanen ne. A cikin duk

lokutan da mutum yake yin hassada, ba shakka a irin waɗannan lokatan, yana cikin masifu huɗu ko ma fiye da haka, waɗanda ya sa kansa ciki:

i: Yana cikin tuhumar Allah (swt) a kan abinda Ya hukumtawa wani. 'Don me Allah Ya ba shi?' Tuhumar Allah, raina Allah ce, kuma ba ƙaramin ɓata bane. Wa'iyaz Billah! Allah Ya tsare mu da wannan babban kafirci, amin.

ii: Yana cikin mugun baƙin ciki da azabta kansa, domin ransa a ɓace yake cikin fushi da nasarar wani. Wannan ba ƙaranar cuta bace, wadda za ta iya haifarda ciwon zuciya da halaka.

iii: Yana cikin hasara, domin hassadar tasa ba za ta canja komai ga wanda yake wa hassadar ba. Wannan ba ƙaramin ɓata lokaci bane.

iv: Yana cikin maƙurar takaici, domin a daidai wannan lokacin, wanda ake yi wa hassadar bai san ma ana yi masa ba; yana can cikin bushashar nasararsa da arzikinsa. Kuma Allah (swt) Ya kan dubi wannan hassadar ya ƙara nasarar da arzikin, ala-barshi mai hassadar ya mutu. Da ma an ce, "*Hassada ga mai rabo taki".* Hassada, ba shakka, ba ƙaramar hasara ba ce.



Idan abu ya fi ƙarfinka, kuma ka gwada ka gwada amma babu alamar cimma maslaha ko nasara, to sake mai da al'amuranka wajen Allah (swt), ba tareda hassada ga waɗanda suka sami nasasar ba. Amma lallai ka ci gaba da son jama'a, sha'awar masu nasarar, ka kuma kare mutumcinka, imaninka da ibadunka. Lallai ne ka daure ka ci gaba da fafutukarka, ko da ka canja bukatunka ne. Ka tabbata kana cikin yanayin zuci mai-kyau da kuma yawaita zaton alhairi, domin *"wani hanin baiwa ce"*, in ka yi tunani a gaba.

Kada ka yarda ka raunana wajen zaton canji na alhairi daga Allah (swt), ta hanyoyin da bá ka zato, amma waɗanda su ne mafi alhairi a gareka. Allah (swt) Ya karanci zuciyarka, Ya riga Ya zaɓar maka rayuwa mafi dacewa a gareka, in dai ka amince ka bar al'amuranka a hannunSa. A Halayya irin wannan, ka roƙi halayyar Annabi (saw), domin sai Allah (swt) Ya fara yi maka kyauta da *Wadatar Zuci* ta zama *Ganimarka"*. Nan da nan sai ka ga ka fara tunawa da sauran baiwoyin da Allah (swt) Ya yi maka, waɗanda za ka iya sarrafasu yadda suka dace domin ka cimma sabon burinka. Maiyiwuwa ne a nan arzikinka da bushashar rayuwarka suke. Kai ne ba ka bincika ba; ko kuma sai yanzu Allah (swt) Ya buɗa maka saninsu, domin sai yanzu

lokacinsu ya iso. Allah (swt) baYa barin mai bukatar alhairi a cikin nadama. Amma mahassadi kullum a cikinta zai kasance. Kowa ya san kansa, kuma kowa ya san abinda nake magana a kai. Da jama'a sun fahimci ba ka da hassada ko ganin ƙyashi, toh ka tabbata ka ci babbar nasara. Kai ne nasu a kowanne lokaci, ko ba ka san hakan ba.

11.
YAKANA DA KULA DA HAKKI

Waɗannan manyan halaye na-gari ba su da bambanci da junansu sosai, kuma rashin ɗaya daga cikinsu ba ƙaramar hasara ce ga Halayyar mutum ba. Rashin Yakana, shi yake kawo taka haƙƙin wasu; ka ga mutum yana ta wahalarda mutane, yana wulaƙantasu, ko yana matsanta masu, ko kuma yana ƙuresu. Mutumin da ba shi da Yakana, shi ne ya yi hasarar muhimmiyar madafar rayuwa mai ƙarko, komai ƙudinsa ko mulkinsa. Mutumin da ɗabi'arsa ita ce ya keta haddin wasu, to kuwa zai tadda baƙin-ciki, ko ba-daɗe ko ba-jima. Rashin Yakana da rashin Sanin Yakamata uwarsu ɗaya ubansu ɗaya. Sukan kashe aure; sukan kori 'yan'uwa har ma da abokan arziki; sukan jawo hasarar sana'a da baƙin jini irin wanda ba a saba yinsa ba.



Mafi yawancin mutane ba sa son a wulakantasu ko a ƙaskantarda su a nuna masu ba su isa ba. Waɗannan munanan ɗabi'u kuwa su ne halayen mutane mara Yakana. Waɗanda aka wulakanta ɗin tilas ne su yi fushi, in dai suna da mutumci, kuma ƙiyayya ta iya shiga tsakani in ba a yi hankali ba. Jama'a sun ƙi jinin a taka haƙƙinsu, a hana su damarsu da 'yancinsu; a hana su sakewa da walawa. Waɗannan kuwa ɗabi'un mara Yakana ne. Hankali ne a tsammaci mutane za su fusata idan aka takurasu, ko ma su kai duka idan *tura ta kai bango.* Yawancin mutane ba sa son mai girman-kai, mai burga da son nuna isa. Waɗannan kuwa su mara Yakana ya gawurta a kai. Tilas a tsammaci mutane za su tunzura idan aka yi masu girman-kai, kuma su mai da martani irin nasu duk lokacinda dama ta samu. In sun yi haka, wa zai zarge su?

Yakamata mutumin da yake neman gyara rayuwarsa da arzurtata ya san Yakana, ya kuma nunata a halayensa da ɗabi'unsa. Kada ka ce sai ka ƙure wani, ka nuna masa bai isa ba, sannan zai san ka isa. Kada ka ce ba wanda ya isa ya yi magana in kana zaune. Kada ka ƙi sauraron mai ba ka haƙuri, sai in ba yadda za ka yi. Kada ka fizge abu daga hannun wani don kana zaton bai isa ya riƙe abin ba; karɓi a hankali cikin ɗa'a. Kada ka shiga ɗakin

mutum gaba-gadi ba izninsa, don shi yaronka ne, ko danka ne. Kada ka tofarda miyau a gaban mai-kurji. Kada ka yi latti don ka isa, ko don mutanen ba su isa a idanunka ba. Kada ka badawa jama'a kura don kana cikin mota, shige a hankali. Kada ka zagi mutum don ka san ba zai iya ramawa a fili ba. Kada ka kwacewa yara alawarsu ko ka zaluncesu don ba su da karfin ramawa. Kada ka kushe aikin wani don son muzanta shi. Kada ka washi abin yabo. Kada ka ci fuskar wani, ko ka sa a yi masa dariya don kana zaton bai isa ba. Kada ka cinkishi mutane da surutanka, don kana zaton ba yadda za su yi. Kada ka wulakanta iyayenka da iyalanka, ko ka hana su daga arzikin da ka ke da shi; ku ci tare shi ne karkon arzikin. Kada ka zagi na gaba, ko yawan kushe masa, don kawai ba ka sonsa, ko ba ya gurin. Jeka ba shi shawara in za ka iya, ko da ta hanyar wani ne. Kada ka wulakanta masu nema a gurinka ko marasa galihu don kana zaton ka fi su. Ba su taimako, ko ka ba su hakuri da murya mai taushi. Kada ka zalunci wani ko wasu don kana zaton ba yadda za su yi da kai. Kada ka ki cika alkawuranka don kana zaton ba yadda za a yi da kai. Lallai ne ka kiyayi kanka.

Duk abinda ka san kai ba ka son a yi maka, to, kada ka yi wa wani. A wannan duniya, matsayinka



zai iya canjawa nan-da-nan daga matsayin mutum gingirim mai tsoratarwa zuwa na abin tausayi. In mulki ne, akwai ranar ƙarewarsa. In kuɗi ne, akwai inda ba su isa ba. In kyau ne, akwai wanda ya fi ka. In Ilmi, kai koma bayan wasu ne. Ko menene ka ke da shi, mutumci ya fi shi, kuma wasu da yawa sun fi ka abin. Maza zubar da girman kanka, yadda za ka dace da jama'a ka sami walawar rayuwarka. Ba sai ka nuna ka isa sannan za a san ka isa ba. Wanda bai isa bane yake son sai ya nuna. Mutane sun san sirri da matsayin kowa. Mai Yakana ya san haka.

Mutum mai Yakana shi ne ya san dabarar rayuwa mai falala, kuma Yakanarsa takan sanyayarda zuciyarsa ta kuma jawo masa alhairi daga duk inda ba ya zato. Yabon abin yabo; godewa abin godiya; girmama masu mutumci; tausayin mawahalta; ladabta na gaba; yalwata murmushi da miƙa hannun gaisuwa da na kyauta; halarta a kan lokaci; cika alkawari; bin ƙa'ida da dokoki; gyara kuskure; ba wa wasu dama, ƙauracewa guraren da ba su dace da kai ba -duk halaye ne nagari. Mutanenda aka yi masu Yakana da ɗa'a, sukan ji daɗi, su kuma saka da yabo ko ma da wani alherin dabam. Wanda ya yi Yakanar shi ne ya ci riba mai yawa, mutumcinsa da kimarsa su ɗaukaka a idanun jama'ar. Shi ne irin mutumin da jama'a za su iya

sawa a gaba a kan al'amuransu duk sa'inda dama ta samu. Saboda haka, Yakanarsa, ta kafa masa tushen nasara cikin nasa bukatun, ko a yanzu ko a gaba. Hausawa sun ce: "*Alhairi danƙo ne, ba ya faɗuwa ƙasa banza".* Wannan magana cike da hikima take, kuma lallai mutum ya lura da ita.

Mara Yakana, shi zai ga wulakancin jama'a duk sa'inda dama ta samu garesu. Ba shakka a kodayaushe jama'a suna cikin lura da halayen mutane dabam dabam. Saboda haka, rashin Yakana ashe tushe ne na hasara a cikin bukatun mutum, ko a yanzu ko a gaba.

12.
GYARA MATSAYI:

Gyara Matsayi da hanyar "Bi" a rayuwar mutum su ne ƙwararan ginshiƙan ni'imar rayuwa waɗanda a nasu juyin suke kafa ginshiƙan shiriya da Jin-dadi. Mutanen da ba su da tafarkin "Bi" a rayuwa, sukan shagalce cikin rashin makoma, jidali da mummunan matsayi. "*Manufarka ita ce Madafarka"* ta rayuwa, domin sai kana da manufa za ka san inda ka dosa; watau, ina ne al-ƙiblarka, wadda kuma ita ce za ta kai ka ga tsara hanyar cimma manufar.



Mutane masu manufa su ne suke iya gyara matsayinsu su kai kansu da kuma al'umma inda suke so. Da babu irin waɗannan mutane, da har yanzu ɗan-Adam bai ƙirƙiri tufafi ba, balle muhalli; da har yanzu bai iya ɗinka takalmi ba, balle ƙirar basukur, ko mota, balle kuma jirgi. Dukkanin ababan ci-gaba masu taimakawa da saukaƙawa da daɗaɗa rayuwarmu, sakamakon himmar mutane ne masu son gyara matsayinsu. Irinsu ne suke shiga ɗawainiya iri-iri ta bincike domin su gano duk yadda za su yi domin su kyautata rayuwarsu da kuma ta al'ummarsu. A sakamakon wannan ɗawainiya tasu, kowa zai amfana ya ci riba.

Yawancin ilminmu da fahimtarmu da dabarunmu; ci gabanmu da jin daɗinmu, duk daga sakamakon ɗawainiyar irin waɗannan mutane ne. Telan da ya fito da sabon salon ɗinki, yana cikinsu. Likitan da ya binciko hanyar sabon magani, yana cikinsu. Samarin da suka gyara hanya don su ƙawata unguwarsu, suna cikinsu. Mai hikimar da ya ƙirƙiro wata na'ura, yana cikinsu. Mai basirar da ya rubuta abinda zai amfani wasu, yana cikinsu. Ko da kanka kaɗai ka samowa hanya ma fi maslaha wadda za ta kyautata rayuwarka, kana cikinsu, domin wataran wani zai yi koyi da kai.

Lallai mutum ya bincika kansa, kuma ya yi ƙoƙarin inganta kansa don ya zama cikakke mai tsarin rayuwa da ƙoƙarin ciyarda kansa da wasu gaba. Wasu a rayuwarsu, sukan saduda su ƙi himmata, don a zatonsu taɓukawar ba za ta canja komai ba. Irin wannan salon rayuwa ba shi da amfani, domin shi ke dakushe al'umma har talauci da rashin makoma su ci ƙarfinta.

Amma, a al'ummar da jama'a suka yunƙura wajen yin abubuwanda za su ɗaukaka matsayinsu, tareda kishin junansu, to ba shakka, su ne waɗanda falala da kwanciyar hankali za su lulluɓesu. Al'ummar da akodayaushe tunanin yadda za su ciyarda kansu gaba suke yi, don matsayinsu ya inganta, rayuwarsu ta zama mai amfani, falala da ban sha'awa, ita ce al'umma ta-gari, wadda ta san ciwon kanta. Haka mutum mai wannan hali don kansa, shi ya kama hanyar nasara a rayuwarsa.

Manufa takan faɗaɗa ta zama buri ga waɗanda suka taceta, suka ɗau wani muhimmin abu da za su yi fafutuka a kansa a rayuwarsu, ko a yanzu ko a wani lokaci na gaba da ya fi dacewa. Shi kuwa buri madaidaici, wanda aka ƙudire shi saboda Allah, watau da kyakkyawar zuciya, inji ne na rayuwa, sai ka hau ka yi ta sukuwarka a kansa; in



ba ka dangana yau ba, gobe tana nan. Lallai ne irin wannan aƙida ta rayu a zukatan masu burin kyautata rayuwarsu da ta wasu. Amma kuma buri na rashin kima, wanda ya ginu saboda hassada, ko nufaƙa, ko zaƙalewa da gasar banza, ƙaya ne a tafarkin rayuwa, domin ya iya zama sharri ya kawo cikas a rayuwa a gaba. Irin waɗannan mutane ne suke yanƙwanewa su lalace. Nan da nan su tsofe.

Idan ka gyara tunaninka, to sai ka ɗau damarar gyara rayuwarka. A kodayaushe ka nemi mafi kyau a komai, ko da don ka kalla ne, domin kallon abu mai-kyau ko ayyana shi a zuci, yakan haskaka Zuciya ya kuma sanyayata cikin tuananin alhairi.

Ringa duba Sararin Samaniya cikin sha'awar tsarinta da zurga-zurgar taurarinta da ƙyallinsu da nisansu. Yi al'ajabinsu da tunani a kansu da yabon hikimar Wanda Ya haliccesu. Ringa sansana turare mai-kamshi, kuma ka ringa shafa shi. Ringa kallon furanni da launukansu masu ban sha'awa, ka kuma samarda su a muhallinka. Ringa sha'awar jama'a lokacin da suke cikin bushasha ta buki ko ta wani alhairi da ya samu. Ringa kallo kana nazarin 'yan yara in suna wasa ko suna hira cikin irin nasu azancin. Ringa kallon dabbobi da tsuntsaye a muhallansu na ainihi suna harbin iska. Ringa kallo

da sha'awar mutane masu tsabtar kaya da ado mai tsari a jikinsu, ka kuma lura da yadda suke alfahari da kansu. Ringa hirar nishaɗi da mutane da abokai masu iyata domin yalwata murmushi ko dariya matsakaiciya. Ringa hira da 'ya'yanka da matarka, domin ku fahimci juna ku ƙara kusantar juna. Ringa nazarin mutane masu manufa a rayuwarsu, waɗanda saboda ƙoƙarin inganta kansu, al'uma gaba ɗaya ta ingantu.

Duk waɗannan ɗabi'un inganta kai ne ta wajen kwantarda zuciya da ciyarda ita ga abubuwan alhairi. Zuciyar da ta ci ta sha alhairi, su za ta haifar. Wanda hankalinsa yake kwance shi ya ci riba, kuma shi ne mai iya nazarin al'amuransa.

Saboda haka, lallai ka daure ka kauda idanuwanka da tunaninka daga munanan abubuwa ko na sharri, ko na lalaci, don ta hakane kaɗai za ka iya keɓe zuciyarka daga sharrin da lalacin. A taƙaice dai, lallai mutum mai son gyara matsayin rayuwarsa cikin nasara, ya gyara zuciyarsa, ya kuma yi yunƙuri, ya dage sosai wajen cimma manufarsa da burinsa ta hanyoyin da suka dace da abinda yake nemarwa kansa ko jama'arsa. A sannu-da-sannu, zai ga sakamkon fafutukarsa. Hausawa ma, sukan ce: *"Mahakurci Mawadaci".*



12.
NUTSUWA DA HANKALI

Waɗannan muhimman sigogi ne, musammam ma idan aka yi wa mutum shaida da su. *"Kai! Ai Hajiya Amina mace ce mai nutsuwa da sanin yakamata.* Ko kuma,. *"Musa? Ai yaro ne mai hankali".* ko kuma, "*Ganiyu da nutsuwa yake".* Ba shakka, waɗannan ababan alfahari ne ga duk wanda ya mallakesu, domin sukan ƙara masa mutumci su kuma kare shi, sannan su hanzarta nasara a cikin al'amuransa. Duk nutsattse ya san abinda yake yi.

A wasu lokatai, sai ka ga shekaru ko muƙami ko cuɗanya da jama'a ba su ƙari waɗannan sigogi ba. Sai ka ga Yaro mai hankali; Babba gaɓo. Shugaba mara kirki; talaka mai tausayi da son taimakawa. Ɗalibi mai nutsuwa; Malami watsatstse. Namiji rago; Mace jaruma. Da Kimtsuwa da Nutsuwa da Shiriyar hankali, sukan samu ne ta hanyar kyakkyawan raino daga iyaye, 'yan-uwa, malamai da abokai nagari. Haka lalacewa, takan zo ne saboda sakacin reno daga waɗannan mutane. Tsoron Allah da bin umarninSa, sukan sa mutum ya zama mai ɗa'a da hankali, waɗanda su kuma suke taimakawa wajen kafa ginshikin Nutsuwa da Sanin Yakamata. Kishiyoyin waɗannan, suke sa

mutum ya zama mara haƙuri, mara tsinkaye.
Ga misalai:

** *Gurɓataccen Ra'ayi*: yakan wanzu a yawancin lokatai saboda gajeren haƙurin sauraron cikakken bayani. Nan da nan sai ka ga mutum ya ɗau ra'ayi ba tareda jin ilahirin maganar ba. Wannan Hali na gajen-haƙuri yakan sa mutum ya taka haƙƙin wani, ko mai-Shari'a ya yi zalunci, ko Shugaba ya ɗau matakin da ba zai haifarda alhairi ba. Maƙiya da mahassada, mutane ne masu baza munanan labarai gameda wanda ba sa so. Idan mai gajeren haƙurin bincike ya ji, sai shi kuma ya karɓa ya aikata nasa sharrin ko ya baza shi. Ta haka, sai sharri ya bazu a ƙasa, ƙiyayya kuma ta sami makwanci. Amma, masu nutsuwa da haƙurin binciken al'amura, suke da makaman fyaɗe sharri da masharrata. "*Mai haƙuri shi kan dafa dutse ya sha romo."* Akwai hikima a wannan magana.

** *Jahilci:* Kowa yana da Jahilcin wasu abubuwa, amma mutum mai nutsuwa ne kaɗai ya san haka, da kuma inda nasa jahilcin yake. Mara nutsuwa yakan jahilci abubuwa da dama, amma, kaico! Bai san haka ba. Kamar dai Ilmi ne; sai ka ga wasu suna ta ƙoƙarin sai sun burge mutane da son nuna sun san komai, har su je suna bayarda



amsoshin da za su ɓadda mutane, su kuma jefasu cikin halaka. Amma idan mai Nutsuwa ya ji tambaya, ko wani abu da bai sani ba, nan-da-nan zai san aikin dake gabansa shi ne ya nemo amsar abin don inganta nasa ilmin shi ma, maimakon ya ba da amsar da ba daidai bace, nan gaba a ji kunya. Gudu daga Jahilci yanayi ne a zuciyar mai-Hankali, mai-Nutsuwa, wanda ya san abinda yakamata. A kullum nutsatstsen mutum ya kan nesarda tunaninsa daga ra'ayin riƙau, son-iya-yi, son nuna sani, da hanzarin ɗaukar matsayi ba tareda cikakken sanin bayanin matsalar ba, ko saurin bayarda amsa ba tareda sanin haƙiƙaninta ba. Irin waɗannan mutane masu shisshigi su ne suke dulmiyar da al'umma, musammam a inda jahilci ya yi yawa, su jawo ruɗani da muguwar hasara ga jama'a, musammam waɗanda su ka dogara da su.

Mecece alamar MALAMI na ƙwarai?
Mecece alamar SHUGABA na ƙwarai?

Malami na ƙwarai shi ne wanda aka yi masa tambaya, amma da ya nutsu cikin tunanin bai san amsar ba, sai ya shaidawa mai tambayar da cewar, *"Ban san amsar tambayarka ba. Amma, insha'Allahu, yau zan bincika littattafai, idan ka zo*

gobe zan yi maka bayani yadda zan iya". Wannan Malami ya san Allah (swt) ne kaɗai Yake da cikakken Ilmin komai. Duk Malamin da ya cika-baki ya san komai, kuma yake ta ƙoƙarin amsa kowacce tambaya, to guje masa. Ba masani bane, mai shisshige ne kawai. Masu sauraronsa da aiki da maganarsa sai sun yi da-na-sani wataran.

Shugaba na ƙwarai shi ne wanda ya yi kuskure a wata matsala ta shugabanci. Da aka sanarda shi kuskuren, sai ya nutsu, bai ɗimauta da fushi ba don ya san idan bai gyara ba, jama'arsa ne za su cutu. Saboda haka, ya karɓi kuskurensa ba tareda girman kai ba, ya nemi gafarar jama'arsa, ya kuma gyara kuskuren da sabon tsari wanda ya dace. Wannan shugaba ya san Allah (swt) ne kaɗai, saboda kulliyar IlminSa, ba ya kuskure a kan kowanne al'amari a cikin mulkinSa. Duk shugaban da ya san yana cikin kuskure, amma ya ƙi gyarawa don girman-kai ko son-kai ko mugunta, to ba shugaba bane, mazaluncin jama'arsa ne kawai. Nutsuwa da sanin haƙƙin jama'a su ne suke sa a gane shugabanni da mutane na ƙwarai.

** *Camfi:* Mutum nutsatstse ba ruwansa da Camfi, don ya san Camfi ya kan keta imani, ya jefa mai shi ɓatan da ba dawowa. Haka kuma mai



nutsuwa ya san, lallai idan ya daka ta Camfi da wasu al'adun banza, zai dakusarda rayuwarsa ne kawai, watakila ma har da ta wasu. Duk mai hankali ya san yarda da Canfi, balle bin tafarkinsa, yana daga bakaken tunani. Duk kuma wanda ya dauwama cikinsa, to kuwa wata rana zai iya yin maraba da tsafi. Abin takaici shi ne akwai masu camfin da suke zaton suna amfani da Sunaye ko Ayoyin Allah (swt) don cimma manufofi da sauran bakaken ayyuka, amma ba su fahimci cewar su matsafa bane. Akwai kuma masu aikata miyagun zunubai cikin camfa cewar alhairi zai zo masu na kudi ko na wani mukami ta hanyar wadannan zunuban, amma ba su san su gafalallu bane. Sun raina Allah (swt) da gargadinSa. Ba shakka, sun kasance masu matukar izgilanci ga Mahaliccinsu; kuma mun san makomarsu. Wa-iyaz billah!!! Hakika wasu suna cikin wannan kafirci.

Ba irin halakar da Camfi ba ya kawowa ga mai yinsa da mai yarda da shi. Nutsuwar tunani ne kawai ke karfafa imani yadda zuciya da tunaninta za su yaki shaidanci, su kafa iyaka mai karfi daga sharri, su kuma iya aikata abubuwan da suka dace don samun nasara a dawainiyar da ke gabansu. Camfi shi ne kishiyar Imani, kuma ba abinda zai haifar sai sharri. Idan kana da bukata wajen Allah

to nemeta wajen Allah. Idan kana da ita a wajen wani, to nemeta wajen wanin, sannan ka roƙi Allah Ya taimaka maka. Haƙiƙa mutane masu Nutsuwa da Hankali su ne abokan sirri, su ne abokan harka. Su ne masu nasara a aljihunsu.

13.
HAKURI, JURIYA DA LA'AKARI DA WASU

Mutane marasa Haƙuri da Juriya su ne wahalallu a zuciyarsu, kuma ba a kowanne hali za su yi rayuwa mai kyau da amfani ba. Irin waɗannan mutane, ba su iya zama da jama'a ba tareda rai yana ɓaci ba. Sannan yawancinsu, masu ɓoye wata gazawa ce a tareda su. Wannan gazawar, ita ce take ƙona masu zuciya, suna tozarta kansu daga yanayin fuskarsu da kalamansu waɗanda suka bayyana daga abinda zuciyarsu da tunaninsu suke dafawa. Amma Mahaƙurta, su ne masu zuciya a sanyaye cikin ni'imar gamsuwa da kansu, waɗanda za su iya rayuwa a ko'ina, kuma a kowanne hali ba tareda hassada ko ƙin jinin halayyar rayuwar wasu ba. Hausawa sun yi hikima da suke yi masu take suna cewa: *"Mahakurci Mawadaci".* Ba makawa hakane ta duk inda ka auna. Mahaƙurci ne kaɗai zai iya kare imaninsa

daga jinkirin amsar addu'o'insa, a nasa ganin; ya kuma sa ran Allah Zai amsa a kan lokacin abin.

Haka, masu Juriyar jama'a, ba ruwansu da launin fatarka, ko ƙabilarka, ko addininka, ko matsayinka a wajen hidimarsu ta kyautatawa jama'a saboda Allah (swt). Masu waɗannan halaye na-gari, sun san akwai hanyoyi da yawa na kallon abubuwa da yawa, kuma ba ruwansu da tunanin haɗama, ballantana na ƙyashin wani ya samu. Waɗannan mutane su ne salihai ababan misali da koyi.

Adalcin rayuwa a gunsu shi ne kawai su rayu ba matsi ko matsantawa wani. Aƙidarsu ita ce, *"In Alhairi ne, mu Ci tare"*; *In kuma sharri ne, ka Ci kai kaɗai".* Sun san cewar akwai ƙazamtu a rayuwa waɗanda illolinsu sa iya lahanta jama'a. Sun san akwai mutanen banza waɗanda suke yawan gurɓata gaskiya, sannan su sa ƙafa su shure abin tausayi. Amma nutsuwarsu da haƙurinsu da juriyarsu sun haɗu sun karesu daga son yin mugunta, ganin-ƙyashi, girman-kai da annamimanci, ko da za a kwaɗaita masu wata bushasha in sun aikata hakan. Waɗannan mutane su ne masu nasara a cikin rayuwarsu, duniya da lahira. A cikinsu ake samun masu:-

** *La'akari da wasu;* waɗanda suka san cewar akwai wasu ba su kaɗai ba, kuma sun san cewar Son-kai shi ke cizge jijiyar ci-gaba da zaman-lafiya a cikin al'umma. Masu La'akari da wasu sukan yalwata tambayar kansu:

"Menene amfanin Dukiyata ko Arzikina, idan ban bautawa Allah (swt) da su ba? Hankali ne na ki taimakon maƙwabcina, amma na je na ba da gudun-mowar fariya da ƙarya a daji? Shin, yakamata na ba da lokacina da ƙarfin jikina ga wani aiki na alhairi don ƙaruwar jama'a, tunda ba ni da kuɗin bayarwa, ko kuwa yawon banza da zaman banza sune suka fi min alhairi? Mecece dangantakata da sauran jama'a?: Shin damuwarsu damuwata ce; kuma jin-daɗinsu nawa ne? Ko kuwa, son-kai da annamimanci da mugunta su ne tafarki na?

A tsarin mutum da halittarsa, akwai kogon tunani iri biyu kamar yadda muka sani: Kogon *Farin Tunani* da na *Baƙin Tunani.* Watau, a bayyane, akwai siffar "*Annabci"* da ta "*Ibilisci"* ga kowanne mutum, kuma zaɓi na gareka. Ko ka zaɓi ɓangaren Annabci ka yi fafutuka don Jama'a ba don kanka kaɗai ba; ko kuma ka zaɓi ka yi son-kai ba tareda la'akari da halayyar jama'a ba. Wanda ya ce: *"Ni,*

ba abinda ba ni da shi, don haka ba ruwana da kowa”, to ya zaɓi ɓangaren ibilisci. Amma, wanda ya ce: *“Allah Bai ba ni ba, sai don Yana son in aikata alhairi; na yi amfani da wani bangare na baiwar da Ya yi min ta wajen fafutukar jama’a”,* to, ba shakka wannan mutum ya zaɓi ɓangaren Annabci. Allah (swt) Yana tareda irin waɗannan mutane waɗanda suka bi tafarkin annabawa, domin su ne suka zaɓi hanyoyi madaidaita, waɗanda za su kaisu ga nasara mai amfani. Haka Zai ta ƙara masu wannan baiwa ninkin baninki, duk sa’inda suka aikata alheri da ita. Amma waɗanda suka zaɓi tafarkin Iblis, to su ne masu hasara masu fama da lahanin zuci.

14.
ZURFAFA TUNANI

Tun daga wayewar gari har zuwa lokacin barci da daddare, ɗan-Adam cikin tunani yake a kowacce daƙiƙa ta rayuwarsa, ko yana sane, ko ba ya sane. Bambancin mutane shi ne na zurfafa tunanin don ganin damarsu. Lokacinda wata muhimmiyar matsala ta ratsa kwanya, wasu sukan keɓeta su yi tunani na musammam a kanta; wasu kuma ba sa yi, sai abinda kwanyar ta ba su don kanta. Wasu sukan yi tunani yadda yakamata, su kuma cimma amsoshi

na gaskiya waɗanda za su taimakesu wajen fuskantar al'amuransu; wasu kuma ba sa yin tunani yadda yakamata, sai su cimma amsoshi na banza waɗanda za su iya taɓarɓara matsalarsu. Bambancin yawancimu a zurfin tunaninmu da aiki da shi yake.

Tundayake, tunanin mutum shi ne yake gabatarda mutum, ashe ya zama tilas mutum ya nutsu sosai ya yi ta yin tunani mai zurfi a kan matsaloli masu muhimmanci tareda shi. Bambancin mutum da dabba, shi ne tunani. Bambancin mutum da mutum, shi ne *tunani mai zurfi*. Wanda ba ya yinsa, ko kuma ba ya yinsa a nutse, haƙiƙa, Nasara zata yi nisa daga gareshi.

A al'umma irin tamu, ci-gaban jama'a ya dakushe sosai ne saboda jama'a sun ɗauki tunani mai zurfi abune mai wahala, ko kuma abune wanda ba shi da muhimmanci, ko kuma abune sai 'wasu' ba 'ni' ba. Tunani shi ne maganin taɓewa, kuma ko al'amura ba su gyaru ga mai zurfin tunani ba, to kuwa zai iya tsinkayar wahalolin da ke gabansa, ya yi shirin tunkararsu kafin su zo, ko kafin lokaci ya ƙure masa. An ce, *Riga kafi ya fi magani."*

Amma, kaico! Wasu mutane sukan guji yin zurfin



tunani, wasu, don tsoron abinda zuciyarsu za ta fassara masu; wasu kuma don tsananin sakacinsu. Amma kuma, kowa ya san cewar matsoraci shi ne wanda zai kasance cikin ƙangin rayuwa, ya yi kane -kane cikin fargaba mai tsawaita wahala, har sai abinda yake gudun ya cimmasa. Idan kana son ka kasance *"Mai-Tunani"* toh, ka fara tunanin, kuma tunani mai-zurfi cikin gaskiya ba tareda tsoron abinda tunanin zai fassara maka ba. Idan *Kai da kanka, kai-kaɗai,* ka ƙi faɗawa kanka gaskiya, to waye zai faɗa maka? A lokaci irin wannan, kana da maƙiyi fiye da *kai kanka*? Ka tuna fa: *Ka fi kowa sanin kanka, kuma ba ka da aboki irinka. Asirinka naka ne.* In kana zaton akwai mai sonka fiye da kai, to kana cikin babban kuskure da ƙarancin hankali. Wanda bai san ciwon kansa ba, shi ke cikin hasara da nadama.

Mutum zai iya fara tunani a kan matsaloli ko abubuwa dabam-dabam, ba lallai sai waɗanda suka shafe shi tawwali ba. Ko a hira, ko a karatun jarida, ko wani Littafi (kamar wannan), ko a muhawara, ko radiyo, ko laccar malami ko ta wani ɗan siyasa, ko daga yadda shugabanni suke gudanarda wata matsala da masalaharta. Ga dai dama nan birjik a kewaye da kai waɗanda zaka iya yin tunani a kansu. A kullum tambayoyin su ne:

Ta Farko*: "Me ake nufi?"*(tunaninka)*;*
Ta Biyu: *"Gaskiya ne, ko kuwa?"*(bincikenka)*;*
Ta Uku: *"Ya za a yi?"*(amsoshinka).

Ya zama tilas ka yawaita waɗannan gameda kai kanka, da kuma abubuwan da suke kewaye da kai.

Dukkannin waɗannan suna da irin nasu amshoshin dabam-dabam, kuma ya rage sabon tunani mai zurfi ya auna komai a kan sikelin azanci da adalci, ya zaɓi wadda ta dace a halayyar ake ciki. Kowanne al'amari, ko wacce magana, ko wanne aiki, yana da manufarsa da sakamakonsa a kan waɗanda ya shafa. Idan tunaninka ya nuna maka cewar abu ya shafeka, kai kanka, ko iyalinka, ko ma Garinku da Kasarku, to, ba shakka akwai bukatar a yi sabon tunani da nazari a kansa. Idan ka yi biris da waɗannan al'amura, to wataran za a ba ka mamaki ma'illaci a gareka, watakila ma da iyalinka da kuma jama'arka, daidai matsayin rayuwarka. A inda ka san wayonka da hikimarka sun gaza ga samun amsar da ta dace, sai ka yi tambaya a gurinda ka tabbata za a ba ka amsa saboda Allah, ko da kuwa gurin ɗanka ne ko matarka, ko wani yardajjenka.

Babu abu mai daɗi da wanke zuciya irin tunani na

gaskiya, tsakani da Allah. Farin Tunani, wanda ya fi sukari zaƙi; kuma ya fi tuwo ƙosarwa. Ga araha, ga sakamakon alhairi. Mai tunani mai zurfi, shi ne mai nasara mai fadi.

15.
CIKA ALKAWARI

Ba sharri mai illata mutum da dangantakarsa da wasu irin rashin cika Alƙawari. Ba ƙazamin mutum, mara sanin yakamata, mara mutumci, mara tausayi, mara madafa a tareda shi, irin mutumin da zai ɗau alƙawari da sanin ba zai cika shi ba. Da mutanen kirki sun fahimci wannan illa a tareda mutum, to ba yadda za a yi su miƙa kayansu a gunsa, don ba zai iya ɗauka ba, balle ya sauke. Ba mai hasara irin mara cika alƙawari, kowanne iri ne alkawarin, balle na lokaci ko taimakon wani.

Da mara cika Alkawari ya ga an rubuta, "*Alƙawari Kaya ne",* sai ya karanta a hagunce yadda abin ya dace da mummunan halinsa: "Alƙawari ƙaya ne". Irin waɗannan mutane sam ba su san mutumcin kansu ba balle na matsayinsu ko muƙaminsu, in suna da shi. Har ga Allah (swt) su mutane ne waɗanda ba su san yakamata ba. A idanuwan jama'a su mutanen banza ne, komai muƙaminsu da

kuɗinsu; kuma maƙaryata ne, komai ilminsu; kuma mamugunta ne komai darajar da ake ba su; kuma macuta ne idan suka sami damar cutar. Me ake yi da mara cika alkawari. Amma, kash! Wasu da yawa sun ɗau wannan ɗabi'a. Can dai!

Idan ba za ka taimaki mutum ba, to kada ka ƙara masa wahala. "Jeka ka dawo" mugunta ce, in an san ba abinda za a yi in an dawon. Wanda ba shi da niyyar cika alkawari, to kada ya ɗauke shi, komai runtsi, sai dai in halaka ya gani. Amma, mutumin da zai zubda ta idonsa, ya dubi jama'a ya ɗau alƙawari, ya kuma ƙi cikawa da gangan, wannan mutum bai san mutumcin kansa ba, bai kuma damu da komai ba. Hasalima, mayaudari ne.

Tunanin irin waɗannan mutane, ba shakka baƙi ne ƙirin, kuma ba yadda za a yi su ci nasarar rayuwarsu sai ta zamba da ƙarya da hilata da yaudara da zubda mutumcin da ba su da shi.

Amma mutum mai cika Alƙawari, shi ne cikakken mutum har ga Allah (swt), domin wannan mutum ya san haƙƙi, ya san yakamata, ya san martabar waɗanda ya yi wa alƙawarin da abinda ya yi alƙawarin a kai. Mutane sun san shi, kuma sun san mutumin kirki ne shi, wanda zai iya riƙe amana da



shugabanci. Wanda ya san nauyin alƙawari, yake kuma cika shi, toh ya yi galaba a kan mummunan tunani, ya ci nasara tuni a rayuwarsa. Wanda zai iya cikawa wasu alƙawari, ba shakka, zai iya cikawa kansa alƙawarin tunaninsa da niyarsa ta fafutuka a kan duk irin burin da ya sa a gabansa. Daga wannan ƙarfin zuciyar alƙawarin, zai iya samun sabon ƙarfin tafiyarda al'amuransa, har ma da na wasu; ya kuma yi wa kansa jagora zuwa ga nasara a dukkanin abubuwan da ya sa kansa yi. Idan ya ɗau alƙawari sai ya cika shi, sannan zai san ya sauke nauyin da ya ɗauka. Sannan kuma hankalinsa zai kwanta. Wannan shi ne mutum!

Ba yadda za a sami rago a cikin masu cika alƙawari; kuma rago ba zai iya kasancewa a cikinsu ba. Ɗaukar nauyi da sauke shi, ba shakka, aiki ne na jarumai, waɗanda zuciyarsu ta ɗau manufarsu da ƙarfi, tunaninsu kuma ya duƙufa wajen ƙara himma a kan turbar cimma wannan manufa, har sai an kai gaci. Nasarar rayuwa, ba shakka, ta tabbata a gareshi, duk wanda ya ɗau ɗabi'ar cika alƙawari a lokacin cika shi.

Cika alƙawari yana daga bin Allah (swt), kuma ba ƙaramar ibada bane. Mai cika alƙawari, shi yake iya tsaida ibada, fisabilillah, ba don ganin ido ba;

ba kuma don kawai haka ake zato daga gareshi ba. A gareshi, cika alƙawari ruwa ne da yake gudu a cikin jininsa. Duk mai son mutumcinsa ya tsira, nasara ta tabbata a rayuwarsa, to lallai ya wanke zuciyarsa, ya kuma ƙarfafa tunaninsa a kan hanyar cika Alƙawari.

16.

MASLAHA DA GAFARTAWA

Riƙe mutum a zuci da ƙin gafartawa wanda ya aikata maka laifi, sun fi laifin da aka aikata azaba. Wannan abu haka yake domin sai ka tarar ka fi tunanin ƙullatar mutumin fiye da yadda ka ke tunanin laifin da ya aikata. Maganin wannan baƙin cikin shi ne kaɗai mutum ya sabunta tunaninsa ya ɗau ɗamarar gafartawa da neman maslaha. Mafi muni kuma shi ne tunanin 'maida martani', watau ka ƙudiri niyyar sai ka rama.

Ramuwar Gayya tana ga Allah (swt) domin Shi yakamata ka miƙawa kukanka gameda haƙƙinka da aka taka da gangan domin a ƙuntata maka, ko tozartaka, ko a ci maka mutunci. Idan ka shige gaba ka ce kai ne mai ramawa, to wataran sai ka yi da-nasani. Amma idan ka haƙura ka barwa Allah (swt) sakayyarka, to ba shakka kai ne mai nasara ko badaɗe ko bajima.

Ga bayani mai sauƙi:

Idan wani ya cuceka, sai ka ce sai ka rama irin wannan cutar, toh take a nan ka aikata miyagun abubuwa biyu: Da farko dai ka cire Allah a cikin al'amarinka, sannan kuma kai ma ka zama macuci. Idan ka cire Allah a cikin al'amarinka, ka ce kai ne za ka karewa kanka, toh idan wanda ya cucen naka ya fi ka ƙarfi ko iko ko galihu, toh nan take zai sake cutarda kai. Dalilin kuwa mai sauƙin fahimta ne: domin babu adalci a cikin tsarin; domin an cire Allah (swt) daga cikinsa. Toh, amma, idan ka barwa Allah (swt) sakayyarka fa? Waye ya fi Allah ƙarfi ko iko ko galihu? Ai ka ga a wannan hali, lallai za ka sami cikakkiyar sakayyarka ta hanyoyi uku. Da farkon fari, sai Allah (swt) Ya mayar maka da duk abinda ka rasa daga waccan cutar ta hanyoyi iri iri; sannan kuma in ka zuba ido, a hankali za ka ga yadda wanda ya cucen naka zai zama. Ta ukun kuma, ká adana lokacinka wajen yin wasu abubuwan dabam na alhairi.

Mutum mai iya gafartawa shi ne kuma mai iya neman gafara da maslaha a tsakaninsa da duk wanda ko waɗanda wani abu na rashin jin daɗi ya wakana a tsakaninsu. Lallai ne mutum ya kimtsa tunaninsa a kodayaushe wajen yin la'akari da

rashin kyautatawarsa ga mutane ko menene ƙaskancin rayuwarsu a idanunsa. Kada mutum ya manta cewar a gurin Allah (swt) kowa muhimmi ne, musammam kuma masu taƙwa. Ko almajiri ka zaga cikin fushi don ya nace yi maka bara, toh ba shi haƙuri, ko ka dawo ka ba shi sadaka da niyyar ita ce haƙurin da ka ba shi. Ya zama tilas ga mumini ya san cewar Allah (swt) a tsarin adalcinSa ba Ya yafe laifin da aka aikatawa wani. Sai ka yi ta ibadarka kana ta samun ladanka, amma duk ka zagwanye shi da haƙƙin jama'a a kanka.

Duk mai la'akari ya san wannan; ya san kuma babbar ɗabi'arsa ta farko ita ce 'kiyayewa'. Ta biyu kuma 'neman gafara' da 'maslaha' idan ya yi kuskure ga waɗanda ya yi wa kuskuren. Ba ƙaramin jarumi ne shi ba, wanda ya duƙufar da kansa ya nemi gafarar waɗanda ya aibanta. Haka kuma, ba ƙaramin mai dabara ne shi ba.

Duk wanda ka yi wa laifi, ko wanne iri ne, ka kuma zama jarumin da zai je ya nemi gafara ya kuma sulhunta, to ba shakka ka sami zaman lafiya da kanka, ko da ba a gafarta maka ɗin ba. Allah (swt) Yana sane da kai da niyyarka, kuma Ya san abinda Zai yi a kan wannan al'amari naka. Ba mutumin banza a idanun Allah (swt) irin wanda

aka nemi ya gafarta ya ƙi, ko kuma ya kasance mai saurin maida martani don ramar-gayya. Irin waɗannan mutane in ka lura za ka ga ba su da madafa a rayuwarsu, domin ba za su sami gafarar Allah (swt) ba; domin ba su yi koyi da Shi ba; ba su kuma yi koyi da ManzonSa ba. Ka gafartwa wanda ya yi maka laifi, alabarshi ka nisance shi, in har ka tabbata yin haka shi ne mafi alhairi a gareka.

Kai dai adana zuciyarka, ka tserarda ita daga sharri ko ƙulla shi; ka nesantar da ita daga rashin haƙuri ko ramuwar gayya. Lallai ka zama mai neman maslaha a rayuwarka. Kada ka yarda ka riƙe mutune a zuciyarka, ballantana ka kafa wasu a muƙamin maƙiyanka. Duk masu ƙiyayyar da sharrin da hassadar da muguntar da sauran irin waɗannan baƙaƙen tunani, haƙiƙa, su ne cikin azaba da nadama a rayuwarsu. In kana cikinsu ka san haka. In ba ka cikinsu, ba ka san haka ba. Wannan ita ce babbar shaida, wadda kowa zai iya bincika zuciyarsa don ya fahimta ya kuma gyara tunaninsa a kansa da kan wasu.

17.
RIKE SIRRI

Riƙe sirri alama ce ga mai iya yinsa cewar yana da

adanannar zuciya, wadda ta kimtsu, ta nutsu, ta san abubuwan da za ta haɗiye da waɗanda za ta tofar. Zuciyar da ba ta san waɗannan ba, almubazzara ce; wataran sai ta rasa komai na kanta. Mai irin wannan zuciya yana cikin haɗari.

Da muke cewa, *'Wanda ya rufa asirin wani, Allah zai rufa nasa',* ai matashiya muke yiwa kanmu ga muhimancin sirri, musammam ma idan aka ba ka amanarsa, ko kuma ya kasance dole ka adana shi don kada kai, ko wani ya lahantu. Kishiyar waccan magana ita ce, *duk wanda ya tona asirin wani, Allah Zai tona nasa'.* Daga wannan magana za mu iya fahimtar cewar ashe idan ka tona wani asiri a kan rashin cancanta har ta kai aka shiga cikin wata wahala saboda hakan, ashe kai ma wataran kana tafe zuwa ga wannan wahalar ko ma wadda ta fita. Haka, kuma ana cewa, *"In za ka haƙa rami, haƙa shi gajere"*, saboda ko wataran za ka faɗa cikinsa.

Mutane biyu su ne aka fi sani da tonon asiri: Da Wawa da Mamugunci. Wancan don bai san abinda yake yi ba; wannan kuma don sharri. Amma kuma lallai ne mutum ya san da wa yakamata ya yi magana; wa yakamata ya bar wa sirrinsa; a ina yakamata ka yi, ko ka ce, abu-kaza? Wanda bai adana sirinsa ba, to shi ya jawowa kansa. Ashe



maganar sirri, magane ce mai gefe biyu. Gefen da ya fi muhimmanci shi ne gefen mai sirrin; sannan gefen wanda ya san wannan sirrin ta wata hanya. Shi kansa sirrin kuma iri biyu ne: Da sirri mai kyau da mai muni. Sannan kuma akwai sirri wanda sai an faɗa za a gane shi, akwai kuma wanda sai an aikata wani abu za a iya gane shi. Mu ƙara tunani a kan wannan.

Idan ka ji wani yana ƙulle-ƙullen cutar wani, ko aikata wani sharri dabam wanda zai illata wani ko ya kawo wata rigima ga wasu ko ga Kasa, lallai ka auna da kyau ka san abinda za ka yi gameda wannan sirri. Idan abinda za ka iya hanawa ne, toh maza hana. Idan wanda za ka iya tonawa ne don al'umma ta sami maslaha, toh maza tona. Amma idan mutum yana da sirrinsa na kansa, ko da wani abin kunya yake aikawa tsakaninsa da Allah, toh rufa masa asiri, ko ka ba shi shawarar ya daina, in za ka iya. Baza shi a kasuwa cewar shi ne mai aikata kaza da kaza a ɓoye ba shi ne maslaha ba, sai dai in ka ga yana neman jan mutane a Sallah, ko neman wani shugabanci wanda bai dace da masu irin waɗannan aƙidu ba. Idan azzalumai suna neman wanda suke son zalunta, shi kuma ya ɓuya a wani gu, toh kada ka nuna makwancinsa. Duk wanda ya san ka san asirinsa, ya kuma roƙe ka don

ka rufa masa asirin, to yi ƙoƙari ka rufa masa.

Yawancin abubuwa da shirye-shirye muhimmai a cikin sirri ake tsarasu. Wanda ya fallasa su ya doshi hanyar tarwatsa su. Inda babu sirri a kan abubuwan da suka cancanta a asircesu, toh babu nasara cikakkiya a tareda su. Haka kuma duk inda surutu ya yi yawa, toh ba shakka sirri zai yi kaɗan. Guji hirar sirrinka da mai surutu da kuma wanda ya faɗa maka sirrin wani. Guji fallasa asirinka ga waɗanda ba ka amince da su ba, ko mecece bukatarka. In a gun Allah (swt) ka ke nema to tuni ya san sirrinka, ba sai ka tonawa wani ba.

Yawancin masu tona asiri mahassada ne, kuma ba za su iya riƙe amana ba. Lallai ne mu yi la'akari da wannan, mu kuma san su waye abokan hira; su waye abokan yawo; su waye abokan kasuwanci ko wata mu'amala; su waye kuma abokan sirri. Wanda ya iya rarrabe mutane haka, shi ne zai ci ribar rayuwarsa asirinsa a rufe.

Duk wanda ya ji sirri, toh ba shakka babban aiki ya same shi. Lallai ne wannan mutum ya zauna ya yi tunani a kimtse domin ya san wanne irin sirri ne wannan, kuma ya zai yi da shi? Da ya tsaida shawara, toh lallai ne ya yi tunanin ita shawarar, ya

sake tankaɗeta da rairayeta har sai ya tabbatar ita ce wadda ta dace, sannan ya yi maza ya aikatata.

Da mai tona asirin da bai kamata a tona ba, da mahassadi da munafuki, duk launinsu ɗaya. Mutane ne waɗanda nufaƙarsu ta cinye zuciyarsu.

18.
TALLAFAR IYALI

Tsarin rayuwar al'umma gaba ɗayanta ya ginu ne a kan iyali, kuma tallafar iyali aikin karɓa-karɓa ne. Watau, wannan ya karɓa ya ba wa wancan daga zuri'a zuwa zuri'a. A inda duk zaren tallafar ya tsinke, to zuri'a ɗinkakka ta yage.

Ya zama wajibi jama'a su fahimci muhimmancin wannan gini na iyali da zuri'a, su kuma san menene matsayinsu a wannan bango, watau wanne tubali ne su. Idan mutum ya san shi ne tubalin ginshiƙin bangon, to lallai kuma ya san cewar idan ya goce bango ya tsage, ko ma ya ruguje. A tarayyar iyali, lallai duk dangi su san cewar '*tsintsiya ɗaya ba ta shara'*, domin ta sanin hakane kaɗai za su iya tallafar junansu, su kare iyalinsu da zuri'arsu daga watsewa. Lallai ne kowa ya taimakawa ginshiƙin

bangon nan ta yadda kowa zai iya, kuma lallai ne su yi shirin '*in ba wane akwai wane*', domin rufin asirinsu yanzu da kuma gaba. Idan suka ƙi taimakawa juna, ko suka yi sakacin fahimtar magaji, toh kuwa su san cewar daga lokacin da ginshiƙin ya kasa, toh daga wannan rana wahalu za su fara sallama, sai dai kuma wani taimako na Allah (swt) a dalilin da Shi Ya fi kowa sani.

Mutane da yawa ba sa sa muhimmancin iyalinsu a cikin tunaninsu na yau da kullum. Su kan manta cewar iyali, musammam ma na kurkusa, watau, na aure da 'ya'ya da iyaye da yayye da ƙanne, su ne babban nauyin da yake kawunansu. Sai sun sauke waɗannan haƙƙuna tukuna, sannan za su iya ɗaukar sauran 'yan'uwa, sannan kuma wani a waje. Amma sai ka ga wasu, sai wajen ta ƙoshi tukuna, sannan za su kawo sidi gida. Sai ka ga wasu sun yi watsi da matansu, ko 'ya'yansu ko ma iyayensu, suna ta hululu da waɗanda ba su kamata ba. Sai ka ga wasu sun ginawa maroƙi ko karuwa gida, ko sun sai masu motoci, amma ga iyayensu da matansu da 'yan'uwansu duk cikin wahala. Sai ka ga wasu tunaninsu tamkar na dabba.

A tsarin rayuwa, tallafar iyali tana da muƙami mai girman gaske. Lallai ne a yi tunani mai haske a kan



wannan. A cikin iyali kimtsattse, ba a jin labarin jahilci ko fatara ko rashin aikin yi, domin jama'ar wannan iyali sun ba wa zuri'arsu muhimmanci, sun haɗa kansu ga taimakon juna daidai yadda za su iya, kuma kowa daidai ƙarfinsa. Fafutukarsu a kodayaushe ita ce su san yadda suka rufawa kansu asiri, suka ɗauki ɗabi'u da al'adu waɗanda za su tabbatar masu da mutumcinsu. A irin wannan iyali ake samun na-gaba wanda idan ya faɗa za a saurare shi, ba don shi ne mai-kuɗi ko wanda ya fi kowa ilmi ba. A a, sai dai don shi ne babba, ko kuma wanda ya fi dacewa a cikinsu. A cikin iyali irin wannan kowa ya san matsayinsa da duk abubuwanda ake bukata daga gareshi. A cikin iyali irin wannan rufin asirinsu gaba ɗaya da kuma ingantar kowannensu su ne babbar manufa.

Duk wanda ya salwantar da iyali, ya salwantar da babban haƙƙi. Duk wanda ya tallafi iyali daidai ƙarfinsa, to ya tallafi babban haƙƙi yadda Allah (swt) Yake so. Irin waɗannan mutane masu son iyali, masu kula da zuri'arsu yadda za su iya, ba za su taɓe ba har abada abadun, domin Allah (swt) Yana tareda su a kodayaushe. Jama'a ma sukan yi sha'awar masu zumunci da tallafar iyalansu.

Kuskure ne ƙasaitacce, mutum ya ringa tunanin

hasara wajen taimakon iyali, domin jarin da yake cikinsa ya fi na kowacce irin sadaƙa. Sannan ga shi ta nan ake samun ɗaukaka, zuri'a ta ginu, gari ya ginu, ƙasa kuma ta ginu, kowa ya ci riba.

19.
IMANI DA ALLAH (swt)

Masu imani da Allah ne kaɗai za su ci riba biyu: Ta duniya da ta lahira. Tuni dai mun gamsu da cewar nasarar da za a samu a duniya a cikin tunani ake shirya samunta. Tundayake kuma daga duniyar ake shirya lahirar, ashe wancan tunanin nasarar na farko shi ne maƙasudin komai.

Imani da Allah (swt) abubuwa uku muhimmai ya ƙunsa. Na *farko* ka yi imanin cewar Shi kaɗai ne, kuma babu wani abin bautawa sai Shi kaɗain. Na *biyu*, ka yi imani da duk abinda a haƙiƙa Shi ne ya faɗesu da waɗanda suka kawo saƙon. Na *uku* kuma, ka aikata duk umarninSa, ka kuma bar duk abubuwan da Ya hana. A cikin waɗannan ukun za mu ga cewar komai ya shigo. Shiriyarmu da shari'armu, duk sun shiga mazauninsu. Amma, sai tunani ya kimtsu ya karɓesu sannan za su sami gurbi a cikin zukatanmu; sannan ne kuma za mu iya zama kimtsatstsu mutanen kirki waɗanda suka

san yakamata, suke kuma da tsari na alhairi.
Tushen komai, musammamma ‘nasara’ daga imani da Allah (swt) yake. Wanda ba shi da wannan imani a zuciyarsa, ba shakka, ya yi babbar hasarar rayuwarsa ta duniya; tuni kuma ya rasa damar kimtsa ta lahira. Mai imani ne kaɗai ya san haƙƙin wasu, ya kuma san dukkanin nauyin da yake kansa ko menene matsayinsa, jin daɗinsa da wahalarsa. Shi ne ya san muhimmin aikinsa a wannan duniyar bai shige gina lahirar ba.

Mai imani da Allah (swt) ne kaɗai yake iya daurewa fitinu da masifu in sun zo; ya sarrafa kuɗinsa da talaucinsa cikin arziki. Irin wannan mutum shi ne mai fahimtar duniya a matsayinta na ‘tasha’ ce mai ƙarancin lokacin jira, domin ya san shi matafiyi ne daga wani gu wanda bai sani ba zuwa wani gu dawwamamme, wanda ya sani.

Mai imani ne kaɗai ya ke la’akari da duk waɗancan shawarwari goma sha takwas na baya, ya ke kuma iya sarrafa tunaninsa saboda Allah.





9



Tunani da Nazari

"Kukan Kurciya ma Jawabi ne ...."

"Duk wanda ya fahimci bambancin da yake tsakanin kwano da abinda yake cikinsa, toh ya sami isasshen ilmi"

Wannan Magana ta sama lallai abar bincike ce, domin tana ƙunshe da bayanai masu zurfi. Maganar, ita kanta, ta fidda zato ce, ko kuma tana fahimtarda mu ne yadda a al'ada aka fahimci wasu abubuwa, aka kuma riƙe ra'ayi a kansu ba tareda zurfin nazarin da zai tabbatarda hakan ba. Tankaɗe abubuwa da rairayesu, suke sa a fahimcesu a kuma san yadda za a yi da su. Ba kowaɗanne kwanuka ne

suka dace da ɗaukar abinci ba; wasu na ado ne; wasu kuma na zuba furanni ne; harwayau, wasu na ɗaukar shara ne. Don haka bai kamata a ba wa kwano fassara ɗaya ba don shi kwano ne, ba tareda an nazarce shi ba. Ashe, 'Kwano' a nan yana nufin abubuwa da yawa.

Daga tunani irin wannan za mu ga: ba kowanne mai kuɗi yake da arziki ba; ba kuma kowanne malami yake da ilmi ba. Ba kowanne Kare ke cizo ba, ba kuma kowacce dabba ce kidahuma ba. Ba kowanne sarki ke mulki ba. Ba kowanne wuridi yake ibada ba. Kamar yadda ba kowacce dariya take bayyana jin daɗi da bushaha ba. Wata dariyar ta ƙeta ce, kamar yadda wani kukan yake na jin daɗi. Wani a wuridinsa sharri yake neman ƙullawa, wani kuma kuɗinsa yake ƙirgawa da 'ya'yan carbin. Wani Karen haushi kawai ya iya, wani kuma na wasan yara ne. Sai an nazarci kowanne abu tukuna, sannan za a san haƙiƙaninsa. Sannan za a san ko menene shi.

A nazarin halayen mutane, shin, za mu iya cewa kowa yadda ake zatonsa, ko yadda ake zaton an san shi, haka lallai yake? Shin ma wai, za mu iya zuba al'umma a kwano ɗaya mu ce duk haka suke don kawai ana yi masu take haka? Ko kuwa za mu



iya cewa nama daɗi gare shi a bakin kowa? Ko duk sarki mai alfarma ne, duk talaka kuma ƙuntatacce? Ba shakka, zai zama wawanci mu zuba mutane ko wasu abubuwa a kwano ɗaya, mu ce duk daidai suke, domin duk a cikin kwano ɗaya suke. Shin zai zama hankali mu ce halayen duk 'yan-tagwaye ɗaya ne ta ko'ina muka aunasu, ko da kamaninsu iri ɗaya ne ta kowanne gefe muka duba su? Menene bambancin mahaukaci da mai rawa ba kiɗa? Menene bambancin siliki da alawaiyo?

Yadda kwanuka suka bambanta, haka mutane suka bambanta. Kai, ko a dabbobin ma, akwai masu hankali irin nasu, ba dukkaninsu ne kidahumai ba. Iya bambance abubuwa, tankaɗesu da rairayesu, ba ƙaramin ilmi bane. Amma wannan aiki ne na masu haƙurin nazari waɗanda suka san muhimmancin bambance abubuwa. Ko a fahimtar halayen mutane, sai ka ga abinda ya dace da wani bai dace da wani ba. Abinda wani ya ɗauka da muhimmanci, sai wani kuma ya banzartarda shi. Haka, in ba ka lura ba, sai ka ɗauki mutum mai kirki ka sa shi a matsayin da za ka ga rashin kirkinsa; ko ka ga mutum fes fes da shi, amma ba ya wanka, watau a fuska kawai tsabtarsa take. Da ya tuɓe, sai ka ga dauɗa ko ma kirci a ƙirjinsa. Kamar dai ka ga miciji ne, nan da nan ka shara da gudu ba ka san wan-

nan micijin baya sara ba. Ko kuma ka fahimci murmushin wani tamkar alama ce ta kirki, nan kuwa gani ya yi za ka faɗa rami. Ba shakka akwai fuskoki masu murmushi a fili, amma turɓunannu a zuci. Wasu a hannun gaisuwarsu kunama suka ɓoye. Wasu a hirarsu ta yabo, munafurci suka ƙulla. Abubuwa ba kodayaushe suke yadda ake ganinsu ba. Sai a duba a hankali.

Wani ba za ka san iya aikinsa ba, sai ka ba shi damar yin aikin. Ba za ka san ƙwazo da hikimar matarka ko ɗanka ba, sai ka amince masu da wata hidima daidai su. Idan ka bar matarka a ƙulle, ko ‘yarka a dankwafe, to har abada ba za ka iya saninsu a ainihin yadda suke ba. Haka ba za ka san yadda zamanin gaba zai yi watsi da su ba, domin watakila ba ka nan. Wasu matan, mata ne kawai a siffance, amma zuciyarsu da ƙwazonsu sun fi na maza. Wasu mazan kuma mata ne ta kowanne gefe ka dubasu, illa a kayan sawarsu. Toh amma, ta yaya za ka san haka, idan ba ka yi nazarin kowa ka ba shi damar da yakamata a san ko waye shi ko ita ba?

Dáma ba ƙaramin ‘yanci take haifarwa ba. Kuma sai da ‘yanci za a san ƙokarin mai shi. Kamar dai Uba ne, ko Shugaba, wanda ya takura ɗansa ko



jama'arsa domin su yi biyayya a gareshi. Toh, zai sami biyayyar, amma fa ba ta soayya ba, sai dai ta tsoro. Daga ranar da tsoron ya fice, Uban ko Shugaban, sun shiga uku; sai juyin juya hali. Ko da ga Allah (swt) ne, ba tsoronSa Yake so ka ji don Zai iya azabtaka ba. Haka, ba biyayyarka Yake so don Zai iya ni'imtaka ba. Allah (swt) Ya fi so ka so shi da soyayya ta gaskiya, ko a ina Zai sa ka.

Don haka, tsoro kaɗai ba shi ne siffar mumini ba. Soyayya ga Allah ita ce siffar. Idan ka tsorace Shi don Yana da Wuta, toh a gaskiya Wutar ka ke tsoro ba Shi ba. Idan ka bi Shi domin Yana da Aljanna, toh a gaskiya Aljannar ka fi so fiye da Shi. Da Bai yi maka zancen Aljannar ko Wutar ba fa? Lallai a yi tunani mai zurfi a kan wannan domin a iya bambancewa. Wanda yake sonka da gaskiya, ba zai keta haddinka ba; ba zai ɓata maka da gangan ba, ba zai ci maka amanarka ba, ba zai yi abubuwan da ba ka so ba. Amma mai tsoronka, yana gudun azabarka ne kawai. Shugaban da ake tsoro sai a bi shi sau da ƙafa, da ya kau sai zagi, domin dama can ba sonsa ake yi ba. Shi kuma bai iya bambancewa ba. Wasu abubuwa fa ba yadda suke ake ganinsu ba. Ladabtarwa ta hanyar tsoratarwa ba ta ƙarko, amma ta hanyar soyayya sai ta kafa tushe mai ƙarfi, furanninta su yaɗu nan da nan. Lallai a bam-

bance biyayya don tsoro da biyayya don soyayya, sannan a duba hanyoyin da za a gina abinda zai yi ƙarko. “Tsoron Allah”, na soyayya da biyayya ne.

Malamanmu masu bulala a hannunsu, cin zalin yara kawai suke yi, domin idan da za a auna nasarorinsu na ladabtarwa a ma’unin kimiyya, ba abinda za a samu na gamsarwa. Irinsu ke sa yara su zama taƙadarai ko ma daƙiƙai. Yara suna son a nuna masu soyayya, a kuma faɗakarda su amfanin ilminsu domin su maida hankali cikin sanin abinda ya dace da su. Ta haka za su zama masu biyayya da ƙoƙari a duk inda suke, domin sun san su za su fi kowa cin amfanin biyayyarsu da ilminsu. Haƙiƙa, ladabtarwa in ta zama tilas, sai a yi ta. Wanda aka ladabtar ɗin kuma ya fahimci dalilinta da dacewarta domin ya guji maimaita rashin ladabinsa, ko halayensa na banza.

Iya bambance abubuwa da aza komai a mazaunin da ya dace da shi ba ƙaramar hikima bace. Ko da kai ne da kanka, ka iya auna kanka daidai, ka nazarci kanka daidai, ka fahimci kanka daidai, to ba ƙaramar ribar rayuwa za ka samu ba, don ka san yawancin abubuwan da suka dace da kai. In kai mai nauyi ne, ba za ka shiga layin masu tsalle ba, balle ka ji kunya. Amma, idan aka ce ‘danne min



nan', ka san da kai ake, kuma in ka danne ɗin ba za a ɗaga ba. Wannan magana muhimmiya ce ko da a wajen auna matsayinka, damarka da mutumta-karka. Haka, ta hanyar nazarinka, al'umma ita kanta za ta iya aunaka.

Misali: Idan a sikelin cikar mutum, watau, **Ingancin** mutum, akwai abubuwan dubawa waɗanda kowanne yana da nasa awon. Idan a ce maƙurar inganta ita ce a inda aka sami awon waɗannan abubuwa sun cika 100 bisa 100, to ashe lallai ne a binciki kowanne daga cikin waɗannan abubuwa domin a ga awo nawa suka bayar a cikin ɗarin. Idan a misali, a awon **Inganci**, aka ce:

'*Gaskiya*' tana da awo 20 cikin 100; '*Ilmi*' da amfani da shi' yana da awo 15; '*Yakana*' tana da awo 15; '*Kyauta*' tana da awo 10; '*Tausayi*' yana da awo 10; '*Biyayya*' tana da awo 10; '*Son jama'a da murmushi*' suna da awo 10; '*Iya aiki*' yana da awo 5, duk sauran suna da awo 5; to ai ka ga za a iya cewa jimlar ingancin wane ya kai awo 40 ko 60 cikin 100, ko dai yadda aka fahimce shi aka kuma auna shi da ƙiyasin hikima da adalci. Shi kansa zai iya yi wa kansa wannan awon fiye da kowa, ya kuma gyara ingancinsa yadda ya dace, in dai shi mai ƙaunar kansa da gyara ne.

Amma fa duk waɗannan, mutum ya iya sirkawa yadda ya ga dama a guraren da ya ga dama, kuma a fahimce shi a hakan in ba a yi nazari mai zurfi ba. Wani ya surka daidai, wani kuma ya surka a kuskure. Waɗanda suka surka da hikima, kuma saboda Allah domin su inganta kansu, sai su sami yabo ta kowanne gefe aka duba, kuma asirin halayensu ba zai tonu ba domin babu wani kuskure.

Amma waɗanda suka ƙi duba kowanne ma'auni yadda ya dace domin su inganta kansu, sai ka ji ana cewa, 'kai wane da gaskiya yake, sai dai rowar tsiya'. Ko kuma a ce, 'akwai iya aiki, sai dai rashin tausayawa'. Wasu ma ka ji an ce, 'me za a yi da wane? Wannan kirkin da murmishin duk na banza ne, in ka ba shi amana, sai a lahira'. Wani a unguwarsu, sai ya kasance mai inganci da yawa a gun 'yan-unguwar, amma da ya bar gurin, sai ya ɗau ɗabi'arsa ta ainihi. Idan 'yan unguwar suka gan shi a wannan gurin, sai ka ji suna cewa, 'anya kuwa wane ne?' Ko, 'ashe haka wane yake?' Ashe dai yadda suke zaton sun san shi ba haka yake ba, domin ba su yi nazarinsa da zurfi ba.

A duk waɗancan awon, babu hidimomin addini da ibada a cikinsu, domin muna zancen fahimtar mutum ga mutum ne kawai. Idan muka kawo addini



da ibada, to wa zai iya ɓoyewa Allah (swt) ainihin kammaninsa? Ko kuma wa ya san abinda mutum yake yi a bayan ƙasa? Duk ibadarka, Allah (swt) Ya san ko waye kai. Sai dai ka burge mutane waɗanda ba su san sirrinka ba. Idan mutane suka ce za su yi awo ne da ibadarka, to sai su bi ka duk inda ka ga damar kai su don yawan ibadarka; ko su kauce maka duk ta inda ka ja su, don ƙarancin ibadarka. Amma ba a nan take ba. Wa ya san abinda ka ke yi a asirce saboda Allah? Wa kuma ya san abinda ka ke yi a asirce saboda Iblis? Haƙiƙa, wanda aka sani da ibada, akwai alamun mutumin kirki ne shi ko ita. Amma a nan awon ya tsaya.

Mutane za su fi fahimtar mutum idan suka auna ɗabi'un da suka san shi da su tun farko, suka ajiye addininsa da yawan wuridansa sai daga ƙarshe. Daga awon ingancin ɗabi'unsa kaɗai ma, sai su fara samun shaida ko addinin nasa na gaskiya ne ko kuwa na bilhu ne. Idan suka ɗau yawan ibada da farko, to za su yi mugun kuskure, domin sai su fara amincewa ingantacce ne tun ma kafin su auna ingantar tasa. Ta haka sai su ɗora mutum a matsayin da bai dace da shi ba, domin ba su san shi ba. Abinda suke zato ba haka yake ba. Kamar dai a kama liman ne da kwartanci, ko sarki da kwalabe. Ko ba a kama su ba, idan waɗannan halayensu ne,

toh ba su cancanci limancin da sarautar ba. Amma tunda ba lallai ne duk mutane su san waɗannan ɗabi'u nasu ba, sai su yi ta binsu cikin rashin sani. Wasu limaman ba su dace da ko sharar masallaci ba; wasu sarakunan kuma ba su dace da zama dogarai ba; wasu shugabannin ko kaɗan ba su dace da muƙamansu ba. Amma kaico! Haka yawanci ake tafiya da ka, saboda rashin sani ko ƙin bincikawa, ko tsoro, ko kwaɗayi, ko wani abu dabam.

Akwai waɗanda in sun zo auna inganci, sai su ba wa dukiya ko kuɗi muhimmanci a awonsu, su ce dukiya ko kuɗin suna da awo 20 ko ma 30, ko dai yadda kuɗi suke da muhimmanci a cikin al'ummarsu. Wannan al'umma ba ta kirki bace. A al'ummar kirki, sai an yi amfani da kuɗin ko dukiyar tukuna, sannan za a san a ina za a sa su. In ba a yi amfani da su ta hanya mai kyau ba, to suna cikin abubuwan da ake tsarawa a awon rashin inganci, domin kuɗi sukan iya jefa mutum cikin hanyoyi na rashin mutumci waɗanda suka dace da la'anta. Ko Zakka aka tabbatar ka ƙi fitarwa da gangan, toh ka cancanci a la'anceka. Zakka tana daga sashen addini, amma 'taimako' yana sashin al'adu nagari, kuma mutane za su iya auna shi. Don haka, duk abubuwan da suka shafi addini, sai a ajiye su gefe guda da farko, domin a fahimci mutum sosai.



Haka kuma, abin a ce: A awon **Munanci** misali: '*Karya*' tana da awo 10; '*Munafurci'* yana da awo 25; '*Jahilci*' yana da awo 10; '*Rashin Yakana*' yana da awo 10; '*Rowa*' tana da awo 10; '*Keta*' tana da awo 10; '*Rashin Kunya*' tana da awo 10; '*Kin jama'a da saurin fushi*' suna da awo 5; '*Lalaci*' yana da awo 5; duk sauran suna da awo 5.

To ka ga ashe, za a iya cewa 'Munancin wane ya kai awo 50 ko 60' a yadda mutane suka fahimce shi, suka kuma auna shi da hikima da adalci. Haka kuma ya iya sirka waɗannan ma'aunai yadda yake so a guraren da yake so. A inda aka san shi, sai a yi watsi da shi a siffarsa ta mutumin banza. A inda ba a san shi ba, sai ya ci da buguzun har sai lokacin da ya fallasa kansa, ko kuma masu haƙurin nazari suka fahimce shi. Dá ma an ce, "*Munafunci dodo ne, yakan ci mai shi*". Saboda haka, duk yadda ka sirka waɗannan, ba yadda za a yi ka fiddo da kanka illa a mutumin banza. Ba shakka, mutum mai da-bara, shi kansa, zai iya yiwa kansa wannan awon fiye da kowa, ya kuma gyara ingancinsa yadda ya dace, idan shi jarumi ne mai son ingantuwa da kuma karɓuwa a cikin jama'a.

Marasa mutumci za su iya shiga rigar mutumci nan da nan ba tareda wahala ba, amma ta ɗan lokaci

ƙanƙani, don neman biyan wata bukata, ko don wani dalili. Amma, mai mutumci ba zai iya shiga rigar rashin mutumci ba ko menene dalilin, ko da ta lokaci ƙanƙani, domin ba za ta taɓa dacewa da shi ba. Da ya ganta, sai ya ƙyameta, ko da kuwa da mayanin siliki da zaren dinare aka ɗinka ta. Masu haƙurin nazari ba sa samun wahalar bambancewa tsakanin masu inganci da marasa shi, kowacce irin riga suka sa. Haka kuma duk yawancin abubuwan da za su zo gabansu, nan da nan za su iyar fahimtar yanayin abin su kuma yi magana ta hankali a kansa. Su ne suke iya fallasar marasa mutumci ko da sun zo a rigunan mutumci. Su ne kuma suke iya gane mai nutumci, ko da a cikin tsumma yake. Amma a al'umar marasa mutumci, 'yan iska suke tashe, kuma su ne shugabanni domin yawancin jama'ar sun ƙi, ko sun kasa bambance halayensu; sun ƙi sa su a cikin ajijuwan da suka dace da su. Wannan kuwa, domin halayensu kusan ɗaya. Don haka, suka kasa fahimtar bambancin wahalunsu da irin shugabancin da suka amince da shi.

Algus da sauran ha'inci ko waɗanne iri ne, har da na halaye, suna daga cikin miyagun ɗabi'un da ake illatar mutane da su. Akwai masu yin algus a maganganunsu da harkokinsu, sai ka rantse su ne daidai, ka kuma halaka wajen amfani da su a gaba.



Sai ka ji wasu na wa'azi a cikin abokansu ko a wata walima in an gayyacesu, amma duk ɗabi'un kirkin da suke magana a kai, ba halayensu bane. Sai ka ga mace mai tsarin siffa, ashe duk kayan kanti ne. Sai ka ji an ce 'Galadima ya zo', ashe galadiman 'yan banga ne. Ko ka ga agogo kamar mai tsada, amma na giri ne. Ga dai misalai nan barkatai. Wani mawaƙi mai hikima, Jan-kiɗi, yana cewa, *"Holoko hadirin Kaka, duba shi da kyau duba ka gani…"* Watau, ga hadiri ya kai hadiri, amma babu ruwa a cikinsa. In aka daka ta tasa sai dai a mutu da yunwa. Wasu kuma ka ji magana tiryan tiryan har da rantsuwa a cikinta. Amma kuma, *'mafi rantsuwa mafi ƙarya'*. Haka za ka yi ta tararwa ga mutane masu yawan gaske, har da wasu malamai da sarakuna da shugabanni da masu kuɗi da 'yan kasuwa da ma'aikata da 'yan siyasa. Yawancin rigunan da suka sa ba su dace dasu ba. Amma mutane sun kasa, ko sun ƙi, bambancewa a tsakaninsu don a san na kirki, as san na banza.

Addini shi kansa, musammam na Islam; yadda wasu mutane suke ta fassara shi cikin jahilci, ba haka yake ba. Sai ka ga musulmi amma ya zubarda halayen musuluncin; ka ga wanda ka ke maƙalawa kafirci, shi ma kuma bai ɗau ɗabi'un kafircin ba. Idan ka nazarci mutane a cikin addinansu, sai ka

rasa inda za ka wasunsu a haƙiƙa. In kai ne alƙali, a ina za ka ajiye wancan munafukin musulmin? Shin *furuci* kaɗai ya yi imani da Allah ɗaya ne, kuma Muhammadu ManzonSa ne, shi ne zai kai shi ga tsira, ko kuwa furucin haɗe da ayyukansa na tabbatarda ingancin furucin ne za su nuna shi mai cikakken imani ne a kan hanya miƙakkiya?

A musulunci, mun san *ayyuka* su ne suke nuna gaskiyar furucin. Wanda ya furta, amma kuma ya ƙi aikatawa ya zama munafuki. Amma, Allah (swt) Ba ya raina aikin mumini komai ƙanƙantarsa. Don haka, mai raina aikin alhairi komai ƙanƙantarsa, bai san hasarar kyakkyawan sakamakon da yake yi ba. Mun ji Hausawa, suna cewa, "*Ɗan haƙƙin da ka raina, shi ke tsokane maka ido*", ko menene haƙƙin, ko na alhairi ne, ko kuma na sharri, domin ma'aunan Allah (swt) suna da yawan gaske. Wasu abubuwa ba yadda ka ke zatonsu suke ba. Ga wata ƙissa mai ma'ana don misali:

An yi wani babban malami a wata Kasa a cikin tarihi. Mutum ne mai son Allah, mai kuma hidimar addini da kyaun ɗabi'u. Wata rana sai Allah (swt) Ya turo Mala'ika (Jubril) domin ya yi masa al-bishir da gidan Aljanna. Wannan malami ya yi matuƙar farin ciki da cikakkiyar godiya da wannan



albishir da aka kawo masa. Amma da ya nutsu, sai ya tambayi Mala'ikan: 'Me Allah (swt) Ya yi amfani da shi a cikin hidimomina na ibada da ɗabi'una na kirki, Ya yi min kyauta muhimmiya?'

Da Mala'ika ya dawo, sai ya ce masa ba ɗaya a cikin waɗannan. 'Dalilin kawai da ya sa Allah (swt) Ya yi maka wannan kyauta shi ne: Akwai wata rana kana alwala, sai Kuda ya sauka a kan hannunka ya sha daga danshin ruwan da yake hannunka ba ka kore shi ba. Wannan kawai ta sa Allah (swt) Ya yi maka Rahma, Ya kuma ba ka Aljanna'.

Malam ya yi mamakin wanan abu. Tareda ƙaskantarda kai, ya sake tambayar Mala'ika: 'Toh sallolina da sauran ibaduna, a me suka tashi?' Da Mala'ika ya dawo sai ya ce masa: 'Idan aka haɗa dukkanin sallolinka da sauran ibadunka, ba za su iya sai maka idonka ɗaya ba. Idan kuma ba ka da idanun, to ba za su sai maka, ko kunnuwanka, ko ƙafafunka ba; ballanta na ƙwaƙwalwarka, ballantana kuma halittarka gaba ɗaya da kawo ka wannan duniyar har ka san akwai Wanda Ya halicceta'. Malam ya ɗaga kansa sama ya ce, 'Allahu Akbar!'

Allah (swt) Shi ne mai yin abinda Ya so a kan dalilai da ma'aunan da suka dace da irin ɗau-

kakarSa. Ashe wasu abubuwan da mutum ya raina na alhairi ko na sharri, suna kuma da irin nasu muhimmanci da sakamakon a wajen Mahaliccinsa. Ba shakka, wasu abubuwa ba yadda muka fahimcesu suke ba. Haka kuma, ashe 'sharri' ƙanƙani, ya iya kai ka ga halaka babba. Ina masu fyadar jakuna kamar an aiko su? Ina masu ƙwacewa yara alawarsu? Ina masu korar Mage in ta roƙesu? Kada ku raina muhimmancin waɗannan wajen Mahaliccinsu. A wajen Allah (swt) babu bambanci tsakanin zahiri da baɗini. Yana sane da sirrin kowannensu, domin dukkaninsu a tareda Shi suke, kuma Shi ne Mai iko da su a kowanne lokaci. Mu ne jahilai, waɗanda zahirin ma ba mu fahimce shi sosai ba, kuma har yanzu ba mu san haƙiƙaninsa ba. Sai mun nutsu za mu fahimci kaɗan.

Sanin haƙiƙa, ba shakka, sai Allah (swt) domin Shi kaɗai ne ita. Watau, Shi kaɗai ne tabbatacce. Duk wani abu ga shi nan ne dai kawai tamkar a mafarki yake. Idan muka yi zurfin tunani da auna abubuwa, lallai mu yi al'ajabin wannan rayuwa tamu. Lallai mu yi tambaya: 'anya kuwa ba a cikin wani gagarumin mafarki muke ba, a yadda Allah Ya tsara abubuwa? Shi kaɗai ne fa tabbatacce! Me ya bambanta zahirin farkawarmu da zahirin mafarkinmu? Barcin kawai shi ne bambanci. A



wasu lokatan ma, sai mu yi mafarki cikin farkawar tamu, mu ga abubuwa tamkar a mafarkin, nan kuwa idanunmu biyu, mu rasa yadda aka yi, sai mun yi zurfin tunani sannan za mu fara fahimta.

A garemu, zahiri dabam take da baɗini, wanda ba mu da sani ko ƙanƙani a cikinsa. A zahirin, sai mun duba mun nutsa sosai sannan za mu iya fahimtar wani abu wanda zai amfanemu. Idan ba mu yi la'akari ba, sai mu dulmiya cikin duhu; zahirin ta zame mana baɗini. Da wannan ta faru kuwa, shikenan mun shiga wahala. Kafin a fita an cutu.

Rashin bincika mutane da sauran abubuwa, suke sa mu zaɓi na banza; suke sa a ci mu da buguzun; su ke sa mu girmama raunanan shugabanni; suke sa mu cikin ɓata; suke sa mu cikin ƙangin rayuwa iri iri. Wasummu ba su da ma'aunin inganci, saboda haka, sai su kai daraja ga wanda ba shi da ita, su kuma hana mai ita.

Wasu da an ce, 'ai wane digirinsa biyu', shikenan sai su maishe shi wani babba. Wasu da an ce, 'ai shi ne sarki', sai su faɗi gabansa irin yadda ba sa yi a gaban Allah (swt). Wasu da an ce, 'ga mai-kuɗi can', shikenan sai su saduda su zama yaransa. Wasu da an ce, 'wane gurgu ne', sai su ɗauka ba

shi da wani amfani. Wasu da an ce, 'wallahi', sai su yarda. Waɗansu da sun ga mara galihu, sai su tsane shi. Duk waɗannan ba lallai ne a ce sun cancanci amincewa, ko ƙi, haka ba. Cikin rashin sani da rashin bincike, sai ka kuskure a wajen ajiye mutane a matsayin da ya cancancesu. Irin wannan takan sa wasu su yi da-na-sani; ta kan kuma kawowa al'umma hasarar mutane ingantattu, waɗanda suka cancanci a ba su amanar shugabanci.

An yi wani mutum baƙo a wata unguwa wanda ba ruwansa da shiga harkokin da ba nasa ba. Kullum yana kaɗaice yana sha'aninsa wanda shi kaɗai ya fi sani. Talaka ne shi ƙwarai, amma ba ya roƙon kowa abinci. Saboda haka sai jama'ar unguwar suka ɗauka mahaukaci ne shi, ganin yadda tsarin rayuwarsa yake. Wasu lokatan ma, yara har dariya suke yi masa manya na gani. Wannan bawan Allah dai bai taɓa ƙorafi ba.

Wata rana ɗaya daga cikin makwabtansa, ya tafi Hajji. A yayin da yake ɗawafi, sai ya ga wannan mutum shi ma yana Dawafi, amma a cikin kamanni da tufafi masu kyaun gaske da ban sha'awa. Wannan abu ya ba shi mamaki ƙwarai da gaske. Ya ce a zuciyarsa, 'ko wannan mutum da muke zaton mahaukaci ne, ko ma waliyi ne? Yaushe ya zo Makkah? Ashe yana da halin tafiya har nan?



Da ya gama dawafinsa, sai ya tsaya daidai bayan 'mukami Ibrahim' yana jiran wannan mutum ya gama nasa dawafin. Da shi ma ya gama, ya kuma iso gurin, sai wannan makwabci ya gaishe shi, gaisuwa ta girmamawa. Mutumin ya amsa cikin nutsuwa da haiba a fuskarsa. Wannan makwabci ya ce, 'ka gafarceni Malam. Wallahi rashin sani ne ya sa dabi'unmu gameda kai suka zama haka'. Malam ya ce, 'Ba komai. Amma don Allah ka rufa min asiri, kada ka fadawa kowa a gida cewar ka ganni a nan'. Makwabcin ya amsa zai yi hakan; ya kuma roke shi ya yi masa addu'a, shi kuma ya amsa.

Da wannan alkawari suka rabu; kuma bai taba tona asirin ba. Bayan yan shekaru da dawowarsu, sai makwabcin ya kamu da ciwon ajali. Don haka, ya shaidawa matarsa cewar lallai in rai ya yi halinsa, wannan malami yake so ya yi masa Sallah. Matar ta yi mamaki, har tana zaton ko zafin cuta ne ya sa shi wannan bukata ta cewar mahaukaci ya yi masa Sallah. Ya sanarda ita ba haka bane. Sannan ya tilasta mata ta yi alkawri a kan hakan. Da ya rasu, sai matar ta shaidawa duk 'yan'uwansa wannan wasiyya tasa. Da ta ga sun fusata, sai ta ce masu ita kam ta yi wa mijinta alkawarin cika wannan bukata tasa; lallai wannan mutum ne zai Sallace shi, ko wasu sun yarda ko ba su yarda ba.

Da suka ga ba yadda za su yi, sai suka haƙura. Suka aikawa wannan mutum saƙon wasiyyar mamacin. Mutumin ya yi shiruu, sannan ya ce, 'Kun tabbata haka ya bukata?'. Suka ce, 'Haƙiƙa'. Da aka zo Salla, mutum ya shige gaba ya fara yi wa mamacin Sallah, sai jama'ar suka ringa ganin wani haske har da gizo-gizon Ka'aba a cikinsa, watau tamkar a Al-Haram suke yin wannan Sallah. Yawancisu suka ruɗe cikin al'ajabin wannan abu. Bayan Jana'izar, sai suka hanzarta suka dawo gida domin su ziyarci wannan Waliyyi. Amma da suka iso, sai suka tarar ya bar gidan; ya bar unguwar; ya bar garin ɗungum. Ba su sake ganinsa ba. Suka yi ta cigitawa, amma Ina!

To, ina masu raina mutane domin ba su da galihu a idanunsu. Ina masu wulakanta maƙwabtansu, ko masu korar masu nema a gurinsu domin sun zaci waɗannan mutane ba su isa ba?

A ɗaya gefen kuma, idan ka bar halaye da yanayin rayuwar wasu, ka ce za ka auna waɗansu muƙamai ko darajoji ko adajen duniya da wasu suke da su, to idan da za ka iya yin zurfi cikin zukatan masu su, mayiwuwa ne ka tarar cewar su kansu ba jin daɗinsu suke yi yadda ka zata ba. Tara adajen duniya dabam yake da tara jin daɗin duniyar.



Wasu abubuwa kana hangosu ne daga nesa kawai, sai ka zo kusa za ka san ba haka suke ba. Idan ka ji masifun da wasu suke ciki, duk kuma saboda abinda suka tara, to sai ka gode Allah (swt) kai ba ka tara waɗannan abubuwa ba. Wasu masu kuɗin, kuɗin ne jidalinsu. Wasu masu sarautar, ita ce wahalarsu da tararradinsu. Wani kuɗinsa ko mulkinsa ne za su kai shi kurkuku ko ma lahira. Wasu kuma, sune su ke jawo masu baƙin jininsu. Wasu kuma su ne hanyar nisartarsu da Allah.

Wasu ga su ana ganin babu irinsu a dukiya, amma bashin da yake kansu ya fi ƙarfinsu, ba wanda ya sani. Wasu sun ɗauko rigimu iri iri, ba su san inda za su kaisu ba. Wasu sai sun mutu magada za su shiga rigima. Wasu masu son sarautar, alla-alla suke iyayensu ko 'yan'uwansu su mutu domin su gaje su. Wasu ma su ne sanadin mutuwar iyayen nasu. Wasu ga kuɗin baja-baja, amma talauci ya ci ƙarfinsu; wasu ga sarautar buja-buja, amma nagarta ta fi ƙarfinsu. Wasu muna ganin ba abinda ba su da shi, amma su suna ganin ba su da komai. Wasu kuma hankalinsu na can a kan wasu abubuwa da suka rasa, sun manta da waɗanda suke da shi. Wasu duk kuɗinsu da mulkinsu, ba su da cikakkiyar lafiya; wasu ma ba mai ƙaunarsu ko da a cikin zuri'arsu. Ga wani can ya tara abinci a rumbu,

amma ya kasa cin ko ƙwaya. Wani ga littattafan ilmi nan, amma duk ɗabi'unsa na jahilai ne. Wani ga sarautar, amma zuciyarsa a ƙuntace. Wani ba abinda bai mallaka ba, amma kuma ba shi da ko-mai, ko kuma kullum cikin baƙin ciki; zuciyarsa a ƙone don wasu dalilan da ba a sani ba.

Wasu da yawa, kai ne abin sha'awarsu, saboda la-fiyarka, ko saboda 'yancinka, ko saboda ilminka da azancinka, ko saboda farin jininka, ko saboda yakanarka da kyaun zantukanka, ko saboda wani rufin asiri da suka hango tareda kai, wanda sun san ba su da shi. Mutum shi kaɗai yake iya fassara kansa daidai, sai dai in zai munafunci kansa da kansa. Wanda kuwa ya munafurci kansa, to babu wawa irinsa. Lallai ne mutum ya san ko waye shi, ya kuma san ya tsakaninsa yake da Allah (swt). Mutum shi ne kaɗai mai iya hangen rayuwarsa ya shiryata yadda yake ganin za ta fi dacewa da shi. Mutum shi ne kaɗai ma'aunin kansa na gaskiya. Amma, a yadda wani ke hango wani ko wasu; da yadda wani yake auna wani ko wasu; da yadda wani ke zaton wasu abubuwa, duk ya iya tararwa ba haka suke a ainihinsu ba. Nazarin wani dabam kuma, ya ba da wata ma'anar dabam. Haka ake tafiya, har sai cikakken nazari da aunawa sun fiddo da gaskiyar tsarin mutum da ingancinsa.



Don haka, ya zama wajibi, mutum ya kasance mai yawaita tunani da zurfin nazari a kan komai, musammam ma a halayen da ya sami kansa ciki. Kada mutum ya yi saurin hukumta mutanen da bai nazarta ba. Kada mutum ya yi saurin ƙyamar mutane domin a idanunsa ba su cimma awonsa ba. Masu iya bambance abubuwa cikin haƙuri ba da gaggawa ba, sune za su iya sarrafasu su kuma ci moriyarsu yadda yakamata. Masu iya bambance abubuwa sune za su iya yin jawabi a kan abubuwa yadda ya dace da kowannensu. Ko a cikin mutane ne, ka iya bambance halayensu da bukatansu, to za ka fi iya zama da su. Hakama dabbobi. Idan ka ce yadda za ka shaƙata a bayan Tunkiya, haka za ka yi a bayan Jaki, to kuwa wataran ka sha harbi.

Yawancin abubuwa ba yadda suke muke ganinsu ba. Lallai a duba sosai a yi cikakken nazari.

A wani zamani can cikin tarihi, an taɓa yin wani mashahurin Malami mai ɗimbun ilmi; sannan ga jama'a da almajirai masu yawan gaske. A kan je neman ilmi iri iri gurinsa, har da kimiyyar azanci da hikima, daga ko'ina a wannan ɓangare na duniya. Amma, duk lokacinda mutane suka tambaye shi asalin wannan ilmi nasa, sai ya nuna masu wani ƙaton littafi yana cewa duk ilmin nan

nasa yana kunshe a cikin wannan littafi daya tak, wanda yake a adane a cikin turakar littattafansa.

Da Allah Ya yi masa rasuwa, sai magada da dalibai suka yi hanzarin dauko wannan muhimmin littafi don kwadayin fahimtar ilmin cikinsa. Suka fara buda shafunan wannan katon littafi daya da daya, amma ba abinda aka rubuta cikinsu. Sai da suka iso kusan karshen littafin suna al'ajabin wannan abu, sannan suka taradda shafi daya tak da rubutu bai fi layi uku cikinsa ba. Abinda kawai aka rubuta a cikin wannan shafi shi ne:

"Duk wanda ya fahimci bambancin da yake
tsakanin kwano da abinda yake cikinsa,
toh ya sami isasshen ilmi."

Ba shakka wannan abin mamaki ne, kuma wannan magana tana bukatar zurfin tunani. Kamar yadda muka fara tun farko, bari mu nanata cewar, wannan kwano ya iya zama komai. Abinda yake cikinsa ya iya zama komai. Duk maganar ta fahimtar bambanci ce. Amma fa ba bambanci cikin hanzari da rashin tunani da nazari ba.

Misali: Idan ka fahimci bambancin duniya, in ita ce kwanon, da al'ummun da suke cikinta, ba



shakka ka sami ilmi mai amfanin gaske. Idan ka fahimci bambancin addinin Islam da musulman da suke cikinsa, za ka iya riƙe addininka komai rintsi, ka kuma zama musulmi nagari. Ba za ka raina addininka don ka ga yadda wasu musulmi suka watsarda shi ba, domin tuni ka bambantasu. Amma idan ka ɗau ɗabi'ar wasu musulmi, ka ce wannan shi ne musulunci, to ba shakka ba zaka san musulunci ba. Idan kuma ka fahimci bambancin dukiya da masu kuɗi, to rayuwarka za ta fi zama mai gamsuwa, domin za ka san yadda za ka sarrafata in ka sameta, da yadda kuma za ka iya ƙuƙutawa a rayuwarka in ba ka sameta ba. Idan ka fahimci bambancinka da sauran jama'a, to za ka iya zama da su lafiya, domin za ka san abubuwan ƙinsu da na sonsu, da waɗanda za su iya yi da waɗanda ba za su iya ba. Haka kai ma dangane da su. Duk maganar ta nazarin banbanci ce, domin ka da ka hautsuna tunaninka ka shiga cikin ɓata.

Idan halayen mutane nagari da ƙoƙarinsu da fafutukarsu su ne ma'aunanka, ba dukiyarsu ko muƙaminsu ba, to ba shakka, ba za ka yi kuskure a kansu ba, kuma ba za ka wahaltu a banza a kansu ba. Wasu sai ka ga abinda kawai suke taƙama da shi shi ne asalinsu, watau su 'ya'yan wane ne, amma fa ba su da wata martaba dabam wadda tasu

ce ta kansu daga ƙoƙarinsu. Duk wanda ya jingina da asalisa, amma shi kansa bai zama komai ba, to ya zama wawa. Mafi mahimmanci a gareka shi ne, ‘waye kai a zahirinka da baɗininka? Me ka ke yi?’ Lallai mutane su yi la’akari da haka.

Idan ka iya bambancewa tsakanin furuci ko wa’azin da wasu ke yi, da kuma ayyukansu da halayensu, to za ka fi saninsu a cikin kamanninsu na ainihi, ka kuma aunasu. Kada kyaun riga da iya zance su ruɗeka ka yi saurin amincewa. A iya damfararka. Amma kada tsofaffin tufafi su sa ka kori mai wa’azi, domin watakila shi ne mai faɗar gaskiyar. An fi jin gaskiya a bakin yaro da wawa, amma ba su ne suka fi kowa hankali ba.

Wasu abubuwa ba shakka, ba yadda suke ake ganinsu ba. Ko sama ka ɗaga kanka, taurari kawai za ka gani. Idan ba ka iya bambancewa da zurfin nazari ba, ba za ka san hikimomin Allah (swt) ba. Ba za ka san kai ma a saman kake ba. Ba za ka san Rana a yadda take minti takwas da suka shige ka ganta ba. Dá al’umma tana bambamce abubuwa irin waɗannan gameda mutane da sauran abubuwa, dá an ci gaba yadda ba a zato. Dá yawancin abubuwa sun tafi yadda ake sonsu. Dá ba haka ba. Kukan kurciya ma jawabi ne…….



RAYUWA ABAR MISALI

Wata rana, Ali bin Abu-Talib (as), ya tambayi Annabi Muhammad (saw), cewar, wacce Sunna zai bi ya zama cikakken mutum? Sai Annabi Muhammad (saw), ya yi masa bayanai gameda nasa ɗabi'un. Ya ce :

****

*I "SANIN UBANGIJI SHI NE JARINA"
*II "HUJJA ITA CE TUSHEN IMANINA"
*III "SOYAYYA ITA CE GINSHIKINA"
*IV "TUNANIN ALLAH SHI NE ABOKINA"
*V "DAGEWA ITA CE DUKIYATA"
*VI "TAUSAYI SHI NE ABOKIN ZAMANA"
*VII "ILMI SHI NE MAKAMINA"
*VIII "HAKURI SHI NE MADOGARATA"
*IX "WADATAR-ZUCI ITA CE GANIMATA
*X "K'WAZO SHI NE GWANINTATA"
*XI "IMANI SHI NE K'ARFINA"
*XII "GASKIYA ITA CE CETONA"
*XIII "LADABI SHI NE CIKATA MUTUM"
*XIV "FAFUTUKA ITA CE ƊABI'ATA"
*XV "IBADATA ITA CE FARIN-CIKINA"





Rayuwa Abar Misali

'Mu yi koyi da Manzon Allah'

Wannan muhimmin Babi ya zama wajabtacce a wannan littafi namu, domin kuwa kulliyar darusanmu sun tattara ne a cikin wadannan dabi'u na shugabanmu, Annabi Muhammad (saw). Duk gaba dayansu a cikin Tunaninsa ya sakasu, sannan suka zama Halayensa. Ba shakka, ba mu da abin bege irin kasancewa cikin kyakkyawar Halayya irin tasa. Koyi da shi ya zama wajibi a kanmu duka.

Zai yi amfani kwarai idan na yi kokarin yin takaitaccen bayanin kowacce dabi'a cikin dabi'un nan 15, domin fito da hikmarta, (a cikin azanci irin nawa) da yadda za ta iya taimakawa duk mai son inganta rayuwarsa da rayuwarta.

I.
"SANIN UBANGIJI SHI NE JARINA"
****

Hakika, duk wanda ya san Ubangiji, Allah (swt), ya sami tabbataccen jari. Amma fa ba sanin shanu ba. Ga yawancinmu, sanin Allah yana da ma'anoni dabam. Yadda wasu suka fahimci Allah, suke kuma zancenSa, ba haka wasu suka fahimta ba. Amma a gaskiya, Allah (swt) Ya shige duk yadda aka fahimce Shi. Sai dai kuma, tilas mu yi kokari irin namu, mu sanShi ta yadda yakamata.

'Sunayen" Allah (swt), guda 99n nan da muka sani, watau. "Asma'ul Husna", ba sunaye kadai bane, ba kuma alamu ne kadai ba. Kulliyar Ikonni da Halaye ne na Allah (swt). Duk zurfin tunaninmu ba za mu iya kure wadannan lakabai na Allah (swt) ba, domin sun kunshe komai a cikinsu. Nazarinsu cikin nutsuwa da saninsu ko fahimtarsu cikin hikima tareda yadda suka danganci juna, da yadda

suke da iko a kan komai wanda ya danganci sunansu, su ne suka tattaru suka ba da ma'anar "Sanin Ubangiji" yadda Yake, ba yadda muke zatonSa ba. Waɗannan 'Sunaye' ba shakka suna da muhimmanci a tareda mu, tunaninmu da yadda za mu tafiyarda rayuwarmu a kodayaushe. Su ne kuma suke gudanarda komai a Sararin Samaniya, da kuma Lahira ita kanta. Da su kuma komai yake tabbata. Hasalima dai, **ta hanyar amfani da su ta hanyoyin da Ya koyarda su a garesu, Mala'iku suke cika kowanne umarni na Ubangiji**. Wannan wani babban ilmi ne mai zurfin gaske wanda masu ɗinbum ilmi ne kaɗai za su iya yin bayani yadda za a gane. Abin ya shige wannan ɗan littafi. Sai a yi bincike a hankali.

Da Allah (swt) Ya ce, "Zan ajiye Khalifa a Kasa" (duniyar Arɗ) (a Baƙara: Aya ta 30), lallai ne mu fahimci abinda 'Khalifa' take nufi a cikin ma'anrarta mafi azanci da dacewa. Ba za mu iya fassara 'Khalifa' tamkar 'magaji' ko 'mai jirangado' kamar yadda wasu mutane suke yi wa kansu, ko ake yi masu, laƙabi saboda siyasa, ko addini ko sarauta ba. Hauka ma ba zai yarda da irin wannan Khalifanci gameda Allah (swt) ba, ballantana kuma hankali. Tunani mai zurfi gameda Allah (swt) shi ne zai iya nuna mana ma'anar da ta dace.



Lallai ne mu fahimci Khalifancin Allah (swt) dangane da mutum ta hanyar baiwowin da Allah (swt) Ya ba wa mutum daga 'SunayenSa' a wannan duniya. Misali: 'Dauki "Al-Malik" ('Sarki'). Ko Jaki ne ya zama sarkin mutane, to sai kwarjininsa da ikonsa sun canja ta yadda zai fi ƙarfin duk mutanen da suke a ƙarƙashin sarautarsa, har sai sa'inda Allah Ya yaye rigar Khalifancin sarautar daga gareshi, sannan zai dawo jakinsa. Da farko dai Allah (swt) Ya ce Shi ne Mai-Mulki ko Mai Sarauta (Al-Wali). A cikin 'Sunayen' nan na Allah (swt) waɗanda suka shafi Mulki akwai 'Mai Iko' (Al-Kadir) a kan komai da komai a duk faɗin wannan mulki naSa. Saboda haka, duk lokacinda Ya zaɓo mutum, komai rashin kwarjininsa, ko yawan ƙasƙancin asalinsa, ko gazawar galihunsa, Ya ba shi mulki, to nan take Zai yafa masa alkyabbar Khalifancin Ya kuma tarfa masa kaɗan daga wannan 'Iko' a kan komai a faɗin mulkin mutumin. Nan take sai wannan mutum ya zama abin tsoro a idanun jama'a, har da waɗanda suka raina shi ko suka raine shi kafin ya sami wannan mulki. Dalilin mai sauƙi ne. Yanzu shi ne Khalifar Allah (swt) a mulkin birnin in shi ne sarkin birnin ko gwamna, kuma mai iko a cikin faɗin mulkin nasa; kuma haka zai tafi da ƙasaitarsa har sai ya zubarda ita ta hanyar kaucewa ƙa'idojin Allah na

mulkin, kamar dai irinsu ‘Mai Adalci’ (daga Al-Adl); ko ‘Mai Tausayi’ (daga Al-Ra’uf); ko Mai Alfarmar Kyauta (daga Al-Karim) da dai sauransu in an duba sosai.

Saboda haka, ashe, wannan Khalifanci yana ɗauke da irin waɗannan nauyi tareda shi, kamar yadda muka gani a cikin waɗannan ‘Sunaye’ naSa (Allah -swt). Akwai kuma ɗaɓi’u waɗanda suka danganci kowanne matsayi da Ya sa ɗan-Adam a kai. Misali: Da Allah (swt) Ya ce Shi ne mai Mulki a kan komai, sai kuma Ya ce, Shi ‘Mai adalci ne”, Shi Mai Jin Tausayi ne’, ‘Shi Mai Gaskiya ne’, da dai sauran irin waɗannan halaye da suka danganci Mulki da shugabanci. Saboda haka, Yana bukatar duk KhalifofinSa a Mulki su kasance masu waɗannan halaye; ba azzalumai ba; ba marasa tausayi ba; ba maƙaryata ko macuta ba. Idan ba su ɗauki waɗannan ɗabi’u naSa a fannin Mulki ba, to sun zubar da Khalifancin, sun ci amanarSa, kuma ko badaɗe ko bajima sai sun tarar da wulakancinSa a tareda su. Ba a cin amanar Allah a zauna lafiya!

A komai ka duba; ko Kuɗi, ko Ilmi, ko menene, za ka tarar masu waɗannan baiwa Khalifofi ne kawai a waɗannan fannoni da Allah (swt) Ya ba su baiwar. Kuma a cikin ‘Sunayen’ Allah (swt) akwai

nauyin da ya wajaba a kawunansu, in sun kasance masu lura da hakan. Idan kuwa suka kauce, to cikin lokaci Allah Zai ɗauke KhalifancinSa ya kuma cire alkyabbar wannan Khalifanci daga garesu. Nan da nan, sai ka ga wulakanci ya fara isar masu, amma mutane ba su san dalili ba. Idan masu kuɗi ne, sai su fara tsiyacewa; idan masu ilmi ne, sai ka ga ilmin ba ya amfanarsu sai ma dulmiyarda su. Idan malamai ne, sai mutane su fara kauce masu. Idan masu Sarauta ne, sai ka ga ba Mulkin, ana gudunsu, ko ma jifansu. Haka dai kowa da abinda ya dace da shi na tonon asiri daga Allah (swt); nunin Ya tuɓe shi daga wannan khalifancin, ko da Ya bar shi da muƙamin saboda wasu dalilan dabam.

Sanin Allah (swt) yana bukatar nazarin waɗannan ‘Sunaye’ naSa. A duk ‘Suna’ na ‘Muƙami’, toh kuwa akwai ɗabi’u da nauyin da suka maƙalu da muƙamin, ko na Mulki ne, ko na Wakilci ne, ko na Arziki ne, ko Ilmi ne, ko na Makiyayi ne, ko na Alƙalanci ne, ko na Amana ne da duk sauransu. Haka kuma, ga kowacce bukata ta ɗan-Adam, ko ta dabbobi da tsiranni, akwai ‘Sunan’ Allah (swt) na Alfarma mai nunin biyan wannan bukata. Da wannan ‘Suna’ za a yi ta roƙonSa domin Ya kawo caffa ga masu wannan bukata kowacce iri ce. Haka duk Mai-aikata kyawawan abubuwa, irin yadda

littafin nan yake ta faɗa, shi ma wannan Khalifa ne shi a wajen wannan alhairi, domin Allah (swt) ya ce, Shi ne “Al-Barr”. Waɗansu ‘Sunayen’ kuwa ba mai iya sarrafasu sai Shi, amma ɗan-Adam yana da damar ya roƙe Allah Ya sarrafasu a kansa. Kamar dai Al-Rahman da Al-Rahim. Haka dai ga abubuwan nan na ban sha’awa da ilmi gameda waɗannan “Sunaye” idan aka yi nazari mai zurfi.

Yawancinmu a yawancin lokuta muna kallon halayen Allah (swt) tamkar shigen irin na mutum ne. Toh, a wasu fannonin ba shakka hakane, domin a mutumtakarmu muna da Khalifanci ta wasu hanyoyin ko su waye mu. Amma halaye da ɗabi’un Allah (swt) sune maƙuran aminci a waɗannan fannonin. Namu ne shigen naSa. Kuma akwai “Sunayen” da za mu kwaikwaye su daga GareShi dominSa da kuma mu kanmu. Kamar dai “Soyayya” (Al-Wadud) da “Hakuri” (Al-Sabur). Ba shakka, Allah (swt) ba Zai halicci abinda ba Ya so ba. Amma tunda Ya bawa wasu hallitu, kamar dai Ɗan-Adam, zaɓi, to mutum ya iya zaɓar ya so Allah, ko kuma ya ƙi Shi. Amma, ƙin Allah, sakamako ne na rashin sanin Allah, domin duk wanda ya san Allah yadda yakamata a san Shi, to shi ma wannan mutumin ba shi da zaɓi illa ya so Allah da soyayyar da ta kamaci a so Shi.



Wanda ya san Allah sosai, shi yake barin al'amuransa ga Allah. Shi yake iya danƙawa Allah amanarSa, domin ya san Allah Zai kiyaye wannan amana, domin Shi ne (Al-Mani). Wanda ya san Allah, shi yake bin Allah ta kowanne fanni a kowanne hali ya sami kansa ciki, ya kuma yi "Haƙuri" da hakan. Shi ne kuma yake iya haƙuri da macutansa domin ya barwa Allah ramuwarsa, domin Allah Shi ne (Al-Muntaƙim). Daga waɗannan "Sunaye", ba shakka, akwai babbar shiriya ga masu nazari.

A kowanne fanni na rayuwa, mutum yana da zaɓin wanne gefe zai tsaya. Gefen Allah ko gefen shaiɗan? Wanda ya san Allah sosai, shi ne nan da nan yake tsayawa a gefen Allah, ba ma sai ya yi wani dogon tunani ba. Wanda ya yi ƙaranci a saninsa na Allah, shi ne yake tsayawa a gefen shaiɗan, ba ma sai ya yi wani tunani ba. Ashe, ba shakka, sanin abinda Allah Zai yi da wanda ba Zai yi ba, babban jari ne da Manzon Allah yake da shi. Dukiyarsa ta 'Sanin Allah' babbar dukiya ce, wadda lallai mu yi kwaɗayinta ta hanyar nazari, mu kuma tabbata mun sameta ta hanyar kyakykyawan tunaninmu gameda Allah (swt). Za mu iya ci gaba da wannan bayani, shi kaɗai ba iyaka, sai dai wannan littafi yana da tasa iyakar.

II.
"HUJJA ITA CE TUSHEN IMANINA"
****

Haƙiƙa, duk abinda ba a yi masa tushe da Hujja ba, to kuwa ba zai yi ƙarko ba. Duk mutumin da yake yin abinda bai tabbatar da gaskiyarsa da dalilinsa da cancantarsa ba, to bai zai ɗau wannan abu da muhimmanci ba, kuma duk sa'inda dama ta samu na rabuwa da abin, to kuwa nan da nan zai rabu da shi. Ko dukiya ka samu a banza, to riƙon sakainar kashi za ka yi mata. Haka mulki da shugabanci, haka aure, haka 'ya'ya, haka komai ma. Duk abinda ba shi da hujja a gareka, to kuwa ba shi da mutumcin da ya dace da shi a gareka.

'Musulmi' da yawan gaske a gurare masu yawan gaske, waɗanda har yanzu ba su kafa hujjar imaninsu ba, su ke wasa da addininsu, suna ganin wannan zance duk kamar na wasa ne. Tunda ba su yi wa imaninsu hujja ba, furucin imanin kawai suka yi, to kuwa ba su iya aikata abubuwan da imanin ke bukata. Saboda haka ba za a iya ganin misalan addinin Islam a yawancin ayyukansu ba. Musuluncinsu a baki kawai yake. Muhimmin dalilin wannan shi ne: yadda aka haife su Hausawa, ko Yarabawa, ko larabawa, ko Malay-

awa, haka aka haife su musulmi. Watau jinsinsu ko ƙabilancinsu sune kaɗai hujjar musuluncinsu. Don haka, wasu lokatan muke ganin waɗanda suka bar wasu addinan suka shiga Islam, sun fi yawancin musulmin da aka haifa cikinsa riƙe addinin da gaskiya. Wannan kuwa ta faru ne saboda waɗannan 'sababbin tuban' kamar yadda bahaushe yake kiransu a wulaƙance, sai da suka sami hujja tabbatacciya tukuna sannan suka karɓi addinin Islam, watau sai da suka ga wata 'gaskiya' ta Islam, ko kuma mu ce, sai da 'hasken Islam' ya ratsasu tukuna, sannan suka yi imani da addinin.

Haka, a inda ka ga yawancin musulmin da aka haifa cikinsa sun karɓe shi da kyau suna kuma aikata shi da kyau daidai ƙarfinsu, to nazarinsa suka yi, suka sami hujja wadda za su ɗora imaninsu a kai. Ba a banza ko haka siddan suka zama musulmin kirki ba. Duk wanda bai yi tunani mai matuƙar zurfi cikin nutsuwa a kan Islam ba, to ba zai sami hujja wadda zai dogara da ita ba. Irin waɗannan 'musulmi' su ne suke jawowa Islam abin kunya, suna ɓata sunan addinin. Irin waɗannan 'musulmi' su ne ba sa jin kunyar zunubansu, ko ma su ringa danganta waɗansu miyagun zunubai nasu da wata daraja da suke nema, ko suka samu. Waɗannan taƙadirai sun raina Allah (swt).

Maganar Annabi Muhammad (saw), cewar, 'Hujja ita ce imaninsa', ba ƙaramar magana ce ta hikima da azanci ba. Wannan tana nuna mana cewar dama tun farko, zuciyarsa da tunaninsa tuni suka gamsu da hujjar Islam, cewar shi ne addini na gaskiya, wanda ya cancanci a bi, a kuma yi aiki da shawarwarinsa da gargaɗinsa da hukumce-hukumcensa, musammam kuma, shi aka aikiowa da addinin don ya yaɗa shi a duniya. Musulmin da ya kafawa imaninsa hujja, ba ya jin kunyar musuluncinsa duk inda ya shiga. Waɗanda ba su tabbatar da gaskiyar musuluncinsu ba su ne suke jin kunyar nuna musuluncinsu a wasu gurare, suna ganin kamar ƙauyanci ne, ko abin kunya ne su ce su musulmi ne, ko su aikata wata ibada ko su nuna wata ɗabi'a ta musulunci. Amma, mai alfahari da addininsa, da kuma aikata shi yadda yakamata, shi ne wanda ya kafawa imaninsa hujja, kuma yake da ɗokin ya nuna musuluncinsa a duk inda ya je, da duk inda ya sami kansa, ba tareda jin kunya ba.

Lallai tun daga yau mu kafa wannan hujja a zukatanmu, mu san dalilan da suka sa muke cikin wannan addini na Islam, mu kuma san bambancinsa da sauran addinai, mu kuma gamsu da hujjar wannan bambanci. Idan ba mu yi haka ba, muka karɓa kawai babu bincike, watau cikin

jahilci, don haka muka gada, to ba za mu iya zama musulmin kirki na ƙwarai ba. Ko a siyance, aƙida ba ta ƙarko idan ba a kafa mata hujja ba. Toh, ballantana kuma a addinance. Wanda ya kafa hujja shi zai ci riba.

Babu laifi ko kaɗan idan mutum ya zauna ya tambayi kansa, ‘me yasa na karɓi Islam addinina? Don kawai shi na gada, ko kuma don shi ne ya fi dacewa? Me yasa ya fi dacewa? Lallai ka karanci Al-Kur’ani da tunani da nazari, ka kuma yi tambaya a kan abubuwan da suka shigar maka duhu, ko kuma suka rikitar da kai. Haka gameda Allah (swt), lallai ka yi tambayoyi a kanSa duk sa’inda wani abu ya ɗaure maka kai. Ta haka kaɗai za ka iya saninSa, ka kuma kafawa addininka hujja, duk a lokaci guda. Daga sannan ne kaɗai za ka iya zama mai cikakken imani ga Allah (swt) da kuma dogara da Shi, Shi kaɗai. Ta haka kaɗai za ka iya zama mai alfahari da musuluncinka, ka kuma iya kare shi a ko’ina, komai rintsi, ka kuma iya rayuwa cikin shiriyarsa. Ta hakane kaɗai za ka so Allah (swt), soyayya ta gaskiya, irin wadda muka yi magana a kai a Babi na 9 da kuma baya kaɗan a wannan Babin. Ta haka kaɗai za ka iya gina soyayyarka da girmamawarka ga ManzonSa, Muhammad (saw) da sauran Mursalai da

Annabawa da duk na kusa da Shi. Ta haka kaɗai za ka iya fahimtar sauran addinai, ka kuma ba su damarda ta dace da su, ka kuma kare ’yancinka a gurinsu. Ta hakane kaɗai za ka iya zama jarumi na ƙwarai a cikin musulmi. Wanda zuciyarsa da tunaninsa suka wadata da hujjar imaninsa, ba shakka, ya samarwa kansa matukar alhairi, ya kuma shiga layin muminai na ƙwarai.

III.
“Soyayya ita ce Ginshikina”
****

Duk wanda ya kafa rayuwarsa a kan ginshiƙin soyayya, a haƙiƙa wannan mutum ya kafa rayuwa a kan ‘tafin hannun’ Allah na Alhairi. Allah (swt) Shi ne ‘Soyayya’ a ilahirinta; kuma Ya halicci komai ne domin soyayya. Duk wanda ya yi soyayya saboda Allah, to kuwa ya yi koyi da Allah (swt) da kuma ManzonSa.

Babu wani abu da zai tabbata, ya kuma yi amfani da albarkar da ake so, sai in an jingina shi, ko an shimfiɗa shi a kan soyayya. Cikakken Sanin Allah ba ya tabbata sai da soyayya a gareShi, kamar kuma yadda soyayyar za ta taimaka wajen ƙarin sanin naSa. Haka son Manzon Allah da koyi da



shi, waɗanda kuma su ne suke ƙara tabbatarda imanin mai su. Ba a taɓa shuka soyayya ta kasa furanni ba; kuma furanninta ba sa mutuwa. Duk abinda ka yi, ko aka yi maka; ko ka samu, ko aka ba ka, ba a sonka ba, to wannan abin ba zai taɓa yin martaba a idanunka ba. Idan kai ne makiyayinsa, to ba za ka kiyaye shi yadda yakamata ba.

“Son Allah”, ba irin son da ya ke tsakanin namiji da mace bane. Haka kuma ba irin yadda mutum ya ke son motarsa ko wata kadararsa bace. Haƙiƙa, ‘son Allah’, irin yadda Annabi Muhammd (saw) ya ke faɗa, soyayya ce wadda take cika zuciya har sai ta mamayeta gaba ɗaya, amma ba ta ƙare ba, ita kuma zuciyar ba ta ƙoshi ba. Sai kuma soyayyar ta kwararo daga zuciyar, har sai mamaye idanu da kunnuwa da harshe. Sannan ta bi hannaye da ƙafafu da sauran jiki gaba ɗayansa. Don haka, ‘mai son Allah’ da irin wannan soyayya shigen ta Muhammad (saw), sai ya ringa jin ba abinda ya ke son gani, sai abinda Allah Yake so da wanda Ya so a gani. Ba abinda yake son ji don biyayya, sai maganar Allah. Ba abinda yake son furtawa sai sunanSa. Ba abinda yake son ya sa hannunsa a ciki, sai abinda Ya halarta masa. Ba kuma inda yake son ya je, sai gurinSa. Wannan ita ce irin soyayyar Muhammad (saw) ga Ubangijinsa, Allah (swt).

Wannan ita ce irin soyayyar da muke ta ƙoƙarin kwaikwayo, domin mu ma, mu so Allah shigen haka, mu kuma so ManzonSa saboda haka.

Rayuwa gaba ɗayanta, takan ginu ne a kan soyayya. Da soyayya ake auratayya, a kuma sami ‘ya’yan soyayya waɗanda ake sonsu. Da wannnan soyayya ta iyaye ga ‘ya’yansu, sai su tabbata sun sa ‘ya’yan a kan hanyoyi nagari, suna yi masu fatan alhairi da ɗaukaka fiye da yadda su kansu iyayen suke. Auren da babu soyayya a cikinsa, ba ya ƙarko, kuma in an matsanta, a sami ‘ya’yan da ba a so waɗanda ba za a kula da su ba. Daga nan kuma tushen iyali ko zuri’a ta-gari ya tunɓuke.

Son karatu shi yake haifarda ilmi, a sami al’umma ma’abociyar ci-gaba. A irin wannan al’umma ake kafa soyayya wadda za ta iya taimakon kowa, ba a bar ‘ganin-ƙyashi’ ya sami gurbi ba, ballantana uwarsu hassada. Masoyi, ba ruwansa da hassada ga wanda yake so. Ba ya baƙin cikin ci-gaban wanda yake so. Masoyi, shi yake damuwa da masifun da mutane suka shiga, ya kuma taimaka ta duk yadda zai iya. Don haka ashe, wanda ya mayarda soyayya ginshiƙinsa, ba zai kasance maƙiyin komai na alhairi ba. Soyayya ita ta kewaye shi, kuma kullum a cikinta yake gameda kowa da komai. Wannan

mutum shi ne masoyin Allah (swt), masoyin addininsa, masoyin al'ummarsa da iyayensa da 'yan'uwansa; masoyin kowa da alhairi. Haka kuma shi ma za a so shi a sakamako na Allah (swt).

Ba shakka, Allah (swt) Yana son dukkanin abubuwan da Ya halitta, domin Bai hallicesu da wasa ko don wasa ba. Don haka, duk wanda ya nuna soyayya ga wata halitta ta Allah (swt), wannan ya nuna soyayya ga Allah (swt). Masoyin abinda ka ke so, ba shakka masoyinka ne. Idan ka so dabbobi, ko tsuntsaye ko tsuranni, ka kuma adane su, ka kare rayuwarsu ko lafiyarsu, to ba shakka, ka yi ibada mai girma a wajen Allah (swt). Hanyoyin samun rahamar Allah (swt) suna da yawan gaske, sai dai in ba a yi tunani a kansu ba. Amma wanda ya azabta jama'a ko dabbobi ko tsiranni, to ba shakka shi ma zai azabtu a gaba.

Masu tunanin soyayya, ba za su ɓata lokacisu wajen ƙiyayya ba. Tunda soyayya ita ce kewaye da su, ashe ma babu gurbin ƙiyayya a kusa da su. Wanda kuwa ya bar ƙiyayya ta sami gurbi a tunainsa da zuciyarsa, wannan mutum ya yi hasarar rayuwa mai ni'ima, ya kuma yi hasarar babban maganin maƙiya da mahassada. A wannan 'yar rayuwa taƙaitacciya, ina ka ke da isasshen lokacin

aikata duk alhairin da ya kamace ka, balle kuma har ka ɓata wani ɓangare na lokacin wajen shiri da aikata ƙiyayya? Wannan hasara da yawa take, amma fa ga mai lura. Wanda ya cika zuciyarsa da soyayya, ya gama da masifun duniya da lahira.

IV.
'TUNANIN ALLAH SHI NE ABOKINA'
****

'Aboki' tamkar 'masoyi' yake, sai dai su 'abokai' ma'abotan saduwa da juna ne, watau ma sun san juna. Za ka iya son mutum, ko wani abu, ko da kuwa ba ku san juna ba, ko da kuma ba ka taɓa ganinsu fuska-da fuska ba. Kamar dai yadda muka yi zancen soyayya ga Allah (swt) da ManzonSa, Muhammad (saw). Amma. Aboki, sai wanda ka sani ya kuma sanka, ku ke kuma da wata alaƙa da juna wadda ta maisheku abokai.

Manzon Allah ya ce, 'Tunanin Allah' shi ne abinda yake yi a kodayaushe, tun da har wannan tunani ya zama jiki, ya kuma zama abokin zama tare. Da 'Tunanin Allah', da 'Tuna Allah' abubuwa biyu ne a ƙunshe a cikin abu guda. Ba za ka yi 'tunanin' abu ba, sai ka 'tuna' da shi. Tunawar ita ce Zikri,



Tunanin kuma shi ne juyayin al'amuran Ubangiji a zuci a kodayaushe. Nafsin da ya mai da Zikri (tuna Allah) daɓi'arsa, kuma saboda Allah, -zan nanata "kuma saboda Allah"- to ba zai taɓa mantawa da Gaskiyar Allah (swt) ba, ballantana kuma ya shagala cikin ayyuka ko al'adu waɗanda ba su dace da wannan kyakkyawan yanayi na zuciyarsa ba. Tunanin Allah (swt) shi ne yake tunasarda mutum matsayinsa da nauyin da yake kansa da kuma haƙƙunan mutane domin ya kiyayesu. Mutanen da Zikri na gaskiya, ba na nuni ba, ya ratsa zukatansu, to waɗannan mutane masu la'akari ne da abinda ya dace da wanda bai dace ba. Haka, Tuna Allah (swt) da TunaninSa sukan tsarkake zuciya ta kasance cikin yanayin alhairi a kodayaushe. 'Tunaninka Kamaninka' ashe babbar shaidar alhairi ce ga masu Zikri a lokacin da suke yinsa, kuma albarkarsa ta bi su ta kare su daga sharri, ko da a cikin barcinsu ne. Ba jarin da za ka tafi da shi har lahira irin Tuna Allah (swt) da TunaninSa.

Idan ka haɗa lokacin sallolinka, sai ka ga jimlarsu a ranar ba ta fi ta rabin awa ba. Amma in ka haɗa da yawan Zikirinka, sai ka sami awa uku ko fin haka a ranar wadda ka ba wa Allah (swt). Shi kuma Ya saka maka da milyoyin haka. Ba ma ci riba irin wanda 'Tunanin Allah' ya zama abokin zamansa.

V.
'DAGEWA ITA CE DUKIYATA'
****

Jarumi shi ne mai dagewa a kan manufa mai kyau, ko aƙida tabbatacciya, har sai ya cimma nasara.

Kamar yadda muka yi ta nanatawa a can baya, duk wanda ya gwada sau ɗaya ya kasa, ya watsar, to wannan mutum da kyar zai taɓa samun nasara a rayuwarsa. Nasara tana ga jarumai waɗanda suka san cewar ba lallai ne su sameta a gwajin farko ko ma na biyu ba, sai sun dage a kanta har illa masha Allahu, muddin dai sun yi imanin cewar wannan manufa tasu muhimmiya ce a garesu, kuma ta alhairi ce a lokatan yanzu da masu zuwa. Wannan tunani shi zai sa zuciya ta dake ta kuma himmatu wajen ababan sha'awarta. Ko addini ne, idan ba ka dage a kansa ba, sai ya tafi ya bar ka, kana ji kana gani ka rasa shi, domin ba ka dage ga yinsa ba. Ta wannan hanya, ba shakka, 'dagewa' babbar dukiya ce ga wanda ya maishe da ita al'adarsa.

Kana yi ana yi maka dariya, ana cewa 'kai wane da naci yake', wataran sai waɗannan mutanen sun zo neman alfarmarka. Duk abinda ba ka dage a kansa ba, toh wataran sai ka yi hasararsa, ko da kuwa



dama can naka ne. Kana ji kana gani za a ƙwace maka shi, kuma saboda kai rago ne, ba za ka iya dagewa ka maido shi gareka ba. Watau, masu dagewa ne kaɗai suke iya kare mutumcinsu da dukiyarsu da mulkinsu harma da addininsu. Ragwaye, ko 'yan aci-bulus' sune suke rasa waɗannan. Duk wanda bai dage a kan abubuwansa muhimmai ba, to dama can ba su da muhimmanci a gareshi. Ɗalibin da bai dage a kan karatu ba, to dama bai mayarda ilmin wani abu muhimmi ba, kuma mun san makomarsa. Ɗan-kasuwar da bai dage a kan sana'arsa ba, toh shi zai yi hasara. Sarkin da bai dage ya kare mutumcin sarautarsa da jama'arsa ba; ko shugaban da bai dage ya inganta shugabancinsa ba, duk su za su yi da-na-sani. A hankali za su rasa sarautar ko kuma martabar sarautar. Haƙiƙa mun ga misalai masu yawa.

VI.

'TAUSAYI SHI NE ABOKIN ZAMANA'

****

Mai tausayi shi ne wanda a kodayaushe yake cikin tunanin halayyar wasu; yake kuma yin iyakacin ƙoƙarinsa wajen taimakawa domin su sami wasila a rayuwarsu. Wannan tausayi bai tsaya kan mutane kaɗai ba, har da dukkannin halittu, watau dabbobi

da tsuntsaye da tsiranni, waɗanda aka sani. Amma dai, musammam ma bani-Adam.

Tausayi ya kasance abokin zamansa ne, domin a kodayaushe a cikin tunanin masu bukatar taimako yake, da yadda zai taimaka masu. Duk al'ummar da ba ta da irin waɗannan mutane masu tausayawa wasu, toh kuwa ba za a sami zaman lafiya a cikinta ba, balle kuma a zaci samuwar arziki da wadata, balle kuma adalci. Shugabannin da suka shagala wajen cuta da rashin gaskiya, shugabanni ne marasa tausayi, domin halayyar jama'arsu ba ta gabansu. Idan aka sami mai tausayi a unguwa, ko a gari, to ba shakka an sami jari babba, kuma ta nan ba abin alhairin da ba zai ɓullo ba.

Idan Allah (swt) Ya ajiye kayansa a wajen mai tausayi, to sai Ya yi ta ƙaro masa ajiyar, domin Ya san zai ji-ƙan wasu ne da wannan ajiya taSa. Amma marasa tausayi, ko badaɗe ko bajima, sai su ma sun zamanto ababan tausayi, kuma a hannun masu tausayin, ko ma a hannun waɗanda yakamata a tausayawa. Ka ga rimi ya juye da mujiya kenan, a cikin adalcin Allah (swt). Idan muka yi tunani mai zurfi, za mu ga irin waɗannan misalai da yawa. Kana zaune, sai ka ga mai tsoratarwa ya zama abin tausayi ta wasu halaye dabam. Ga tsohon Gwamna



yana neman taimako. Amma mutum wanda ya yi koyi da Manzon Allah, ya mai da tausayi abokin zamansa, toh wannan mutum ba zai yi lalacewar da zai zama abin tausayi ba shi kansa.

Mamugunta da azzalumai da maƙetata. Ɓarayi da macuta da maci amana; ba sa cikin rukunin masu tausayi, domin rashin tausayin ne ya haifar masu da waɗannan miyagun halaye. Amma duk mai tausayi ba zai kasance a cikinsu ba, domin tausayinsa ya lulluɓe zuciyarsa da la'akari da haƙƙunan jama'a. Shi banda ya kyautata ba abinda yake son yi saboda kirkin da tausayinsa ya haifar masa.

Da zarar mai tausayi ya shiga cikin wata masifa ko wahala, take a nan za ka ga caffa ta zo masa daga inda ba a zato ba a tsammani. Ba shakka, wannan caffa daga Allah (swt) take, kuma za ta iso daidai lokacinda za ta kasance mai amfani. Tausayin duk waɗanda suka cancanci a ji tausayinsu babban muƙami ne na Khalifanci, kuma babban jari ne ga wanda shi ma ya maida tausayi abokin zamansa. Ba abu mai daɗi a rayuwa irin ka tuna alhairin da tausayinka ya wanzar ga masu bukatar tausayin. Ka sha albarka, ka sha addu'a, ka kuma gamsu da kanka, sanin cewar ka kasance Khalifa na-gari., kuma mutumin kirki a idanun mutane. Lallai!

VII.
'ILMI SHI NE MAKAMINA'
****

Manzon Allah (saw) ya gama magana a nan. Da wannan, ba shakka, marigayi Mu'azu Hadejia ya yi la'akari yayin da yake waƙensa yana cewa:

'Gishiri in ba kai ba miya
Ilimi mai gyaran zamani.

Jama'armu ku jawo hankulanku
Ku lura da halin zamani.
Yadda kaska ke tsotson jini
Haka jahilci gun zamani.

Da tsiya da talauci duk suna
Gun da jahilci ya yi sansani.
Wa'azinmu ga mai karɓa duka
Masu son gyaran zamani'.

'Ilmi shi ne Makamina', inji Manzon Allah (saw). Wannan ba ƙaramar magana bace. Haka kuma za ka gani a hadisai yana cewa, *'gara dabba da jahili'.* Wannan ba ƙaramar la'anta bace; kuma lallai ta dace, domin jahili ko addininsa ma bai sani ba, balle ya san Allah (swt), balle ya tsara rayuwarsa a kan hanya madaidaiciya.



Kada mu ɗauka cewar karatun boko ne kaɗai ilmi, ko iya rubutu da karatu. Waɗannan sashi ne na ilmi masu amfani. Amma cikakken ilmi shi ne ilmin sanin Allah (swt) da yadda za ka tafiyarda rayuwarka cikin nasara, ka kuma zama shaida a kan kanka cewar kana cikin datattu. Ba makami irin ilmi, domin ba za a cika da yaƙi ba, ba za a ha'inceka ba, ba za a yi ba kai ba, ba kuma za ka ƙasƙanta a cikin jama'a ba, muddin ka ci ɗamara da shi, kuma kana amfanin da ya dace da shi.

Bayan ilmin addininka, ilmi mai amfani shi ne wanda ka koyawa kanka saboda halayyar rayuwarka. Ilmin da ya shafi sana'arka ko wacce iri ce, kuma kana mai alfaharin cewar a filin dagarta, sai an nemeka sannan za a san wasu abubuwa. Kada rashin ilmin boko ya kasance cikas a gareka, muddin dai ka gamsu kana da wani ilmin dabam na rayuwa wanda za ka iya amfani da shi wajen inganta sana'arka da rayuwarka. Ya rage naka ka san yadda za ka isarda kanka a cikin masu ilmi na fanninka ba tareda jin kunya ba. Da ilmi irin naka, da ilmi irin na wasu dabam, su ake haɗawa a gina al'umma a kowanne zamani. Idan ka shafa ka tarar lallai kai jahili ne, watau ba wani fanni wanda ka sani, ba kuma sana'a, to lallai ne ka tashi tsaye ka nemi ilmi da sana'a yadda za ka iya, domin ka sami

madafa a rayuwarka. Mai ilmin da ba ya amfani da shi, da mai sana'ar da ya wulakantata, to gara ma jahilin da ya fahimci jahilcinsa yake kuma yin wani abu domin ya canja wannan halayya tasa. Ilmin boko yana da nasa muhimmancin. Ko yi rubutu da karatu don ka ƙaru ta wasu hanyoyin.

'Gemu ba ya hana Karatu' ba ƙaramar matashiya bace a garemu domin mu watstsake mu tashi haiƙan ga neman ilmi yadda za mu iya. Yaƙi da jahilci shi ya tsamo wasu ƙasashe da al'ummu daga jujin talauci da takaici, ya aza su a sahun masu alfahari da kansu saboda nasarorin da suka samu ta hanyar sabon ilminsu da yawan masu shi a cikinsu.

Ba shakka, ilmi babban makami ne na cin nasara a duniya da kuma lahira. Manzon Allah (saw) ya haɗa kan nasihu a wannan manufa tasa.

VIII.
'HAKURI SHI NE MADOGARATA'
****

Ko Hausawa ma sukan ce, *'mahakurci mawadaci'* ko, *"Mai haƙuri shi ke dafa dutse ya sha romo".* Ba shakka daga azancin Manzon Allah suka samu wannan magana mai cike da nasiha. Duk wanda ya



haƙura ya bi abubuwa a hankali, ya kuma mayarda al'amuran fafutukarsa wajen Allah (swt), to kuwa ya kafa madogara mai ƙarfi, kuma wadata tana nan tafe a kan hanyarsa.

Rashin haƙuri, shi ke kawo ci-da-zuci, har kuma a shiga cikin hasarar da za ta tayarda hankali. Rashin haƙuri shi yake haifarda fushi, har kuma a watsar da manufa, ko kuma a tarwatsa tsari. Mara haƙuri shi yake ɓatawa da mutane nan da nan, har ya rasa abokai. Mara haƙurin jin cikakken bayani, shi yake aikata zalunci, abin kuma ya dawo kansa. Rashin haƙuri shi yake hana zuwa, har kuma a yi danasanin ba a je ba. Mai gajeren haƙuri mai gajerar zuciya. Mai gajerar zuciya, mai gajeren tunani. Mai gajeren tunani mai naƙasar nasara a rayuwarsa.

Ashe lallai ne, bayan mun yi shiri mun fara fafutukarmu ta neman wani abu, mu bi abinda haƙuri da dangana. Rashin haƙuri a kan abinda ake nema wajen wasu, shi yake ƙuresu har su hana. Ko Allah (swt) ka roƙa wani abu, tilas ka yi haƙuri sai sa'inda Ya ba ka, ko Ya musanya maka da abinda ya fi wannan alhairi a gareka, in alhairin ka ke nema. Amma idan ka kasa haƙuri da Allah (swt), to ƙarshenta ka watsar da addu'arka. Daga nan kuma sai ka watsar da addininka. Daga nan kuma ka rasa

madogara kowacce iri ce. Karanta surar “Asr”.

IX.
‘WADATAR ZUCI ITA CE GANIMATA’
****

Lallai kimiyyar rayuwa mai inganci da sauƙi tana daga ɗabi’un Manzon Allah, kuma don hakama ya zama abin koyi a garemu duka, ko an yarda da shi, ko ba a yarda da shi ba. Duk wanda ya yi nazarin rayuwar Muhammad (saw), kuma ya juyata da gaskiya ba tareda ƙyamar addini ba, to kuwa ba shi da zaɓi illa ya ji lallai yana son yin koyi da shi.

‘Ganima’, ita ce abar da ake kwasowa in an ci nasarar yaƙi, watau kamar dinare, azurfa, lu’u-lu’u da yaƙutu da su murjani da siliki, da bayi da sauran ababan adon duniya na mulki da ƙasaita. Duk waɗannan abubuwan alatu da jin-daɗi, su ya haɗa gaba ɗaya, ya ce, ‘wadatar zuci’ ta fi su.

Zuciya wadatacciya, ita ce wadda ta gamsu hani’an da ni’imomi waɗanda ta fassarawa kanta su a irin halayyar da ta sami kanta ciki. Watau dai, wata irin gamsuwa ce da irin yadda Allah (swt) Ya umarta halayyar mai ita, ta yadda mutum zai ringa ganin alhairi a cikin duk abinda ya sami kansa ciki.



Misali, idan aka yi wa mai wadatar zuci sharri aka ɗaure shi, sai zuciyarsa ta ringa faɗa masa cewar zaman kurkukun wata tsarewa ce daga Allah (swt) daga wasu miyagun abubuwa da za su iya faruwa ga mutum da yana waje. Daga irin wannan tunani na imani, sai mutum ya sami kwanciyar hankali, ya kuma mayarda al'amuransa wajen Allah (swt). Amma fa mutumin banza wanda illolin rayuwa su ne adajensa, ba zai taɓa zama mai wadatar zuci ba, domin yanayin zuciyarsa ba zai iya yin na'am da wata irin halayyar ba. Mai wadatar zuci shi ne yake iya fassara halayyarsa domin kimtsuwarsa, ya kuma sami biyan bukata daga irin tunaninsa.

Mai wadatar zuci ba ya shiga cikin halayyar talauci domin tuni zuciyarsa ta riga ta fassara wannan halayyar ta hanyoyi masu lumananta rayuwa. Mai wadatar zuci ba ya ganin ƙyashi, domin a lissafinsa '*wani hanin ga Allah baiwa ne'.* Duk abinda ka zo masa da shi na taƙama ko burga ko nishaɗi wanda ka ke zaton ya rasa, shi yadda ya fassarasu dabam ne. Idan kuma yana da waɗannan abubuwan, shi yadda yake auna amfaninsu gare shi dabam ne. Ba yadda za a yi ka husata mai wadatar zuci, ko ka turnuƙa masa wani baƙin ciki, ko wata damuwa, ta hanyar nuna masa wani abu da ya rasa. A gurinsa wannan abun da ka ke taƙama da shi ba muhimmi

bane. Shi ganinsu yake tamkar wasu wahalu ne da Allah Ya sauke masa su; kuma idan aka yi tunani mai zurfi, ba shakka, haka ɗin za a tarar. Ashe kuwa, ba ganima irin wadatar zuci, domin ita ce ganimar da take cire maka dulmiyewa cikin ganimun alatu waɗanda suke iya zamewa masifa in aka samesu, ko in aka rasa su, daidai da yadda zuciya ta yi son kanta gameda su.

Ba za a taɓa samun mai wadatar zuci da hassada ba, domin ba ya baƙin cikin abinda ka ke da shi, sai dai ya tayaka farin ciki idan ya fahimci abin yana amfanarka da wasu. Ba a samun macuta balle kuma azzalumai a cikin masu wadatar zuci, domin tuni tunaninsu ya kore kwaɗayin duk irin abubuwan da suke tunkuɗa ragwaye ga cuta ko zalunci. Ba a samun malalata ko maha'inta a cikin masu wadatar zuci, domin duk abubuwan da suke yi suna yi ne cikin amana ba tareda son ran da zai sa su waɗannan munanan ɗabi'u ba.

Haƙiƙa, wadatar zuci babbar ganima ce ga duk wanda ya kasance ya mallaketa. Amma ba ta da sauƙin mallaka, sai ga wanda ya yi tsaf ya kimtsa tunaninsa, ya kuma fahimci rayuwa sosai, ya kuma tsarawa kansa zaman lafiya da Mahaliccinsa da kuma kowa. Wannan tsari na zaman lafiya ba ya

tabbata sai kuma mutum ya yarda ya sadaukar da kansa ga rayuwa mai sauƙi ko menene matsayinsa, dukiyarsa, ilminsa ko mulkinsa, in yana da su, ko in ba shi da su. Watau dai ya yarda shi mutum ne sak wanda yake cikin zango zuwa ga rayuwa tabbatacciya, kuma ba zai yarda ya ɓata wannan rayuwa da zai tarar ba, a wannan zango nasa na ɗan lokaci mataƙaici. Watau dai, ya san komai na wannan duniya gajeren mafarki ne kawai. Irin waɗannan mutane su ne suke mallakar wannan wadata ta zuci, shigen wadda Manzon Allah yake da ita, kuma ta zame masu ganima abar alfahari.

X.
KWAZO SHI NE GWANINTATA
****

Wanda bai tashi tsaye da ƙwazo ba, to kuwa ba inda za shi, ba kuma inda zai dangana manufarsa.

Masu ƙwazo su ne abin sha'awa, domin su ne kuma masu sha'awar duk abinda suka sa kansu ciki ko suka kuɗiri niyyar yi. Da sun fara abu, ko da abinda wasu suka raina ne, to a cikin lokaci sai sun zama gwanaye abin sha'awa a cikin waɗannan abubuwa. Kwazonsu a kan waɗannan ayyuka ko manufofi nasu, shi ne abincin zuciyarsu, kuma ba

za su tsaya ba sai sun dangana inda suke son zuwa. Duk abinda suka sa kansu, da gaske za su yi shi ko menene abin. A garsu ba hasara irin barin abinda yakamata ka yi, ko kuma ka yi shi a sassauce, ko a lalace, ko a ha'ince ko a watse. Gwanitarsu ita ce su ga sun tashi tsaye sun yi komai nasu daidai yadda ƙarfinsu da ikonsu ya kai, ba kuma za su taɓa gamsuwa ba idan suka lura da kuskure a cikin abinda suka sa kansu yi. *"Duk abinda ya cancanci a yi shi, to lallai a yi shi da kyau."*

Duk abinda ka danƙa a hannun mai ƙwazo, toh sai ka gamsu, watakila ma fiye da yadda kai kanka za ka yi abin in kai mara ƙwazo ne. A kodayaushe, mai ƙwazo so yake ya faranta maka rai daga kyakkyawan aikinsa, muddin dai ya yarda zai yi wannan aikin. Farin-cikinsa shi ne ya ga ka ƙayatu ka gamsu daga abinda ka sa shi yi, ko yake yi don kansa. Idan mai ƙwazo ya fara abu, ba ya tsayawa sai ya gama, sai dai inda aka sami wani dalili mai ƙarfi wanda ya kawo cikas ga abin. A nan ma za ka tarar ba laifin mai ƙwazo bane.

Da jama'a sun fahimci kai mai ƙwazo ne a kan wasu abubuwa, toh ba shakka, kai za su dosa da waɗannan abubuwan. In kai mai ƙwazo ne a sana'arka, to ba shakka, sana'arka ta sami matakin

ɗaukaka, kai kuma tuni ka hau matakin nasara. Duk wanda ya maishe da ƙwazo gwanintarsa, toh ya gama fassara kansa a matsayin mutum wanda yake ba wa muhimman abubuwa muhimmancin da ya dace da su. Irin waɗannan mutane ba sa wasa da abubuwanda aka daɗa a hannayensu. Ba sa kuma wasa da rayuwarsu.

XI.
'IMANI SHI NE KARFINA'
****

Mun yi zancen imani a ƙarshen Babin na 8, a yadda ya danganci 'imani da Allah (swt)'. Mun kuma ga yadda Imani ya zama hujja ga Manzon Allah (saw). Ba shakka, imanin da Manzon Allah (saw) yake magana a kai, irin wannan imanin ne. Abinda kawai za mu duba a nan shi ne yadda ya zama 'ƙarfinsa'. Abinda duk ya zamto shi ne ƙarfinka, ba shakka kuma shi ne muhimmin makaminka da abinda ka ke taƙama da shi. Shi ne kuma ginshiƙinka da makarinka da mutumcinka da tsirarka.

Ba kadarar da mutum zai samu wadda ta fi imani mai ƙarfi. Da farko dai, mutane masu ƙarfin imani ne kaɗai suke iya jurewa da duk halayyar da suka sami kansu ciki, kuma su ne suke zama jarumai

waɗanda ba su taɓa fidda rai daga samun nasara ba, domin lallai sun yi imani cewar, *'nasara tana daga Allah (swt)'*, kuma Shi kaɗai ne mai ba da ita ko mai hanata. Masu ƙarfin imani ne kaɗai suke iya ƙyanƙyashe wadata a zuciyarsu, kuma wannan wadatar zucin ta ƙara ƙarfafa masu imaninsu. Waɗanda imani ya kasance ƙarfinsu, su ne kaɗai suke iya tabbatarda gaskiya ko ana ganinsu ko ba a ganinsu, domin suna sane da cewar Mahaliccinsu Yana ganinsu, kuma abinda Yake bukata kenan daga garesu, watau aikata gaskiyar. Suna sane da cewar Allah (swt) Shi ne Gaskiya, kuma idan suka yi ta, sun haɗe da Shi; idan suka bar ta, sun bar Shi. Karfin imaninsu ba zai bar su su taɓe ba, har abada domin shi ne madogararsu.

XII.
'GASKIYA ITA CE CETONA'
****

Ba gaskiyar da ta shige wannan magana. Kamar yadda muka ce yanzun nan a wancan shafin, Allah (swt) Shi ne Gaskiya. Haka Ya ce a cikin Al-Kur'ani mai tsarki. Yadda Yake ɗaya, haka take ɗaya. Wanda ya karɓeta ya karɓi Allah, wanda kuma ya ƙi ta, ya ƙi Allah. Wanda ya tsaya gareta ya tsaya ga Allah, wanda kuma ya nisanceta, lallai



ya nisanci Allah. Wanda ya aikatata, ya aikata abinda Allah Yake so, wanda kuma ya guji aikatata, toh ya guji aikata abinda Allah Yake so.

Ashe kuwa ba shakka, 'Gaskiya' ita ce kaɗai za ta ceci mutum, ƙarya kuma ita ce kaɗai za ta cuci mutum. Babu wata aba mai fitarda mutum a cikin mutane irin Gaskiya. Idan ka faɗeta sau ɗaya, sai ka yi ta faɗarta ba canjawa, domin ita kaɗai ce, ba sai ka tuna wani abu ba. Amma ƙarya ba ta maimaituwa a yadda aka faɗeta a baya, sai ta canja. Duk wanda aka sani da Gaskiya, toh ko ba a sonsa, tilas ne a girmama shi domin gaskiyarsa, kuma idan ya yi magana take an san ba wasa cikinta.

Da wannan siga ta gaskiya aka san Muhammad (saw). Saboda haka, da ya ce Allah (swt) Ya aiko shi da Gaskiya, ba a yi shakku ba, duk da wasu ba sa son abinda ya zo da shin. Dá an san shi da ƙarya dá ba wanda zai bi shi, dá addinin Islam a yadda ya zo da shi bai karɓu ba. Dá mun yi hasara babbar gaske. Amma, ba a san shi da ƙarya ba, don haka aka karɓi addinin a yadda ya zo da shi, ba gyara. Wa zai gyara abinda aka san ilahirinsa gaskiya ne?

Gaskiyarsa ita ce ta cece shi, kuma ita ce ta zama hujjarsa, kuma ita ce ta zama tushen addininsa,

kuma ita ce wadda, ba shakka, za ta ceci shi wajen Mahaliccinsa a ranar Hisabi. Da wannan Gaskiya dukkaninmu za mu sami ceto. A duniya: mu sami ceton mutumcinmu da ‘yancinmu. A lahira: Mu sami ceto daga kowacce irin azaba da za ta tsimayi maƙaryata a kan tafarkin da Mahaliccinsu Ya horesu. Duk wanda ya riƙi Gaskiya ya riƙi dahir.

XIII.
‘LADABI SHI NE CIKA TA MUTUM’
****

Mara ladabi ba zai iya biyayya ba. Mara biyayya kuma taɓaɓɓe ne shi a cikin mutane. Wannan gazawa ita ce babbar illa a tareda shi, domin shi ma ba zai sami biyayyar da yake bukata ba. Wanda kuwa ba za a bi ba, to kuwa bai cika mutum yadda ake so ba. Ya gaza matuƙa a martabarsa.

A matsayi irin na Manzon Allah, ladabinsa ga wasu, muhimmin shishshike ne na ladabi a gareshi. Idan ba a ladabta shi ba, ba za a saurare shi ba. Idan ba za a saurare shi ba, wa’azinsa ba zai jiwu ba. Idan ba a ji wa’azinsa ba, ba za a ji labarin addinin Islam yadda yakamata ba. Ya zamto masa wajibi ya kasance ma’abocin ladabi ga kowa domin ya sami biyayyar da shi ma yake bukata, a



kuma saurare shi cikin nutsuwa da ladabin, a kuma fahimci duk abinda yake cewa. Wannan ɗabi'a, muhimmya ce ga kowa, musammam ma masu bukatar su ma a mayar masu da ita. Ka haɗa ladabi da gaskiya, ka ga biyayya da soyayya yadda ba ka zato. Kana girmamawa, ana girmamaka. Kana magana, ana sauraronka, ana kuma aiki da ita.

Babbar shiriya a kan wannan dama can mun santa. Wanda bai girmama wani ba, ba za a girmama shi ba. Faƙat. Saboda haka duk mai son kimtsa mutumcinsa, to ya kimtsa na wasu. Raina mutane da yawan galatsi garesu, ballantana kuma ummul-aba'isinsu "girman kai", don kai mai muƙami ne, ko wani basarake, toh wataran sai sun mayar maka da martani duk lokacin da dama ta samu. Ko ma su zageka, ko su jefeka, duk da muƙamin naka.

Rashin ladabi da rashin biyayya suke haifar da rashin yakana da rashin sanin yakamata. Masu waɗannan halaye ba yadda za a yi su zama mutane cikakku, har sai sun sabunta tunaninsu sun gyara halayensu. Mun san wannan tun a Babin baya.

Rashin cika lokaci da alkawari, dangi ne na rashin ladabi da rashin sanin yakamata. Babu nasara a al'amuran masu waɗannan halaye.

XIV.
FAFUTUKA ITA CE ƊABI'ATA
****

Wannan ko shakku babu gameda Muhammad (saw), domin dá bai mayar da fafutuka ta zamto ɗabi'arsa ba, dá Islam bai bazu yadda ya bazu a lokacinsa ba. Dá kuma hakane, dá Sahabbansa ba su kasance masu fafutuka shigen tasa ba.

Kamar yadda muka yi ta nanatawa a gurare da yawa: Duk ƙarfin manufarka, idan ba ka cicciɓata da fafutuka ba, to ba za ka sami irin nasarar da ka ke nema a kanta ba. Mafi muhimmanci gameda fafutuka shi ne, ita ce kaɗai abinda za ka iya yi da kanka, domin mun san 'nasara' tana daga Allah (swt). Amma mai fafutukar ne kaɗai zai iya zaton nasara. Mara ita ya san dama can 'hasara' ce sakamakonsa. Mai fafutuka yakan sami wata irin 'nasara' tun daga gwajin farko, domin ta nan zai iya nazarin kura-kurensa ya kuma gyarasu don gaba. Mai fafutuka ne kaɗai zai iya himmatuwa a kan hanyar cin nasarar manufofinsa.

Rayuwar Manzon Allah gaba ɗayanta, a kan fafutuka ta ginu, kuma wannan ita ce ɗaya daga cikin darussan da ya bar mana waɗanda suka



cancanci yin koyi da su. Idan sai ya yi fafutuka a kan abinda Allah (swt) Shi kansa Ya aiko shi da yi, toh a kan menene kuma ba za a yi fafutuka ba. Wannan ba ƙaramin darasi bane ga masu tunani. Mai fafutuka ba ya lalaci, ba ya hasara, ba ya zama babu sana'a, ba ya zubarda mutumcinsa. Shi ne mutum wanda ya san idan ya yi fafutuka a kan wata manufa tasa ta alhairi, ko badaɗe ko bajima, Allah Zai kawo masa nasara ta wasu hanyoyi. Irin wannan tunani shi ne abincin zuciyar mutum mai ƙwazo a cikin fafutukarsa. Amma mutumin da ya fara fafutuka ya watsar, ko kuma sam ya ƙi farata, toh wannan mutum sam sam ba inda za shi a rayuwarsa. Duk wanda ya maishe da fafutuka ɗabi'arsa, toh kuwa yana tareda nasara. A duk halayyar rayuwarmu, mukan sami ƙalubalanta iri iri. Masu ƙwazo da son fafutuka ne kaɗai suke a shirye su fuskancesu.

XV.


IBADATA ITA CE FARIN-CIKINA


****

Wannan magana haka take a zahiri ga duk wanda ya yi tunaninta da kyau. Duk lokacin da ka ke cikin ibada a nutse yadda ake so, toh ba shakka, a waɗannan lokutan duk wani takaici ya kan fice

daga zuciyarka. Ko mutuwa aka yi maka, in ka zo Sallah, sai ka ji baƙin-cikinta ya lafa. In a kurkuku ka ke, ka shiga ibada, to a waɗannan lokutan sai ka ji wata iska ta 'yanci tana buso maka, musammam ma in zaluntarka aka yi aka jefaka cikin ƙuƙumin, saboda ba a sonka ko saboda ba a son ra'ayinka, ko don wani sharri da zalunci dabam.

Duk masu yawaita ibada take nan za su ga azancin wannan magana domin sun santa, ba baƙuwa bace. Ba maganin masifa da zulumin jidali irin ka tashi ka shiga ibada: nafiloli, zikri, salatin Annabi, Istigfari da sauran addu'o'i na girmama Allah (swt) da neman wanyewar masifu da jidalai. Waɗanda suka maishe da ibada ɗabi'arsu, ba shakka suna tareda farin-ciki a kodayause. Wannan yanayin alhairi na zuciyarsu shi ne kuma zai ƙarfafa masu imaninsu har sai sun kasance masu ɗokin ibada duk lokacin da suka sami dama. Mutanen da suka saba jin daɗin ibada, to duk lokacinda ba sa amfani da bakinsu, zikri suke yi. Irinsu ne ma a kowanne lokaci suke tsimin bakinsu daga zantukan banza, domin su sami sararin yabon Allah (swt) ko na salati ga ManzonSa, domin ta nan sukan sami wata lumana a zuciyarsu. Watau irinsu ne muke yi wa take: 'Zikrinsu Lumanarsu'. Allah (swt) Ya sa mu ma mu kasance haka. Amin.







Tunani da Hikima



'Kalma ɗaya tak, ta ishi mai tunani'

Yawancin waɗannan shawarwari, ko maganganun hikima, wasu mutane ne suka rubuta su domin su taimakawa masu tunani da nazari wajen kimtsa rayuwarsu. Na rubuta sunayensu a ƙasan maganganunsu. Waɗanda ba sunaye, yawancinsu nawa ne; wasu kaɗan daga cikinsu kuma, haka suke ba sunaye a inda na gansu.

Wasu sai ka ga kamar ƙalubalanta ne, wasu kuma ka yi mamakin dalilansu. Amma idan aka yi tunani aka kuma juya al'amuran rayuwa, ba shakka, za a tarar cewar yawancinsu hikima ce don a sami rayuwa mai amfani ta hanyar azancin kalmomin. Sai a duba da lura. Kowa zai sami waɗanda yake so da waɗanda za su iya zama jagoransa.

1.
Auna kanka daidai a kodayaushe,
A kan kowacce irin bukata taka,
A kowanne hali ka sami kanka ciki,
A cikin kowadanne irin mutane.

2.
Kada ka yanke shawara cikin fushi.

3.
Kada ka amsa magana cikin fushi,
Ko ka amsa takarda cikin fushi.
Jinjina sau uku a kalla,
Ka kuma yi tunani mai zurfi.

4.
Tabbatarwa kanka abinda ka ke nema
ya dace da kai,
Kafin ka yi amfani da lokacinka wajen neman.

5.
Kada ka kuskura ka ce sai ka yi abinda wani ya yi,
Ko ka jingina manufarka a kan ta wasu.
Zama mutumin kanka.



6.
Lallai ka yi tunanin abinda zai amfaneka,
Kuma ka yi shi da gaske da karfinka.

7.
Duk abinda ka ke yi, tambayi kanka:
Me na ke yi?
Daidai na ke yi?
Zai amfane ni?
Zai amfani wasu?
Yaushe zan gama?

8.
Duba damanka: Ka ga Littafai?
Duba hagunka: Ka ga shayi ko lemo?
Duba gabanka: Ka ga fulawa,
ko wani hoto mai kyau?
Duba bayanka: Ka ji shiru?
In duk amsar ba 'I' bace, gyara zamanka.

9.
Farkawa daga barci tana da kyau,
Amma motsa jiki muhimmi ne
(Karen Levine)

10.
'Abinda ya shige tarihi ne.
Abinda zai zo gaibu ne.
Amma 'yau' tawa ce kuma a cikinta nake'.
(Tsohuwar maganar hikima a Turai)

11.
'Gwanitar rubutu da zane
A saukin fahintarsu take'
(Walt Whitman: 1819-1892)

12.
Mafi kankanci mai ma'ana,
ya fi mafi girma na shirme'
(Carl Jung: 1875-1961)

13.
In ba za ka fadi alhairi ba,
Yi shiru da bakinka'
(Hadith)

14.
Ka iya gafartawa makiyanka.
Amma kada ka manta sunayensu'
(Pres. John F. Kennedy)



15.
'Ina son jin dadi mai sauki.
Shi ne maslahar mutane masu rikitarwa'.
(Oscar Wilde: 1854-1900)

16.
Kada ka jira sai bukatar abu ta tashi.
Neme shi ka ajiye don gaba, in da hali.

17.
Maza binciko baiwar da Allah Ya yi maka,
Ka riritata, ka yi amfani da ita.
In ba ka haka ba ka dankwafe rayuwarka
A cikin abinda bai dace da kai ba.

18.
'Lallai ka koyi kimtsuwa a cikin hayaniya,
Ka kuma san yadda za ka motsa a cikin shiru'.
(Indira Gandhi: 1917-1984)

19.
'Wanda ya kauda kwadayinsa,
Ya ci yakin rayuwa'
(Charles Dickens: 1812-1870)

20.
Mai wayo shi ne ya san abinda zai sadaukar.

21.
'Ku tafi ku nemi aikin yi.
Allah ba Ya ruwan dinare'
(Khalifah Umar bin Khattaf)

22.
'Da-nasani keya ce'
(Karin maganar Hausa)

23.
'Duk wanda ya kusanceNi da taka daya,
Zan kusantoshi da taka dari.
Duk wanda ya dosoNi a tafiye,
Zan dosheshi a guje.
Duk wanda ya fuskanceNi da zunubi fadin duniya,
Zan fuskanceshi da gafara mai fadin hakan'.
(Hadith Kudsi, daga Muslim, Ibn Maja da Ahmad)

24.
Ilmi kamar madubi yake in kana da shi,
In ka duba sosai sai ka ganka a ciki

25.
Kilo daya na aikatawa
Ya fi ton dari na hirar aikatawar'
(Friedrich Engels: 1820-1895)



26.
Cikakken Imani shi ne:
'Ka dogara da Allah,
Ka kuma san yadda za ka kare kanka'.
(Muhammad Ikbal: a Bal-i-Jibril. Sh.81)

27.
'Rayuwa dáma ce, ba tilas bace'
(Daga littafin shugabanci na Tao)

28.
'Sai Rayuwa ta sumbacemu da safe da rana.
Amma kuma ta yi wa ayyukanmu dariya
Da daddare da Asuba'
(Kalil Gibran)

29.
'Don na kasance 'ni',
Tilas ne na ɗau kasada da 'ni'.
Na gwada sababbin halaye
Na yadda zan kasance,
Har sai na tararda yadda nake sona'
(Hugh Prather)

30.
'Rayuwa kamar Mota take.
Za a iya amfani da Mota a je gurare masu nisa.
Amma sai wasu mutane su shige gabanta.
In ta kaɗesu sai su fara ƙorafi,
Suna zarginta da haddasa haɗarin'.
(Anthony de Mello)

31.
Hanya ɗaya da za ka rayu har abada ita ce:
Ka bar wani aiki na alhairi a bayanka

32.
'Fara komai da Sunan Allah'
33.
Wannan Juma'ar ka yi wani abu na alhairi
Wanda ka daɗe kana son yi.
Sannan kuma ka yi ƙoƙari
Ka maimaita shi sau ɗaya a wata'.
(Denis Waitley)

34.
'Imani da abu, dabam yake da aikata shi.
Wasu sai su ringa magana kamar Teku,
Amma rayuwarsu a daskare kamar ɓaɓarkiya.
Wasu suna saitin idanunsu ga ƙolin tsauni,
Amma zuciyoyinsu sun maƙale a kogon duwatsu'.
(Kalil Gibran)



35.
Idan za ka mutu sai ayi ta yi maka majigi,
Ana nuna maka dukiyar da za ka bari.
Kai kuma kana ta fushi ka yi hasararsu.
To amma, idan dukiyarka…
Zikirin Allah ce fa?'
(Imam Al-Ghazali)

36.
'Ban da 'Sauna', wa zai yi ban ruwa ana ruwa?'
'Wa ya ce maka 'Sauna' ne?
Ka san abinda ya kara a cikin ruwan?'

37.
A cikin wasu mutane kafin ku,
Sai wani mutum ya kasa hakuri da kurjinsa.
Ya dauko wuka ya yanke hannunsa.
Allah Ya ce,
'Wannan bawa Nawa ya yi gajen hakuri.
Ba Zan sa shi a AljannaTa ba'.
(Hadith daga Buhari da Muslim)

38.
Duk abinda ya zo daga zuci,
To kuwa zai faranta zuciyar.
(Don Sibet)

39.
Rashin girman-kai shi ne:
Ka yarda wani zi iya koya maka wani abu.
Girman-kai shi ne:
Ka rufe kofar zuciyarka.
(Arthur Deikman)

40.
Wuni-wunin me ka ke yi ne?
Tsoron me ka ke ji ne?
In za ka gwada ka gwada.
Rayuwa cike take da ababan gwadawa.
In ba ka gwada ba, ta yaya za ka iya?

41.
Kashi 80 cikin 100 na nasara
Zuwa gurin abin ne kawai.
(Woody Allen)

42.
Ba wai don abubuwa suna da wahala
Muke kasa yinsu ba.
A a. Kasa yin shi ne wahalarsu.
(Seneca)



43.
Sai an hada tunani da manufa
Sannan za a sami sakamoko mai amfani.
Yawancin mutane sukan bar tunaninsu
Ya zagwanye a cikin tekun rayuwa.
Kyaun mutum ya kudiri wani buri daidai shi,
Sannan ya yunkura cimmasa.
(James Allen)

44.
Ba kuskure irin ka yi kadan
Wai don kadan za ka iya yi.
Tashi ka yi abinda za ka iya.
(Sidney Smith)

45.
In za ka shiga, yi Sallama a kodayaushe.

46.
Ba za ka san daidaituwarka ba,
Sai ka girmama duk wadanda aka haliccesu
Kamar yadda aka halicceka.
(A Course in Miracles)

47.
Ma'anar Rayuwa ita ce ka rayun,
A sanka
A san manufarka
A san ra'ayinka
A san bambancinka da sauran
A san ka Rayu.

48.
Auna bambancin da yake tsakanin
Mutumin da ya ce, 'sau uku ina kasawa'
Da wanda ya ce, 'na kasa'.
(S. I. Hayakwa)

50.
'Ba Na murna da ɗan-Adam mai ɓata lokaci…'
(Hadith daga Buhari, Muslim, Abu-Dawud)

51.
In kana son ka san kanka,
Yi tunanin kanka.
(Socrates)

52.
Bishiyar Gamji daga 'iri' ta tsiro.
Hasumaya hawa goma daga tubali ta tashi.
Tafiyar mil dubu daga taƙar farko ta fara.
(Lao-Tsu)



3.
Lumanar zuci takan samu ne
Daga yawan Gafartawa.
(G.G. Jampolsky)

54.
Duk yawan littattafai masu tsarki da ka karanta,
Duk yawan zancenka gameda su,
Me ye amfaninsu in ba ka aiki da su?
(The Dhammapada)

55.
Duk abinda muke gani
Ko muka zata
Mafarki ne kawai a cikin mafarki.
(Edgar Allen Poe)

56.
Duk abinda za ka iya
Ko ka yi mafarkin za ka iya
Tashi ka yi.
(Goethe)

57.
Jiya, tunanin yau ce kawai.
Gobe kuma, mafarkin yau ce.
(Kalil Gibran: a littafin The Prophet)

58.
Da kyau a zo ƙarshen tafiya.
Amma ita kanta tafiyar ce muhimmiya.
(Ursula Le Guin)

59.
'Duk wanda ya tambaya zai karɓa.
Duk wanda ya nema zai samu.
Duk wanda ya ƙwanƙwasa za a a buɗe masa'.
(Annabi Isa, a Matthew– 7:7,8)

60.
Nasara balaguro ce
Ba danganawa ba.
Karshen tafiyar rabin nasarar ce.
(Gita Bellin)

61.
Yadda muke yau, tunaninmu ne na jiya.
Tunaninmu na yau shi ne yadda za mu zama gobe.
Rayuwarmu daga tunaninmu take.
(The Buddha)



62.
'Soyayyata tana ga wadanda suka so junansu
Saboda Ni.
Soyayyata tana ga wadanda suka ziyarci junansu
Saboda Ni.
Duk za su kasance a matsayin haske a cikin
inuwaTa'
A Ranar da ba inuwa sai Tawa'.
(Hadith Kudsi: daga Abu Hurayrah, Mushnad Ahmad)

63.
Abubuwa ba sa canjawa.
Mune muke canjawa.
(Henry David Thoreau)

64.
'Duk wanda bai ji bari ba
Zai ji woho'.
(Karin-Maganar Hausa)

65.
Wani abu gameda rayuwa,
In ka ce komai mai-kyau kake so, sai ka samu.

66.
Karya fure take yi,
Ba ta 'ya'ya.
(Karin-Maganar Hausa)

67.
Lokacin da wani ke ja da baya
Don yana jin bai isa ba,
Wani na can yana kura-kurensa
Har sai ya isa.
(Henry C. Link)

68.
Ba abu mai gamsarwa
Irin ka yi abinda aka ce ba za ka iya ba.
(Walter Bagehot)

69.
Idan ka ringa yin abinda kullum ka ke yi,
Za ka sami sakamakon da kullum ka ke samu.
(Anon)

70.
'Yadda kaska ke tsotson jini,
Haka Jahilci gun zamani'
(Mu'azu Hadejia)

71.
Idan ka kyautata sana'arka
Sai ita ma ta kyautata maka.



72.
Kada ka yi tagumi.
Tashi ka tunkari matsalarka.

73.
Yabo ya tabbata ga Allah
Shi kaɗai a MartabarSa da GirmanSa
Da kaɗaituwarSa da KasancewarSa
Da rashin ƙarshenSa,
Wanda ya tauye fukafukan ƙwaƙwalwa
Ta gaza daga hasken ɗaukakarSa.
Wanda Ya bude hanyar saninSa
Daga rashin saninSa.
Wanda Ya hana zaƙin harshe
Yabon kyaun kasancewarSa,
Sai dai ta hanyar da Shi kanSa Ya yabi kansa.
(Imam Al-Ghazali: farkon bayanin Asma'ul Husna)

74.
Mutane suna son su ji abinda za ka ce,
Amma suna son su ga abinda ka ke yi.
Kuma gani da ido ya kori ji.

75.
Gaskiya ita ce ma'aunin rayuwa

76.
Mutane ba su damu da abinda ka sani ba,
Sai sun san abinda ka damu da shi.

77.
Gaskiya daci gareta.
Amma sakamakonta zaki gare shi.

78.
Kiyaye tunaninka
Domin su ne za su zama kalmominka.
Kiyaye kalmominka
Domin su ne za su zama ayyukanka.
Kiyaye ayyukanka
Domin su ne za su zama dabi'unka
Kiyaye dabi'unka
Domin su ne za su zama halayenka
Kiyaye halayenka
Domin su ne za su zama hallayarka.
Kiyaye halayyarka
Domin ita ce makomarka.



79.
Gaskiya ƙarfi gareta.
Ba ta fashewa kamar ɓulɓuli don an taɓa ta.
Ka yaƙeta da safe,
Ka mangareta da rana,
Ka haureta da yamma,
Amma tana nan damdam da daddare.
Haka kuma za ta farka da safe.
(Oliver Wendell Holmes, Sr.)

80.
In za ka fadi, fadi gaskiya,
Komai ta ka ja maka ka biya.
(Sa'adu Zungur)

81.
Idan zuciyarka ta ce, 'I',
Amma tunaninka ya ce, 'A'a;
Kada ka yi.

82.
'Gaskiya ita ce Babin Farko
A littafin Hikima'
(Thomas Jefferson)

83.
'Ya Allah,
Ka tsare ni daga cin hakki da cin bashi'
(Hadith daga A'isha)

84.
'Ba wanda zai iya kaskantar da kai
Ba tareda yardarka ba'.
(Eleanor Roosevelt)

85.
Tuntuɓe zai iya hana faduwa
(Thomas Fuller)

86.
Masu hikima suna magana ne
Domin suna da abin cewa.
Banzaye suna magane
Domin wai sai sun ce wani abu.
(Plato)

87.
Kada ka yi kokarin canja duniya.
Canja tunaninka gameda duniyar.



88.
Ba dangantaka mai wahala
Irin taka da kanka,
Domin ba za ka iya yanketa ba.

89.
Duk abinda ka bayar,
Shi za a rubanya a dawo maka da shi.
Saboda haka, ka yi hankali da abinda za ka bayar.

90.
Akwai hanyoyi biyu na tunkarar wahalu:
Ko ka canja wahalun,
Ko ka canja kanka ka tunkari wahalun.
(Phyllis Bottome)

91.
Abu mai wahalar mu ke yi nan-da-nan.
Wanda ba zai yiwun ba
shi ya ke daukar dan lokaci.
(Taken sojojin Amerika)

92.
'Ko ka shige gaba a bi ka,
Ko ka bi,
Ko ka ba da hanya'.
(Rubutu a gaban Teburin Ted Turner mai CNN)

93.
Ba kasada irin rashin daukarta.

94.
In masifa ta doso
Yi mata waka.
(Karin-Maganar Larabawa)

95.
Duk sa'inda ka fadi,
Tsinto wani abu.
(Oswald Avery)

96.
In ba ka yi kokarin yin fiye da abinda ka iya ba,
Ba za ka taba ci gaba ba.
(Ronald E. Osborn)

97.
'Babbar nasararmu ba ita ce: 'ba za mu fadi ba',
Ita ce: 'duk sa'inda muka fadi za mu iya tashi'.
(Confucius)

98.
Duk tunaninka mai kyau,
Yana da amfaninsa ga rayuwarka.
(Grenville Kleiser)



99.
Ba makara ga abinda za ka iya zama.
(George Eliot)

100
Ba gaggawa ga abinda ba zaka zama ba
Haka, ba gaggawa ga abinda ba zaka samu ba.

101.
Gara ka rayu kwana daya a siffar Zaki,
Da shekara dari a siffar Jaki.
(Take a azurfar kwabon 'Lira' ta Italy)

102.
'Wadatar Zuci ita ce Ganimata'
(Hadith)

103.
Ba ka da abokin da ya fi ka.
Komai ya rage naka.

104.
Ce:
"La'ilaha Illallah, Muhammadan Rasulullah"
Sannan:
"Subhanallah, Walhamdu-Lillah,
Wala ilaha illallah, Allahu Akbar"
***





"Bismillahir Rahmanir Raheem"

****

***"Ga kowane** (mutum)*
Akwai Mala'iku a jere
A bayansa da gabansa
Suna gadinsa da umarnin Allah.
Hakika, Allah ba Zai canja
Halayyar mutane ba
Har sai sun canja kansu
(da zuciyoyinsu)"

Sadaqal-Lahul Azeem

****

Surat: Al-Ra'ad (13)
Aya ta 11

****

"Alhamdu Lillahi Rabbil-Alameen"

****



Mu rike addininmu da kyau, mu kuma nazarce shi a hankali da hikima. Ba shakka, duk abubuwanda muke bukata don cimma nasarar rayuwar duniya da lahira suna nan tattare a cikinsa. Amma fa sai mun bincika.

"Mai nema yana tareda samu"

c

